: DUNIYA TA

BISMILLAH

INA MATUKAR GODIYA GA ALLAH DA YA BANI RAI DA LAFIYA DA KUMA IKON RUBUTA SABON NOVEL DIN NAN DUNIYATA.

MAKARANTA NOVELS DINA DA BIBIYATA INA MUKU GAISUWA DA FATAN ALKHAIRI,ALLAH YASA WANNAN NOVEL YA FADAKAR YA KUMA NISHADANTAR,KAMAR YANDA MUKA FARA LAFIYA ALLAH YASA MU GAMA LAFIYA AMEEN.

KAMAR YANDA KUKA SANI NOVELS DINA NISHADI YAFI YAWA CIKI,INA KUMA GODIYA DA KUKE KARANTAWA HAR MUTUM YA SA KUDI YA SIYA WANNAN YAFI KOMAI DADI,INA GODIYA ALLAH YA BAR KAUNA.

1-5

FREE PAGE

LITTAFAN DANA RUBUTA

GASKIYA CE
MARAICIN RAHMA
MAAIKACIYAR GOMNATI
CIRANIN AMANA
DUK INDA TA FADI
KAMARSU CE DAYA
KASUWANCI NA
JIN DADI SABO
HADIN KAI
ME MAGANI
TUBABBIYA

NA KUDI DANA RUBUTA

RASHIN SA'A
TA GYARU
YAR KWANGILA
ADDUAR KAWA
GIDAN GWAURO/DAN NAZIA
DANGIN RABI
DUNIYA TA.......

GA MASU BUKATAR SHIGA GROUP DIN DUNIYATA DARI BIYU 200 NE

ACCOUNT NUMBER
0175487861 ASMAU GARBA MUHAMMAD, GTBANK.

MASU TURA KATIN MTN KO VTU GA NUMBER TA
08033933642

'YAN NIGER KU NEMI WANNAN NUMBER
+227 90 79 59 39

Official

By
AsmaBaffa

Page din farko naku ne Fans Dina duk wacce ke cikin groups Dina.

Zaune suke a wani katafaren Palo na Alfarma,Palo Wanda yaji furniture Dan gaske,duk Wanda ya Shiga wannan Palo bazai so Fitowa ba,wani uban kamshi da sanyi ne ke tashi,Family Guda su Shida rakacal sai ta bakwan Yar karamar yarinya tana Wasa a kasa,Kidan Bob merly ne ka tashi a wata katuwar plasma tv kamar ka dakko mutum,gaba Daya sunyi Shuru duk Basu cikin nishadi,Ahmad Dake narke cikin luntsumemeyar kujera shine yake kada Kai cikin maye da kwaya da gani kasan Kansa ba kalau ba,sai bin wakar yakeyi da bakinsa,gashi babu Wanda ya Isa yace ya kashe ko ya daina,baya Jin Maganar kowa,Mummy dattijuya itace ta nisa fuskarta dauke da damuwa Tace Haba Ahmad Kaine fa babban Danmu Amma ka duba yanda ka maida kanka Completely Useless har mun gaji da Dake Hanya tun daga Lagos muna zuwa Nan Kaduna wajenka akan magana Daya kaki ji,tunda hakane yau da Yamma zamu koma,Wani farinciki ne ya bayyana a kyakyawar  Fuskarsa,ya Mike tsaye yace wow Mama the Mama,Allah yau zaku tafi?yawwa Haka nake so sabo da na samu freedom,yau kwananku biyu Kun dameni dama,Shut up Daddy ya Furta banzan yaro marar tarbiyya,ai Kai dama Daddy nasan baka so na,Zama ya sake Yi Yana bin wakar Bob merly,sai Chanel din Suka cire wakar aka Sako tallan Wani body lotion.

Wata Uwar Tsawa Ahmad ya saki tare da nuna Tv da yatsa cikin mayensa na giya da kwaya ya kalli dalleliyar Budurwar da aka Nuno tana tallan Body lotion a tv yace Kai...dalla ku matsa can Kar ku kawo Mana Harkar Daudu anan,mu ba Daudu Muka zo gani ba Ana Harkar arziki zaku zo Mana da Mata Yan Daudu,ke dalla ja can, Dan uwarki a Nan Nigeria muna da man shafawar mu Habiba yawwa,Muna da Habiba Muna shafawa Muna Kara Baki wuluk abin mu yafi Mana,Dariya ya Bawa duka Yan palon har Daddy ya kalle shi yace Ahmad Kai da kake fari Kal jinin Larabawa Kuma a gidan uban wa kake shafa wannan Man,sannan ce maka aka Yi Habiba karamin company ne? Mummy Tace Allah ya shirya min kai,Baki ya turo tare da gyara Ass down dinsa da yayi da wani Creazy jean.

Wata Yar kyakyawar jar mota ce Honda tayi parking a bakin wani Restaurant,Yar kyakyawar Budurwar ta fito Hannunta dauke da Handkerchief tana goge zufa, Hannayenta ta Shiga tafawa tana Waka Sannu da Zuwa.....Sannu....da zuwa kekashashe na,Oyoyo Dan Kedararre na.....Oyoyo Karmashashe na,Barka da dawowa Dan tsomalalle na,My Karmash I miss you,Wani saurayi ne matashi mugun siriri wuyansa kamar murkin laima,Kugunsa Kamar zai tsinke,Baki ne wuluk Kamar Iska zata dauke shi Haka ya fito daga jar motarsa Yana wani basarwa a dole babban yaro,Bakinsa ya Bude da Niyyar magana Yan hakoransa manya na gaba Guda hudu Suka yo waje,Yana kallon Budurwar yace naga Alama Baki da tarbiyya,Kamar Ni saurayinki Ina sonki kina so na Amma kina ci min Fuska,glass dinsa ya zare a Fuskarsa ya kalle ta sama da kasa yace Yar talakawa Dake matsiyaciya ki kalle Ni kina wani ce min Oyoyo Karmashashenki? Baki da Manner? An fada Miki badan so ba Zan iya tsayawa da Yar

matsiyata irinki? Ki kalle Ni nafi karfinki ta ko Ina,Yar budurwar kyakyawar gaske fara Tace Kayi Hakuri Wasa nake maka wallahi badan naci fuskarka na fada ba,Tsawa ya daka Mata yace dalla ja can dama iyayenki Basu Miki tarbiyya ba,Baki da hankali dai,Ran Budurwar ya baci tace kaga Malam na maka tauna na maka hadiya baka gani ba,to naji bani da tarbiyyar sai kace Iyayenka suzo su Yi min,daga na maka Wasa Kai baka San wasan masoya ba,wannan ne wasan a gidan uban wa ya Zama Wasa? Nan take Budurwar ta bashi amsa a gidan Ubanka Kamalu,Baki Bude ya kalle ta yace Aamna a gidan wa kika ce? Wacce aka Kira da Aamna ta sake cewa a gidan Ubanka nace Kamalu,Kamalu ransa ya dugunzuma yace it's over between me and you,bani ba ke,Aamna Tace ae naji Nima bani ba Kai tsotsatsen banza,me zanci da Kai dama idan anyi auren ma Banda kashinka ya dinga suka na me zanyi,Dana kwanta a jikinka gwara na hau katifar fasasun kwalaba,Kuma da na aureka ka min kiss da bakinka me hakora Kamar kacar Keke gwara na tsotsi Kusa me tsatsa,Yace irin na Ubanki ne ai hakoran,naji ta furta tare da koma cikin Restaurant taci gaba da aikinta.

Wajen masu girkin taje ta faki idonsu ta saci yankan nama Uku ta watsa a Jakarta ta fito ta baya can ta cinye Naman sannan ta dawo ciki ta Iske Fried rice an Gama an kaiwa wani yaci ya bar Rabi kadan ma ya ci,Aamna da sauri tazo Wajensa Tace Alhaji ka Gama Zan gyara wajen 2pm yanzu resturant zai cika,kafin yayi magana ta sunkuce abincin ta dauke Masa lemon da ko budewa baiyi ba ta Sha kwana tayi ciki,Alhaji ya saki Baki Yana cewa ke ke ke ban Gama ba Amma Ina Aamna tuni Taki ma kula shi,tana zuwa Tace Alhaji ya koshi ta zauna ta lashe abincin ta Balle lemon ta shanye sannan ta fito fes da ita da mamakinta sai taga Alhajin Bai tafi ba,da sauri ta koma Wajensa Tace Alhaji wani abincin Za'a kawo maka ne? Alhaji ya kalleta yace ke Amma wacce iri ce bance na koshi ba kin dauke abinci lemon ma Dan wulakanci ko Bude shi banyi ba kin dauke Ina ta kiranka bakya ji? Aamna Tace eyya Allah sarki kayi Hakuri matsalar kunne gareni banji ba Kuma gashi na zuba komai cikin shara bare na dawo maka da shi,Harara ya balla Mata tare da zube wani kudin yace kawo min wani abincin,da murna ta dauka dama Bata koshi ba,taje ta hadowa Alhaji duk abinda ya bukata,wata white rice with salat ga kwai da kaza,ga lemo,Aamna tunda taga Haka take ta faman zaga wajen da mopper a Hannunta Wai a dole gyara takeyi,tana ta faman goge goge a saitin Alhaji,Alhaji yace ke kin dameni da goge goge ga customers can sunzo kije Mana Haba wannan wacce irin Maaikaciya aka dauka Haka idan bakya so sai na daina zuwa cin abinci a wajenku aikin banza,Aamna tayi murmushi tare da gyara pcap dinta Tace afwan Alhaji ta juya ta tafi Amma sai ta labe a bayan wani lungu daga ciki tana ta kallon Alhaji tana so yayi ya Gama ta samu rabonta,Siyama ce kawarta taje ta sallami wasu customers din Aamna tana labe tana zalama wajen Alhaji,Siyama tayi Dariya tare da kallon Aamna tana labe labe Tace Allah ya shirye ki,Alhaji kadan yaci ya bar komai ya tafi kafin ya Gama fita tuni Aamna ta kwashe komai tayi ciki,Nan ma ta zauna ta cinye ta koshi sannan Tace saura na dare kafin na tafi gida,dole na dinga kiba Ina yin kyau,Aiki a restaurant ai Dadi gare shi ko ba komai Zan cika tumbi na.

Dattijo ne fari me gemu sosai Wanda shi kanshi gemun ka kalla kasan Dattijon ya tsufa domin yayi fari,da gudu gudu sauri sauri ya shigo gidansa inda yake wani mugun Rubabben gida,Gida ne na Haya Kuma gidan Talauci,da gani ba sai an fada maka ba Dattijon Talauci ya

Gama da shi,cikin Gida ya Fado Yana masifa tare da furta me zangani Aishatu?me zangani yau,wacce ya Kira da Aishatu ta kalle shi shekeke tare da balla Masa Harara Tace mene? Gashi can kina karar min da kudi,kina min asarar Duniya da Almubanzanranta,yanzu ki duba sabo da Allah tunda na taho Ina kallon kwalabati kumfar Omo tana ta bin ruwa tana ficewa Ful...ful,Yanzu a zamanin Nan kumfa ka gani a kwata kasan kudinka ake kashewa,kina ta kashe min kudi kina abinda kika ga dama,Ga jarabar karar da Ashana kiyi ta kyastata sai ta Kare,Takaici na yanda kike wanki ko wanke wanke sai asarar Omon bala'i,to wallahi da sake baza ta yuwu ba,kullum Ina fama a hanyar sakateriya wajen Dan aiki na Wanda masinja ne ni nayi retired Ina nemowa Ana wulakantawa bazai yuwu ba,Daga yau ko mangyada ne za a zuba a abinci to kowa cokali Daya Daya babu kari aikin banza,Wata buta yasa kafa tare da yin fatali da ita Yana zare Ido yace Ina Aamna sakarai da Sweety Zuhra?Aishatu banza tayi Masa ta ci gaba da aikinta,yace Aamna har yau ba labarin Mijin Aure?

Aishatu tayi Shuru,Dattijon yace na gaji da yahudanci wallahi da nasan Haka ne Aamna ko secondary baza tayi ba,Dan fa Kawai Ina tunawa Amana ce a wajen mu, Nima ban San ya akayi basirata ta toshe na biya Mata har tayi wani HND sabo da asara,ai karatun mace Bai da amfani,amfanin mace aure da girki tayi ta zazzago Haihuwa,yarinya ta Zama bayahudiya abinda taga Dama shi takeyi,Nima jarabata ce tasa Rana tsaka Ina Kauye tare daku cikin sutura na dawo damu Birni na Kama haya,da Muna Kauye da tuni hankalinmu kwance,da duk wannan karyar Bamu shige ta ba,Aishatu Tace ai sai Dana fada maka kaki ji Aamna tana secondary a Kauye Ss3 ka kwaso mu Muka dawo birni gashi yanzu ta waye Taki aure muna ta ciyar da ita a banza ,wallahi baza ta Sabu ba,gidana ya koma na yahudu bazai yuwu ba,ai Birni na dawo ne Kawai Dan na samu sana'a me kyau to gashi hakan Bata samu ba,Dan pension Nawa ma baya Isa Nawa yake Ina abin,kullum sai talauci ne ke karuwa,birni kwai masifa Ni tunda nazo banga wayewar ba,ban wani waye ba,Aishatu Tace yo shekarar mu Nawa a Birnin kwata kwata shekara hudu fa rak Ina wani wayewa Aamna da Zuhra ne Kawai Suka Dan waye Dake su Yara ne,Dattijon yace ke tafi can Aamna Ina ta waye ai gwara Zuhra,Amma Aamna kina gani magana ma Bata iya ba ta Kauye takeyi duk abinda yazo bakinta dankarawa mutum takeyi Dan tayi makaranta ne ma take Dan canjawa,ni dai na fada Miki a kiyaye asarar Omo yawwa ya furta tare da ficewa falau falau da rigarsa doguwa ta wani tsohon yadi dinkin wani falkeke komai ta Masa yawa

Kuka Aamna ta saki Wiwi tana Hawaye tare da nuna Budurwar da Hannu tana masifa tare da Furta In Allah yayarda Shedan sai ya sumbace ki,Shedan sai yayi kissing dinki,muguwa,Azzaluma, maciya Amana,Baza kiga dai dai a rayuwarki ba Saratu,Saratu anyi asarar Duniya,An Sarai asarar duniya,Shegiya wacce Shedan yayi Mata fitsari a Kai, Wacce ake Kira da Saratu murmushi ta saki tare da karkada key din motarta Tace nafi karfinki Kina talaka kucaka me Deeni zaiyi dake duk kudinsu,ke wawiya ce Baki da hankali da har kina me siyar da Abinci a Restaurant kike tunanin Dangidan Dan Majalisar jaha Deeni zai so ki,ai ko kansila Aamna bazai tayaki ba,ganinki kyakyawa Fara Wai zai sa samari su soki? Kinyi kuskure Aamna,ai yanzu samari sai masu kudi suke Nema gidan da Suka gaji arziki,ai yanzu sai kana da kudi ake rayuwa da kai,ke Dan Dakikiya ce tunaninki kyau Yana sawa a so mutum? Dan kina da kyau har Shishigi kike Yi to ki sani samari sai dai su yaudare ki Amma yanzu duk munin

masu kudi Haka ake aure su,Talaka ma Bai son Auren talaka bare irin su Deeni masu kudi,Ina Baki shawara ki fita Harkar Deeni ba ajinki bane.

Aamna tana tsaye sanye da Jean skert Blue da rigarta T-shirt fara tas me Rubutu Red a Gaban Rigar An saka A&G Food Joint,ta Sanya pcap Red takalminta ma Red,ba karya Aamna karshe ce a kyau,haskenta me kyau ba fari Kal Kal ba Amma fara Ce dai ba Wanda ya Isa yace wankan tarwada ce,dole dai farar ce,Gashinta har gadon baya Baki wuluk,Ga Zararan gashin Ido tare da kwantaccen Gashinta dake goshinta,Girarta wuluk me yawa,Hancinta me kyau bai cika tsayi ba,Fuskarta ba doguwa ba baza Kuma ace Round face ba,Dan Bakinta gwanin Sha'awa Karami with pink lips,Gata doguwa Amma ba can ba,ga Uban Hips kamar ita tayi kanta komai nata me kyau,hakoranta kanana farare tas,Idonta dara dara, Mashaallah,Aamna baza ta wuce 24years ba,Haka kanwarta ma Zuhra kyakyawa ce Amma ita chocolate ce kamarsu Daya da Baba.

Murmushin takaici Aamna tayi Tace ai gaki Nan da Muni yayi Miki yawa Deeni zai kwasa ki cinye Deeni please ta juya tare da komawa Kan bakin aikinta wurin masu siyen abinci,ita kuwa Saratu Tsaki ta ja tare da Bude dalelleliyar motarta baka ta Shiga sannan ta fisgeta a Tamanin.

Sai 11pm ta tashi a Aiki ta saka After dress dinta me Dan kyau tare da rataya handbag dinta tayiwa abokan aikinta Sallama ta wuce gida,Napep ta Shiga zuwa gida,can cikin wata Unguwa ta masu rangwamen gata aka sauke ta a Kofar gidansu na Bulon siminti Amma ka rantse kango ne baiyi Kalar gida bane,da Sallama ta Shiga da kyar aka samu aka amsa mata,Mama Wato Aishatu ta Iske tana Daura Net a dakin babansu Tace Mama na dawo,Tsaki dattijuwar ta ja Tace to sai me,idan da sabo ta Riga da ta Saba,Baba ta kalla Yana daki Tace Sannu Baba,da kyar ya amsa,Kai Kawai ta girgiza ta wuce kitchen Nan ta Iske abincinta an zuba Mata Amma an barshi a Bude baza a iya rufe Mata ba,ta Saba Kawai ta dauka tare da Fitowa sai ga Daya matar gidan tunda dama gidan Haya ne,mutum Uku ne a ciki ko wacce mata da dakinta biyu da kitchen Amma toilet Guda Daya ce du,Gaisawa Suka Yi Tace Maman Zeenat ya gida,Tace Ify Alhmdllh da fara'a, dakinsu ta wuce ta Iske kanwarta Zuhra tana kwance a saman katifarsu tana chatting da saurayinta Wanda zata aura Nan da wata daya.

Murmushi Aamna tayi Tace Zuhra Ana Shan love, Murmushi Zuhra tayi tana juyi Tace Aunty Aamna an barki a baya wallahi,Soyayya tayi a rayuwa,Adam ne ke kashe Ni da zafafan kalamansa masu sweet,Dariya Aamna tayi Tace na tayaki murna kanwata ke kin samu Miji Ni kuwa kin barni nice Kuma yayarki gashi Mama da Baba sun tsaneni akan ban kawo musu Wanda Zan Aura ba,Hawaye ne ya silalowa Aamna Tace why me naaa?why Me Zuhra? What have I done wrong? Tausayin Yayarta ya Kama Zuhra Tace kiyi hakuri Aunty Inshaallah kema Zaki samu miji very soon,Kuma Inshaallah su Mama zasu hakura su daina fushi da ke.

Kai Aamna ta girgiza Tace Zuhra Ni bazan iya auren Wanda bana so ba,da Zan Iya Dana fitar da ko ma waye Dan na farantawa Iyayena Rai Amma idan nayi bazan iya yiwa Wanda bana so Biyayya ba,Illar Hausawa kenan Allah Bai kawo maka Miji ba a takura maka karshe har sai ka auri Wanda baka so,baza ka Dade ba za a sakeka,ko Kuma kullum ku Kare a fada da sasanci,bana fata inyi aure na fito Zuhra,Nafi so ko wa Zan Aura ace Ina sonsa sosai sabo da shine kadai Zan iya Masa Biyayya,kin San halina Ina da taurin Kai,Kuma Ni ba a iya tankwara

ni,So shi kadai ne zai sa nayi Biyayya,Kin San idan bana son mutum wallahi zanci ubansa ne,Amma su Mama sun kasa fahimtata,Zuhra Tace ai ke matsalarki kenan Aunty akwai saurin fushi ga rashin barin ko ta kwana,aure Kuma sai Hakuri,Hakuri na Kawai na auri Wanda nake so ko jibga ta zai nayi kullum Zan zauna Kuma bazan ji Haushin kowa ba.

Mama ce ta fado dakin Tace Ina Jin duk abinda kuke cewa,ke Zuhra ki daina saurarar marar hankali,ai yanzu ba auren kauna akeyi ba dubawa akeyi aikin mutum ake dubawa me yake samu,zai Iya rike ki, ci da Sha shi ake kallo ayi aure,ke soyayya Zaki aura Zaki ci ubanki kuwa a hannun maza,kika sake sai Namiji ya sa Miki ciwon zuciya,Aamna tace kinji ko Mama bakwa duba Iliminsa da Addininsa Kawai kudi kuke dubawa ayi aure,Baba Yana ji ya tsomo Baki daga dakinsa yace Ni ki tambaya Sanda na auri Uwarku ban taba ganinta ba Haka itama Bata taba ganina ba Kuma gashi Muna tare har mun haife ku,wallahi Aamna kika sake Watarana sai na koreki daga gidana,badan ma kece kike rage min nauyin gida ba da tuni nayi Miki auren Sadaka Kuma wallah Matukar Naga dama auren Sadaka Zan bada ke.

To Baba kuyi Addua Allah ya kawo min na gari,Kuma da kuke cewa Baku ga juna ba aka muku aure ai ku a zamanin da ne Kuma asiri akeyi Ana kafe matar ta zauna dole,Salati Baba ya saki yace Ni Zaki hada da shirka Ina Dan Izala? Shuru Aamna tayi,Mama Tace mayaudariyar banza,kin Yaudari Affan kin Kore shi kince kin Kama shi da cin Amanarki Yana kula Mata,Hassan Kuma kince Dan karya ne,Deeni ma yaro me kudi yanzu kince ya yaudareki ya koma wajen Saratu kawarki Yar gidan Alhaji Sani Likita, yanzu ga Kamalu kin ci Masa mutunci ya gudu shima,Jollof din shinkafata wacce ta rigada tayi sanyi ta bushe ita Aamna ke ci su Mama suna ta mata fada har ta Gama,ta cire kayan jikinta gaba Daya ta wanke tare da shanya su a daren,Wanka tayi da ruwan zafi tare da Shirin bacci ta kwanta ta bar Zuhra tana chatting da masoyinta .

Dalleliyar mota ce ta gaske wacce a kalla ta miliyoyi ce,ta danno cikin wani katafaren gida na Gagara,Gida ne Wanda ya amsa sunansa,Babu abinda babu a ciki,motoci ne zasu Kai takwas a gidan Wanda suka gaji da haduwa ga tsada,farare Guda hudu a jere bangare daban Haka ga wasu kaloli daban,Machine ne Guda Uku kala daban daban masu tsada harda Keke na masu kudi su biyu,Gidan Ya gaji da tsaruwa ga flowers ko ina,idan ka Shiga gidan baza ka so Fitowa ba,Kalar gate din ma na daban ne,ba ko Ina ake ganin Irinsa ba a kasar Haka furniture sai dai ko gidajen Gomnoni, Wani Matashi ne ya Bude motar baka Daya shigo da ita,Fitowa yayi da kyar Wow wani Fari ne tas kamar Balarabe har wani ja yake kamar ka taba shi jini ya fito,dogo ne Amma ba can ba,gashi shi ba Mai kiba ba baza ace Kuma siriri ba,Fuskarsa me dauke da hancinsa zarkadede ba irin me tsayi da yawa ba,Sumar Kansa baka wuluk dauke da wani mayen Aski irin na Yan duniya,an kwashe gefe da gefe an yanki wani waje siriri an Kona shi tare da maida shi Fari tas,Sajensa me kyau luf luf me dauke da Dan gemunsa cas,idanunsa Dara Dara farare tas suna wani lumshewa,kowa ya kalli wannan matashi yasan ya Gama gajiya da haduwa,Naira da Hutu sun zauna a jikinsa,Jikinsa na maza Wanda suka amsa sunansu maza,sanye yake cikin wani Crazy Jean me tsada gaba Daya wandon a farfashe yake ruwan toka,da wata T-shirt me Rabinta Fari Rabi Kuma Blue,Takalminsa da agogonsa masu tsada,Yatsansa sanye da zoben Azurfa,da kyar yake takawa ga takama ga aji Amma Kuma Yana tangadi da Alama yayi shaye shaye ya gaji,Yana dafa bango Yana tangadi AHMAD kenan

a Haka har ya Isa katafaren palonsa tare da fadawa saman kujera ko Takalminsa Bai cire ba ya kwanta Haka Yana sambatun maye shi kadai har bacci ya kwashe shi.

Tunda ya fara bacci gab da Magriba Bai tashi ba sai da gari ya waye sannan Rana da hasken gari yasa ya Bude lumsassun idanuwansa a hankali,Kara ya saki kadan Jin jikinsa a gajiye,da kyar ya iya tashi a hankali ya haura samansa Direct toilet ya shige ya Dade Yana wanka dake akwai tsafta,Bayan ya fito daure da Towel jikin mudubinsa ya nufa turaruka ne da mayuka na maza masu tsadar gaske,Lotion me kamshi ya shafa tare da fesa Body Spray a jikinsa sannan ya dakko sabuwar jallabiya me tsadar gaske fara sal Amma ta Dan tsangale Masa baya sa wacce zata Kai Masa har kafa sabo da Damunsa takeyi,Turaruka ya fesa sannan ya dauki wayarsa me tsada Yana latsawa,a hankali cikin tafiyarsa ta Isa da takama ya sakko kasa ya Bude kofa ya fito sanye da wani flat shoe fari sal shima Yana tafiya a hankali ya bi ta wani corido gaskiya gidan Nan ya Gama haduwa tiles din kasan gidan na tsakar gida fari da Baki ne ko Ina sheki yake Yi da walwali,Me Gadinsa ya hango Yana karasa gyara gidan Yana kida da bakinsa Yana rawa Yana aikinsa,Ya Dade a tsaye Yana kallonsa,Abin Dariya ya bashi mutum shi kadai Yana kida Yana Waka Kuma Yana rawa duk shi Daya, murmushi ya saki kadan tare da girgiza Kansa ya juya ya koma inda ya fito.

Har yayi nisa sai ya dawo ya Kira me Gadi Musa,da sauri Musa ya dago yace Oga tare da takowa da gudu yazo gabansa yace Ina Peter banga ya gyara ciki ba Sannan ba Abinci,Oga ai Peter ya tafi kasuwa yace abincinka Yana kitchen yace sauri yake yi,Ni gaskiya Oga Ina tunanin yafi a dakko mace yar Aiki wacce zata na maka girki da gyara maka ciki tunda Ni Ina kula da Campun,Ogan yace ba Campun ake cewa ba Musa Compound,Kuma Ni bana bukatar mace yar aiki,Ni bana son mace ta rabe ni,duk abinda zai sa na hadu da mace bana kauna,Musa ya zaro Ido yace Oga Mata sune Jin dadin duniya duk wata nutsuwa da Namiji zai samu tana jikin mace,Baki Ogan ya tabe yace Allah ko? A wajen wawaye ba,gwara naci abincin Gardi akan naci na mace,Karka sake furta kalmar Nan mace a gaba na,idan ba Haka ba Kora ce tukucinka,Musa yace an Gama,Kayi Hakuri Ranka ya Dade Namiji gwara nace Namiji,macen banza Banda Mum dinka Oga,Baki ya tabe ya juya da Gadara ya wuce,Abincin Peter ya Bude yaga Bai Masa ba,da Kansa ya shirya Girkinsa da lafiyayyen tea dinsa ya karya sannan ya dauki key din mota yayi waje,Yau da wata mota Ruwan toka ya fita kirar Benz.

Washe gari Aamna wanka tayi tare da Shiryawa tsaf cikin kayanta Riga da wando sunsha wanki da guga,After Dress ta Dora a Kai tare da yafa Mayafi,ba Wanda ya kalle ta a cikin Iyayenta Balle Tace Za'a Bata wani abinci dama yanzu basa kulata,ko ta gaishe su basa amsawa,Sallama ta musu ta tafi,Mama Tace yarinyar banza ace tasan Burin mu Bai wuce mu Aurar da su ba Amma Taki fitar da Miji abin kunya kanwa zata Riga Yaya aure duk ta tsufa a gida Allah wadaran Dan Riko,shekara ashirin da Hudu ai ba Wasa bane,mu duk da a cikin birni muke muna Nan da akidar mu ta Iyaye da kakanni na auren wuri Amma kash Yaran namu musamman Aamna ta Gama watsa Mana kasa a Ido,marikinta Bai da Buri sai na Aurar da su,ai mutuncin ya mace gidan Miji Amma ba komai Aamna wahala da azaba ma Sai ta sa kin fito Mana da Miji,kin daina Jin dadin gidan Nan kwata kwata,yanzu Zan canja Taku wajen gana Miki azaba duk da Kamar mahaifiyarki ce Ni dole wahala tasa ki fitar da Miji,Zuhra kuwa Shiryawa

tayi tuni tayi Kari me kyau Ana ta nuna Mata gata da kauna ta tafi makarantar Boko Wato Secondary school sabo da sun kusa yin candy.

Ahmad Bai tsaya ko Ina ba sai gidan Mashkoor inda Suka Fi Zama suna shaye shaye a gidan,can ya Iske abokansu su Biyar Mashkoor, Abdul Tawaga,Jibril Jibson,Bashir Bash, Mubarak Brown sai shi Oga Mai gayya me Aiki Ahmad King,Yana zuwa ya Iske su a zaune a Garden suna zaune a kujeru ga karamin Table an zube kayan maye na shaye shaye kwayoyi da giya iri iri ga Sigari taba da Wiwi,Kirari suke Masa Suna The King...Our King,shi Kuma Yana uban Gadara Abdul Tawaga ya Daga Masa kujerarsa ta tsakiya Kuma kujerarsa ta mulki ya zauna tare da Balle kwalabar Giya ya Shiga tiltila Kamar ya samu ruwa,Bash ya kunna Wiwi Yana zuka ga wasu kwayoyi Daya hada a cikin wani ruwan giya Yana korawa Yana tiltilo hayaki ta Hanci ta Baki cikin kwarewa,Tawaga Yana Aswaki Yana cijewa Yana karkace Baki yace Our King....Sweet Boy,The Handsome King,Fresh Boy, shi kuwa King ya kalli Kansa yace Na me....Na me My Guy,Look at my skin color....
Mubaraq Brown yace Handsome King,Mashkoor Yana wani tangadi a zaune yace Our King ka huta baka hura hayaki sai ruwa Kawai kake bulbula sai kwaya,King ya wani girgiza Kai alamar ya fara daukan chaji shima yace,Hayaki sai dai na shaki na Titi My Guy, Mashkoor yace Look King akwai wata yarinya tayi Fuck Up,the Girl done Mess up man, Wai Ni Ina sonta Tace Banda hankali wani yaro Rabiu Yana Nan malamin makarantar Islamiyya ya kwace min ita,King Yana lumshe Ido duk ya fita a hayyacinsa ya karkace bakinsa gefe Daya irin na Yan shaye shaye cikin kakkausar da mayen muryarsa yace She must Collect,Dole ta karbi Certificate na abinda ta aikata,Na yarje muku kuci mamanta,shi Kuma Yaron za a tare shi dole mu bashi Sample,Sumarsa me laushi ya yamutsa,yace guys gobe Mommy da Dad zasu shugo garin Nan Karku zo gida na sai bayan sun tafi,Abdul yace  Confirm,No wahala,Jibril Jibson ya Mike Yana tangal tangal yace ya za ayi ace baza mu zo gidan King ba,The sweet Boy,Cikin zafi da daga Murya King Ahmad yace hey What's up man Ina magana kana magana kana hauka ne? I'm sorry cewar Jibson ya Fadi a kasa Yana mayensa,da ganinsu kasan talakawa ne Ahmad shine me kudin shike musu komai,Haka Mashkoor Yana da kudi shima Amma ba Wani da yawa ba,Sai Abinda Ahmad yace shine King dinsu,duk wani rashin mutunci da sukeyi a gari shine yake daure musu gindi sai da sa hannunsa akeyi,Ba Wanda ya Isa ya nuna su da yatsa,Dai Dai ne Basu San da zamansu ba musamman Ahmad King din Wanda ya fita daban sabo da Naira da hutu,suturarsa Kawai abin kallo ce,Dukkansu baza su wuce 30years ba zuwa 34years,Ahmad 34yrs yake cif.

Washe gari da Yamma su Mashkoor da abokansa gaba dayansu har King din nasu Ahmad machine sababbi suka hau kowa da nasa Kuma duk King ne ya Siya musu  kowa da nasa King shine a gaba suna binsa a baya sun kure Masa gudu sun biyo Hanya duk Wanda Bai matsa ba sai dai su bige shi ba ruwansu,sabo da an sansu Ana ganinsu ake kaucewa,Can layin da Islamiyayyar take suka tsaya Suka Parker machinansu,King shine kadai ya zauna a saman nasa suna ta Masa Kirari suna Our King,Fresh Boy,Sweet Boy,shi Kuma Yana ji da Kansa,Suna Haka sai ga malamin Islamiyya ya taho zai wuce matashi da shi Yana tafiya cikin nutsuwa Baki da shi,Tare shi Mashkoor yayi tare da cewa Yawwa ga dan Iska ya Furta tare da tallafe Masa keya,King ya Mike cikin maye yace kana gaba na kana tsaye,Robar Lemo Wanda ciki hadin

kwaya ne a ciki Yana Sha ya daga ya tsiyaya wa malamin Islamiyya a kansa,Nan suka rufe shi da duka Wai yayiwa Sarkinsu magana a tsaye,Wata Mahaukaciyar mota ce me kyau da tsada ta taho a hankali,Mommy da Yar Autarta Humaira sai Daddy Mijinta a baya gaba Kuma Kanin Ahmad ne Saddiq da matarsa Mufida a Gaban mota suna tafiya, Saddeeq shi ke tuka motar,Daddy yace ai Kinga Ahmad din ma gashi Nan da Yan Iskan abokansa,na gaji da zuwa Kaduna akan Yaron Nan wallahi,Na rasa wannan masifa data sameni,Kinga Ni yanda suke dukan wani,Kanwar su Humaira Tace ga Yaya can da kayan maye a hannunsa, Saddiq ya tabe Baki tare da cewa kalli Askinsa Ana ganinsa anga Dan Iska,Mufida matar yayan Tace kuyi Masa Addua Kawai.

A wajen Suka Yi parking sai tsawar Daddy dinsa yaji a Kansa Ahmad Mene Haka? Baka da hankali ne,duk suna mota ba Wanda ya fito sai Mummy da Daddy,Daddy ya tashi malamin makaranta Wanda ya ci duka da gudu ya arce Yaron,Su Mashkoor suka kame a Gaban Daddy tare da Sara Masa kamar suna Gaban wani Soja,Zaga Daddy da Mummy suka shiga Yi suna musu Sannu da zuwa Wai Nan murna ce da girmama Iyayen Ogansu,Bash kuzo mu Basu kariya Guys ba Wanda ya Isa ya daga Musu yatsa a Birnin Kaduna kaf.

Tsaki Daddy ya ja Yana Jin yanda suke wa Ahmad Kirari,Wandonsa ya kalla wani shegen crazy an Masa daga daga,Askinsa ya kalla yace kalli yanda ka maida kanka Ahmad, Dariya ya Shiga Yi ta mahaukatan Yan maye,Mommy Tace Ahmad Dina meke damunka muje gidan da kake,Daddy yace shiga mota mu tafi,Wani fareti ya shiga Yi a Gaban Daddy Yana dariya cike da maye Yana karkace Baki yace No...no Ni a bike Dina zanzo kasan Ina Jin dadin bike Dina Kawai kuje zanzo daga baya,Tsawa Daddy ya daka Masa shiga muje,Amma ko a jikinsa sai ma Dariya da ya Shiga kyakyatawa irin ta basawa Yana kallon Daddy din da Mommy,Dole Haka Suka shiga mota Suka tafi shi Kuma shi da Abokansa suka take musu baya a machine suna tukin ganganci Dan Ahmad harda dage kafa Daya ya daura ta can sama Yana tuki da kafa Daya,Har katafaren gidansa Suka shiga sannan abokan daga bakin Gate Suka tafi gida abinsu shi Kuma yayi Horn me Gadi ya Bude Musu Gate,Bayan sun Shiga Suka firfito da akwatunansu,Wani handkerchief ya daura a wuyansa ya tsaya a Gaban Mommy Dinsa Yana zagata cike da maye Yana cewa Mummy...Mummy....Momma....You are looking Good ya furta tare da rungumeta yace Ina sonki Mummy,rokonsa ta fara Tace Dan Allah ka nutsu Ahmad,Da karaji Daddy yace Mene ne kike rokonsa, why are you Begging him,Dan ubansa tunda bashi da hankali sai yayi ai,Why...why...Daddy Ni dama fa ba tun yau ba nasan baka kaunata,musamman idan ka saka wannan farin Glass din naka sai ka dinga kwana idan anyi Nan sai kayi can,Ido Daddy ya zaro Yana kallon rashin kunyar Ahmad,Kaninsa Sadeeq ne yace ka canja wallahi Yaya,Cikin karaji ya tasowa Saddeeq Yana ce Masa Kai dalla gafara Ina yayanka zaka min fada,ko Dan kaga munyi Kai Daya Ina da gemu kana da gemu shine zaka rainani Kai wuyanka ya Isa yanka ko,Ka dai gyara halinka,Tafiya yayi zai Mari Saddeeq Mummy ta rike shi tana rokarsa yayi Hakuri, Humaira ya riko tare da Rungume ta yace kanwata kin girma,ya school? Tana Dariya Tace nayi Candy Yaya,Wow ya Furta tare da dagata sama ya ajiyeta suna Dariya,Matar Kaninsa ya kalla Mufida nutsatsiya kyakyawa yace matar mu ya gida fatan wannan shashashan yana kula Dake? Dariya Mufida tayi Tace sosai ma,yace Good muje ciki matar mu ke kadai ce tawa a gidan Nan,kishi ya Kama Saddeeq ganin Ahmad Yana shaye

shaye tunaninsa har Mata yake bi sai kishi ya kamashi yace kaje kayi aure wannan matata ce Ni Daya ka daina cewa matarmu yawwa,Stupid Boy Kawai Ahmad ya furta Suka jera da Mufida suna Hira duk da a maye yake Amma Yama Saba Bai fiye buguwa da yawa ba, Sadeeq da Sauri yazo ya shiga tsakiyarsu ya rike Hannun matarsa ya janye ta da karfi,Baki Ahmad ya tabe ya Rungume Humaira Suka Yi ciki.

Bayan sun huta sunci abinci Daddy yace da dare Yana neman kowa za ayi Meeting zasu fadawa Ahmad dalilin zuwansu yanzu ma again, Har dare yayi Ana jiran Ahmad Amma tuni ya bar gidan Yana can suna shaye shaye har 1am Bai dawo ba sai kowa ya hakura yayi bacci,Da safe ma Ana ta jiransa har sun karya Shuru Bai dawo ba,can sai gashi a bige ya Fado palon ya tafi taga taga zai Fadi sai ya cije ya Dage Yana bude Ido da kyar Yana Rufewa ya fada saman kujera shirim kusa da Daddy yace An tashi Ify?
Ina....Ji...ji..jinku.....m....me.....yaaaaaa....ya...kawo ku Kuma yanzu Kun wani sake dawo min gida...na tuna ance jiya za ayi meeting yanzu gani Ina da abin Yi ku Fadi meke tafe daku har zuwa gidana? Daddy ya zaro Ido yace au gidan ka ne ma? Gidana kace gidanka? Yace gida nane Mana Kai ai Temporary Owner ne Nan gaba mutuwa zakayi naci gado,Ran Daddy ya baci yace gidan Nawa? ni da gidan gida ka gaje min gida?aikin uban me kake Yi? Kaki nutsuwa,Mummy Tace Ahmad Dan Allah ka tsaya ka nutsu kaji abinda ya kawo mu,Ina jinku Mana ku fada,Kaninsa Sadeeq ya tabe Baki,Humaira Tace Addua zaku Masa please,Ita Mufida ita tunda auro ta akayi Bata cikin wacce zata Shiga matsalar Family tana bedroom.

Daddy yace kana ji na Ahmad? Yace Yeah,yace so nake ka bar Nan ka dawo Lagos kazo mu koma inda nake da Zama can Lagos Ina so Zan maka Visa mu tafi London gaba Dayan mu,akwai Company na Dake can kayi Handling dinsa kayi Aiki a can ka dogara da kanka,kullum sai dai na cika maka account da kudi kana kashewa a banza,ya kace?Ahmad yayi Dariya yace kasan amsata Mana Daddy Ni bazan je ba wata kasa da zanje Kuma Ni bana son Lagos a Nan gidana Zan zauna a Nan Zan mutu,Daddy yace to gidanka ne? Ni da gida na,Mummy Tace Dan Allah Ahmad ka bimu mu tafi kaga London ko Turkysh ko Kuma a Nan kasar Nigeria sai kayi Aiki an baka company kyauta ka dogara da kanka Kaine fa babban Danmu Kai ya kamata ace ka nutsu,kalli kaninka ya rike nasa a Lagos Yana aikinsa gashi da Degree da Masters Kai kuwa Degree daya ma da kyar muka samu ka karasa a Russia,Ahmad yace kunga fa Ni ba inda zanje Kawai ku daina Bata bakinku mutanen da basa son bakar fata ku Kun damu da su kuje kuyi harkarku,kuyi rayuwarku nima nayi tawa,yawwa kunji ba inda zanje ya tashi Yana tangadi ya haura sama,ya barsu a Nan cike da Alajabi yafi karfinsu.Daddy bakin ciki ya Kama shi ya juya kalli Mommy tare da galla Mata Harara yace Kinga danki ko kin ga abinda kika haifa ko? Mummy Tace au da nane ma Ni Daya? Daga Nan suka fara cacar Baki.

Aamna ce ta fito tsakar gida sanye da wani gajeren wando ko gwiwa Bai ba Milk color,da Yar rigarta t-shirt dark Blue,Hannu biyu ta zuba a cikin aljihunta tana tafiya tana yan ga,Cinyoyi da kafafunta lukutaye,Mama ce ta Bude Baki Tace Yau me Zan gani? Aamna kece yau kika Yi wannan shigar ke da bakya so aga jikinki yau me Zan gani na Shiga Uku Kamar Namiji, Malam fito ka gani,Kuma wandon ma na Yan Ball ta saka wani katon buje,Aamna saman bakin rijiyar tsakar Gidan ta zauna daram tare da Harde kafafu,Baba ne ya fito da sauri shima ya Bude

baki,yace kwaya kika Sha? Nan fa gidan haya ne ga maza Wanda da matansu,Aamna Fuska ta bata tare da Furta naga Alama a gidan Nan magauta sun min yawa,Magauta sun sani a gaba Ana so aga baya na,to Zan dauki mataki

Mama kirji ta dafe Tace Aljanu ne da ke Aamna? Tace Ni yawwa da ace akwai Sigari a kusa ma yau Zan fara zukawa sai anayi ana feso da hayaki ta Hanci da baki sabo da Naga an tsaneni a gidan Nan so ake na lalace to wallahi Zan bi duniya kowa ya huta Matukar ba a daina uzura min ba.

AsmaBaffa
10/26/21, 8:51 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA🌵🌵

DUNIYATA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

NA KUDI NE

GA MASU BUKATAR SHIGA GROUP DARI BIYU 200 NE.

ACCOUNT NUMBER
0175487861
ASMAU GARBA MUHAMMAD GTBANK.

MASU TURA KATIN MTN KO VTU GA NUMBER
08033933642

'YAN NIGER KU NEMI WANNAN NUMBER
+227 90 79 59 39

6-10

Official

By
AsmaBaffa.

PAGE NAKU NE

SAMEERAN GAYA
FLOWER
AUTA
AIDA MAMAN TASNIM
CHOICE

Aamna ce a Resturant dinsu tana hadowa customers abinci tana bin wakar Dake tashi a ciki da manyan speakers sabo da Jin dadin masu cin abinci a wajen,idan kaji uban kida kamar kana club,ai Aamna Bata San Sanda take kada Kai ba tana bin wakar da Baki tana bi layi layi inda masu jiran order suke zaune tana ajiyewa kowa nasa,duk Wanda ya kalleta sai yayi Dariya yanda Bata ji bata gani bilhakki aikinta takeyi tana rawa da kanta,wani babban mutum Bai San Sanda ya saki Dariya ba Amma Aamna ko a jikinta sai ma data soke Wayarta a jikin aljihun skert dinta,wani kida ya dado ta tayi tafi tare da daura Hannayenta biyu a kanta tare da Furta wayyo Baba.... Ai kuwa wasu duk sunyi tunanin kwaya take Sha Kawai sai Dariya akeyi tana Basu nishadi gata kyakyawa ta karshe.

Wata Budurwar da saurayinta Tace wannan Yarinyar ba karamar Yar Iska bace ko a jikinta duk mutanen Nan ko kunya babu,Matashin Yana zuba Dariya yace ai shi yasa nake zuwa resturant din Nan,sabo da ita nake zuwa wlh abin Dariya Zaki gani iri iri tana yi,Budurwar kishi ya turnuketa ta kalle shi ta watsa Masa Harara Tace Ni Kuma fa? Allah ya tona maka asiri ka Fadi gaskiya,shi yasa ko yaushe kace muzo Nan munafuki Ashe Dan ita kake zuwa,sai lokacin matashin ya tuna tabargazar da yayi a Gaban Babynsa.

Aamna kuwa wani sufa tayi da takalminta a tiles din tana tafiya a Haka Kamar wacce ta hau takalmin Taya Wai duk cikin saurin Aiki ne,Siyama kawarta itama Haka ta shararo da sufarta Hannunta dauke da tire da kayan Abinci

Washe gari da Ahmad ya fita Wata hanya Suka samu tare da tare hanyar mota kowa idan yazo sai dai ya juya Inda ya fito,sai da aka kawo Yan Sanda wajen suka dinga fada da Yan Sanda,Bincike Dpo yayi Dan waye? Ai Yana ji an Fadi waye Baban Ahmad a kasar sai ya tsorata yaje har gidan ya samu Babansa tunda ance yazo Yana Kd ma,Bayan sun gaisa Dpo ya Kai karar Ahmad yace mun kyale shi ne sabo da Kai da irin taimako da kake Yi a kasar nan sabo da Haka Dan Allah Ka Jawa danka kunne,Daddy ya Basu Hakuri tare da sanar musu duk irin kangarewar Dansa,Dpo yace sai dai ku dage da Addua Amma a tsawatar Masa Kar mu dauki mataki aga Bamu kyauta ba,Bayan sun tafi Shuru Ahmad Bai dawo ba sai cikin dare Daddy,Mummy da Saddeeq duk suna jiransa sai kuwa gashi ya dawo a make,Daddy ya lullube shi da fada ba ji ba gani,Kaninsa Sadeeq yasa Baki Nan take Ahmad ya shaki kwalar Sadeeq zai Duke shi,Mommy ta rirrike shi tana kuka tana cewa ka Bari Mana Ahmad wayyo na Shiga Uku Ni,Daddy kuwa Mari ya kwadawa Ahmad,Nan take ya dafe kuncinsa Daya da mamaki sai Kuma ya sheke da Mahaukaciyar Dariya Yana Nuna Daddy da yatsa Yana ka mareni akan wannan kanina shi zai ce zai min fada,Daddy yace banza shashasha sai na sake marinka wallahi,Juyawa Ahmad yayi ya haura samansa a fusace,Humaira kanwarsa da Mommy suka bi bayansa suna ta bashi Hakuri suna lallaba shi,Ahmad yace kina gani Mommy marina fa yayi Akan kanina,Ni dama nasan Daddy Baya kauna ta,Bai so aka haife Ni ba gaba daya,Ba Haka bane Ahmad Yana sonka Nima Ina sonka,Yace ai nasan ke kina so na Amma Daddy Baya kauna ta Ni ku tafi ku bani waje Kawai ya dakko kwalabar barasarsa ya shiga korawa,Mummy suka fita sun San halinsa idan yayi Fushi.

Ranar da su Mymmy suka kwana Uku da Yamma Ahmad,Mufida matar Saddeeq da Humaira Autarsu suna Garden suna Hira Ahmad Yana ta musu magana irin ta Niggogi irin ta Yan kwaya suna ta dariya, Sadeeq ta sama ya hango su ta window kishin matarsa ya kamashi ya sakko tare da Fitowa Haka ya dinga zaga garden Yana kunci,ya Shiga ya fita ya dawo ya wuce ya sake dawowa,Mufida ta fuskanci wani Abu Tace lafiya dai Baby? Cike da bala'i yace ba lafiya ba ki taso ki kula da mijinki kin zauna kina wani dariyar banza da wofi,Ahmad yace ya zaka dauke ta muna Hira,Hira mukeyi Kai wanne irin yaro ne? Tsaki Saddeeq Yaja ya Fisgi matarsa Suka tafi,Juyawa yayi Suka ci gaba da Hira da Mufida kanwarsa suna ta dariya abinsu,Wayar Humaira ya karba ya juya yace irin wannan waya Haka sis idan kika hadu da irinmu Yan duniya ai sai mu tare Miki Hanya muyi Miki fashin ta,Dariya Suka sake yi Yana ta Dariya ba ji ba gani irin ta Yan kwaya,yace sis yanzu ma Dan na sanki ce ke kanwata ce da su Jibson Zan turo su kwace ta,Dariya Suka sake Yi a tare Humaira ta daki kafadarsa tare da furta Kai Yaya,Kallon Kanwar tasa yayi sosai yace sis you are cute wooo...see your Nose fine nose,kina sa Nikaf fa Kar ki hadu da irin su Brown abokina I swear Kamaki zasu Yi su Sha harka kina kula fa tam,hope Baki kula samari Kar wani yazo ya taba min kanwa Naga kin fara girma abubuwa sun fito Haka, zanzo har Lagos nayi yaki ne idan wani ya Bata min ke, Humaira harda rike ciki sabo da dariya ga kunyar abinda yace,shi kuwa ko a jikinsa

Kwanan su Mummy biyar suka fito cikin Shirin tafiya Ahmad Yana binsu a baya Yana ta murna zasu tafi yanzu ma su barshi ya sakata ya Wala,Mummy ta Rungume shi Tace ka Zama mutumin kirki Dana tunda baza ka bimu ba ka kula da kanka,yace to Mummy na, Saddeeq yace wannan ba Wani shiryuwa da zaiyi Nan take Ahmad yayi Kansa da bala'i,Mufida tazo Tace Yi

Hakuri kyale shi Yaya King,yace yawwa matar mu ki kula da kanki,Da sauri Saddeeq ya janye matarsa cike da kishi,Ahmad yace wannan wanne irin Dan Uwa ne Haka? Daddy ne ya Kira Driver su wurin Tara yace ya kwace Motocin Dake Hannun Ahmad kaf,Dama Bai damu ba yace tunda Yana da kudin machine ya ishe shi,Daddy kuwa yace tunda baza ka nutsu ba ai Motocin da kudi na ka siya na karbe,Ko a jikin Ahmad yace kuje da ita,Daddy yace dole ma ko baka fada ba,kudi dai Zan na tura maka na kula da kanka sabo da hakki na ne,gida ma kayi ta Zama Amma ka sani ba gidanka bane Nawa ne.

Mummy Tace please Ahmad ka daure nasan kana Sallah Amma baka Yi sai Sanda kaga dama ka gyara Sallah ita ce komai awajen musulmi,Ahmad yace sured Mum Zan gyara ki yarda Dani,Nafa sanka Ahmad tun yaushe kake cewa zaka gyara Amma kaki,Ki yarda Mum Inshaallah,nine fa Ahmad dinki,Sunana fa aka kalla aka yo Guarantee trust Bank,Dariya sukayi har Daddy,Yawwa ehem Dad karka manta na tura maka new accnt number Dina Ina bukatar kudi kudina sunyi low,Daddy yace Zan tura ai Ina sane sakaran banza.

Ahmad Yana ji suka shiga mota Gate man ya Bude Musu suka tafi Basu bar mota ko Daya a Hannun Ahmad ba aka su Suka kwashe su,Suna tafiya ya dauki waya tare da Kiran Abokansa su zo Iyayensa sun tafi sai murna sukeyi yau suna gidan King.

Me Gadi ya kalle shi kawai ya jinjina Kai Amma Ogansa Yana da Hali me kyau Kawai matsalarsa shaye shaye da Rashin Ibada sosai.

Aamna tana cikin Restaurant dinsu tana ta Kai abinci wajen masu ci,sannan Kuma suna Hira da Babbar kawarta Siyama wacce aikinsu Daya,tare suka Yi HND a Poly,Rashin samun Aiki yasa suka nemi Aiki a sabon Restaurant da Maman kawarsu Saratu ta bude sabo da Talaucin da suke fama da shi, Siyama Tace kawata Nima fa Allah ya kusa daga Ni,na manta ban fada Miki ba Nafa fada cikin kogin son Faisal,kwanan nan ma nake so na bashi dama ya turo magabata,Murmushi Aamna tayi Tace wow I'm Happy for you Kawa But Ina ganin Kamar kinyi gaggawa ya kamata ki Bari ku fahimci juna sosai Bai Yi ko 1month da fara zuwa wajenki ba,Karki je garin sauri da matsuwar Aure a samu matsala,Siyama ce ta dakatar da Aamna ta hanyar daga Mata Hannu tare da Bata rai,Tace Ni fa Aamna ban Gane Miki ba,ai sai kisa nayi zargin ko bakya kauna ta kina bakin ciki na samu Miji ke Baki samu, Subhannallahi Siyama Allah ya kiyaye ko wani da musulmi bazan Masa bakin ciki ba bare ke da kike kawata wacce muke kashewa mu rufe tare Allah ya kiyaye min,sabo da Haka Dan Allah gobe a daura aurenki da Faisal ma Bai Dame Ni ba Bai shafe Ni ba,babu abinda Zan tsinta ciki,idan wahala ce ma ke Zaki Sha abarki mu Yan jaje ne.

Siyama Tace ai ke dama bakya kaunar Aure bakya so kiyi Kuma bakya kauna wani yayi,gaba kike da Sunnar ma'aiki sabo da ke Kinga Baki da samari idan ma kin samu guduwa suke yi,idan Zaki hakura ki auri kowa kika samu ki hakura yanzu an daina auren Soyayya wa zai Iya rike ka Kawai ake Nema ya zaka ci ka Sha ka rayu inda zaka huta da iyayenka,Faisal Doctor ne matarsa mutuwa tayi wajen haihuwar fari,yaro matashi ga kudi me nake jira ai yanzu ba a jira Yan Secondary ma idan suka samu Miji aure suke Yi,kiwa kanki fada,shekaru tafiya suke Yi mu matane,ko ba komai kar tsufa ba aure har mu zo lokacin Haihuwar mu ya

wuce,Aamna Tace Allah Baki Hakuri ayi aure lafiya mu muna Nan daram za muci gaba da Addua Allah Bai manta damu ba Yana sane da mu,Siyama Tace ae aci gaba da Zama lafiya Ana gantali, wanne gantali mu da muka yo rako duniya,gamu an halicce mu a Nigeria babbar jarabawa,ga talauci,wannan duniyar Ina Dadi cikinta, aikinsu Suka ci gaba Yi suna Hira kamar ba sune Suka Yi fada ba,dama sun Saba fada da junansu.

Washe gari Bayan ta tafi wajen Aiki Sai ta Iske Siyama Bata karaso ba sai Aamna da sauran ma'aikatan,Siyama kuwa Direct gidan Su Aamna ta wuce,Mama ta tarbe ta,Tayi sa'a Baba ma Yana gida,Bayan sun gaisa Tace Baba wata magana ce ke tafe Dani da Kuma shawara,Baba yace Muna jinki Siyama,Siyama ta Basu labarin yanda sukayi da Aamna Akan Maganar Aurenta da Faisal,Baba yace na rasa dalilin Yarinyar Nan da Bata kaunar Aure,Siyama Tace Ni abinda na fahimta Baba Aljani ne ya auri Aamna Kawai shawara ku kaita gidan malamai a Nema Mata magani shine Kawai,Mama Tace tabbas yarinya kinyi nisan hankali,shi yasa ake son kawa irinku ta gari,Haba biri yayi Kama da mutum cewar Baba,yace Inshaallah gobe zamu dauketa mu tafi da ita kauyenmu can Sokoto mu Nema Mata magani,dama jiya anyi Mana Albashi sai a fasa siyan komai mu tafi neman magani Allah yasa a Dace kafin ayi Auren Zuhra itama ta samu nata Mijin mu hada a Sha rikitiba sosai,Haka Siyama ta fito ta zo wajen Aiki a makare ranar Aamna Bata San dalili ba tana komawa gida taga Baba da fara'a ya amsa Sallamarta,ta Gaida shi Kuma ya amsa,Mama ma Haka,Aamna dai hankalinta Bai kwanta ba tayi mamaki,Zuhra kuwa tana ta karasa miyar Taushe,Mama Tace Aamna Sannu da Aiki zauna na kawo Miki abinci,Aamna mamaki ya kamata sai binsu take da kallo har taga an kawo Mata abincin a flask Wanda a baya ko rufe Mata ba ayi bare wani Flask,ta kalli abincin ta kalli Mama Tace Mama ko dai maganin bera kuka saka min zaku kashe Ni?Mama tana gyara daurin zaninta Tace haba Aamna kin taba ganin Iyaye sun kashe yarsu? Aamna Tace na nawa Kuma,bazan ci ba gaskiya wallahi,Ina so na Kara tsawon Rai,bana so na mutu yanzu sabo da Haka Ni bazan ci ba ko ruwan gidan Nan na daina Sha gaskiya.

Babu irin lallabawa da lallashin Aamna da Iyayenta Basu Yi ba Amma Taki cin abinci ko ruwa Bata Sha ba,Baba ya kalle ta yace Ki shirya Aamna gobe zamu je Kauye gaishe da Yan Uwana da abokan arzuka,Aamna Tace Amma ba a fada min da wuri ba na shirya,shike Nan Allah ya kaimu goben Amma kafin mu tafi Zan sanarwa ogar mu sabo da gudun matsala,Ba damuwa Aamna cewar Mama.

Aamna kwana tayi Bata ci komai ba duk da cewar taci a Restaurant dinsu,Washe gari da wuri ta nufi gidan su Saratu kawarta,Saratu tana bacci har Aamna ta Shiga aka Mata Sallama da Maman Saratu ta Mata bayani zasu Yi tafiya,Hajiya Tace Baki da matsala Aamna Amma kin San dai Baki da kudin fashin da zakiyi,a cikin Albashinki za a cire na Iya kwanakin da kika Yi bakya zuwa Aiki tunda kin San ba aikin Gomnati bane,Gomnati ce ake cin banza Ni Kuma ba Gomnati bace,Aamna Tace ba damuwa Amma,Hajiya Tace a dawo lfy ta Mike tare da haurawa sama,itama Aamna ta Mike ta tafi,dama sun Gama shiri Kaya Kawai ta canja wani lace ja me adon Golden, me Dan kyau Riga da skert,Ta sa takalminta na Sallah da jaka duka Golden,Zuhra Kawai aka Bari a gida sabo da makaranta suna Exam,Napep muka shiga zuwa

Tasha daga can Muka hau Motar Sokoto tana ta Adduointa, sun Dade suna tafiya Amma sai kusan dare muka Isa can kauyen Su Baba da Maman su,Asalin gidan Iyayen Baba muka sauka a bangaren Baba,Dakuna biyu da toilet ne na Bulon Siminti Wanda Baba ne ya Gina ya sumulmule ko Ina da Siminti idan sunje can suke sharewa su zauna a gadon uban su,Ko wanne daki akwai  Ledar tsakar daki da katifa katuwa da Bedsheet,sai kwanikan cin Abinci da Tukwane har da Reshio dinsu,komai na bukata akwai dai dai talaka,Mutanen gidan Suka tarbe su dake Babban gida ne a bangaren Kanin Baba wato Kawu Ismail muka sauka.

Sai da suka ci abinci suka huta sannan suka gyara bangaren Baba ita da Mama, Bedsheet din Yana wanke a cikin kayansu suka shimfida abin su,a saman Katifun dakunan Guda biyu,wanka suka Yi tare da Yin Sallar Isha,Baba suna Kofar gida shi da Kaninsa da sauran dangi,suma dakinsu Mata ne Yan Uwa aka taru suna hira sai ga Baba da Kawu Ismail,ba tare da Bata lokaci ba Baba yace ke Aamna taso muje Ina Maman taku ta taso mu tafi muyi abinda ya kawo mu ba dadewa zamuyi ba,Hijab me Hannu Aamna ta Daura saman Riga da skert Dinta na jar Atamfa,Mama kuwa Mayafi ta yafa tare da Fitowa zasu tafi,Baba ya kalli Mama yace wannan tayani gantalin Wato baza ki daina yafawa ba ko? Har yanzu fa da sauranki Baki Gama Expire ba,Dariya Aamna tayi tare da sadda kanta kasa sabo da fadan Baba da Mama ya rigada yabi jininsu,Mama Tace Kai ka sani dai,Baba yace ya kamata ki daina Narka kibar Nan ke ba Wani abinci kike samu me Gina jiki ba Amma kullum Hawa kike kamar ana buga Miki Iska,Mama Tace sai ka fara rage taka kibar tukun,Haka suka tafi Suna ta cacar baki,Kawu Ismail kuwa fada yake ta yiwa Aamna lallai ta fitar da Mijin Aure,yace abokan haihuwarki daga me Yara hudu sai me Yara biyar a Nan kauyen,ita Aamna Bata taba sanin Mama da Baba Basu Suka haife ta ba,tasan dai suna Dan nuna Mata banbanci tsakaninta da Zuhra,Haka Dangin Baba tasan Suma sunfi son Zuhra,Haka ma Dangin Mama,Sai wani gida da ake kaita tun tana karama a cikin Sokoto city wani me kyau gidan mutanen Sudan ance Wai Yan uwane suma

Gidan wani mutum suka je Malam me Almajirai,Bayan sun zauna Aamna sai ji tayi Baba suna ta Masa bayani akan bata samu Mijin Aure ba,Kuma ko zancen Aure akayi Aamna Bata kauna,Malamin Yana tauna goro yace Ashsha Aljan ne namijin dare ne wallahi take fama da shi,Mama Tace biri yayi Kama da mutum,Baki Aamna ta Bude tana kallon Iyayen Nata,Malamin yace yanzu Zan kwana Uku ba bacci Ina wani Aiki Amma dole aikin Nan kullum sai an yanka zakara Guda Uku har na kwana Uku,Baba duk talaucinsa sai yace dama na samu wasu kudi Nan take ya biya kudin zakaru tare da bawa malamin dubu goma kudin Aiki,yace Nan da kwana Uku ku dawo ku karbi wata laya wacce zata soke ta a cikin gashinta,Fuska Aamna ta Bata kamar zata saka kuka,Ace Allah Bai kawo lokacin Abu ba Amma Iyayen nata basa gani.

Suna Fitowa Kawu Ismail yace saura wajen Malam Kare Aiki,Wannan malamin sanatoci layi suke Yi a Wajensa,Aamna ta girgiza Kai Tace Baba wallahi ba kyau,Wannan shirka ce baza a fadawa Allah bukata ba sai Malam,Baba ya kalleta cikin duhun dare yace ai ke Aljanu gareki sun aureki Bai ma dace a saurare ki ba sabo da ba a cikin hayyacinki kike ba,Yo ka biyewa sakarai cewar Mama,Kawu Ismail yaci gaba da cewa inshallah Kuna komawa zata samu Miji itama,Wannan malamin da suka je Wajensa Rubutu yayiwa Aamna a tafin Hannu yace lashe ai magauta ne Suka mata asiri kuma makwaftan ku ne,Takaici yasa Aamna Tace Allah ya tona

muku asiri masu hada fada tsakanin Musulmai,Rankwashi Mama ta zubawa Aamna tayi Shuru,Lashe Kawu ya furta Yana zaro Mata Ido,Haka ba a sonta ba Tace Allah na tuba bana nufin kowa da sharri sannan ta lashe su Baba suna ganin Aljanu ne ke hanata Sha,Haka Suka je wajen wani malamin shima yayi nasa sannan suka jira Bayan Kwana Uku Suka karbo duk wasu Magungunan da aka hada Suka dawo ,Duk wani Rubutu da magani da Suka bawa Aamna Kan tayi amfani da su sai ta samu jikin katanga ta zubar babu Wanda ya sani,Laya Kuma Haka ta soketa da pin a gashinta sabo da kullum Mama sai ta duba gashin dole ta soke Laya a gashinta.

Su Baba Basu Sani ba suna ta jira suga saurayi yazo neman Auren Aamna Amma Shuru,ga Kuma bikin Zuhra yana ta gabatowa,duk sunyi Anko da Dinku Nan su na biki duk wani shiri da za ayi mun Riga sunyi,Baba ya siyar da manyan shanayensa Guda hudu dake Kauye sabo da Haka ba Harkar Talauci sunyi komai cikin rufin asiri,Adam Ango ya hada musu Dinner zazzafa me kyau ranar Saturday,Sunday za a daura Aure a Kai Amarya,daga Aamna sai kawarta Siyama bata gayyaci kowa ba,Amarya dai taci Uban gayyar kawaye wurin Dinner,Biki saura kwana daya a fara Aamna tayi lalle da gyaran gashi,amarya kuwa ta Sha gyara sai sheki take zubawa,dangi na nesa sun zo sai tsiya ake yiwa Aamna kanwa zata Yi aure ta bar Yayarta,Haka suka Sha bikin Zuhra da Angonta Adam anyi an Gama Ify tare da Kai Amarya da gararta,gidan Adam madaidaici ne me kyau harda gate yayi kyau gidan,ga Yar motarsa me kyau Toyota,Itama Zuhra Baba ya Dage ya Mata Kaya masu kyawun gaske.

Ahmad Yana kwance a makeken Gadonsa Yana zuba bacci,wayarsa ta dinga ruru gashi ya kasa tashi sai da kyar ya farka ba tare da ya Bude idonsa ba ya jawo wayarsa yaga number Mummynsa dama ta fada Masa zata zo ta ganshi a kaduna ita kadai kasancewar Daddy,Saddeeq da Humaira suna Saudiya Umrah,Cikin Muryar bacci ya Kara Wayar a kunnensa tare da Furta Hello Mummy......Muryar Namiji yaji yace da Allah me wannan Wayar sunyi Mummunan Hatsari Driver ya mutu ita Kuma tana asibiti da Allah ayi sauri azo,Firgigit ya farka Yace what....?cikin gigita yace please fada min Address din Asibitin,Nan take ya fada Masa,Da sauri Ahmad ya figi machine dinsa sanye da wando 3qutr da Riga t-shirt fara tas sai asibiti,a gurguje ya fada ciki Yana tambaya aka kaishi Emergency Nan ya Iske Mummy Rai a hannun Allah.

Aamna Yau da matsanancin ciwon Mara ta tafi wurin aikinta gudun kar a hanata kudinta cas sabo da ba aikin Gomnati bane,a Haka take daurewa tun tana aikinta da karfin Hali har abin ya fara gagararta,Siyama ta kalla tana rumtse Ido Tace Siyama dole Zan hakura da aikin yau Hospital Zan wuce a duba min marata ya kamata ayi min scanning a gano min mene a wajen Nan,Siyama da tausayawa Tace Allah ya Baki lafiya kawata a dawo Ify sai munyi waya,Aamna ta daura After Dress a saman Uniform dinta Riga da wando ta fita tana tafiya a hankali ta Isa bakin Titi tare da Shiga Napep zuwa Asibitin da suke ganin Likita idan lalura ta taso,asibiti ne na Gomnati Amma ba laifi akwai kyau.

Tana rike da mara hankalinta baya jikinta tana zuba Uban Sauri tabi wani Corridor,Gaf taji tayi Karo da mutum,wani kamshi me jarabar Dadi ya daki Hancinta,da sauri taja baya ko kallon

Wanda ta buge Bata Yi ba,shima Bai ko kalleta ba hankalinsa baya jikinsa,Bayan tayi magana da wani Emergency ta nufa tana matse kwallar wahala gashi Bata fadawa kowa a gidansu ba,Karo suka sake Yi da juna kamshin mutumin dazu ta sake ji ya cika Mata Hanci Kamar Kar ta daina Shaka,Tsaki Yaja sosai yayi cikin Emergency Yana ta faman yiwa Doctors masifa,Yana cewa a bani Mummy na dole ne,Ni Nace bana son wannan Hospital din me Araha,a bani Uwata wannan so kuke ku kashe min Mummy a Asibitin Gomnati, Wallahi Mummy na ta mutum sai na daure ku,wani babban Likita ne yace Haba Malam Ahmad kake ko wa? Da masifa yace karka sake ce min Malam,Ni ba Malam bane,a masallaci ka ganni Ina Kiran Sallah ko Tafsiri kaga Ina Yi? Idan zaka iya Call me king,Doctor yayi Murmushi sabo da daga ganin Ahmad kasan inda tarbiyya take ma Bai nufa ba,Cikin tausasawa Doctor yace kayi Hakuri zamuyi Aiki iya yin mu a samu ta farfado wallahi Matukar ba a Bata agaji ba ka dauke ta to kafin kaje da ita wani Asibitin zaka iya rasa ta kayi Hakuri idan aka samo kanta sai ka dauke ta idan kaga dama ma ka tafi da abarka China.

Aamna kwance take tana hawayen wahala Ana ta lallaba Ahmad Anki kulata,Cikin masifa Tace da Allah ku rabu dashi azo a duba marata Likita mayu sun kamani sun min Ajiya a marata watakil ma Tukunya ce a wajen ko wani karfen Kun zauna a wajen wannan muma ai ba daga sama muka Fado ba Kuma Nan gaba Aure zamuyi mu haihu,muma Iyayen wasu ne,Wani mugun kallo Ahmad ya aikawa Aamna sannan ya koma gefen Mummy ya zauna Yana cike da tashin hankali,Likita Yana zuwa kanta yace Rannan anyi Miki scanning nace ciwon sanyi ne dake sai kin dage da magani,Aamna Tace to ai har na gaji da maganin, wannan sanyi da naci yake jaraba Kawai,kankara nake Sha ko me?Ni ba Yar Madara ba Bamu da ko fridge ace wani sanyi,Ahmad sai lokacin ya kalli Aamna kadan tana kwance yace Doctor da Allah kazo wajen Mummy na ka rabu da wannan rubabbiyar Sanyi ya Gama kashe ta mijinta shike nan sai asosa Mata asosa,Aamna tunda ta kalli Ahmad Bata sake Kallonsa ba sabo da kyawunsa da wani mugun kwarjini da yake mata,cikin lokaci kadan Doctor ya yiwa Aamna Allurai tare da Bata magunguna,sai gata ta watsake ta warke yayin da Mummy itama ta farfado bayan likitoci sunyi aikinsu,Ahmad sai murna yake Yi,Mummy ta sa Hannunta tare da shafa sumarsa Tace karka fadawa Humaira da Daddy tunda naji sauki yanzu da ace akwai mace wacce zata kula Dani sai ta zauna har a sallame Ni,idan za a samo min Yar Aiki ma Zan biyata kudin jinya cewar Ahmad,Aamna ta dauki Handbag dinta ta wuce kenan taji Ana Neman me Aiki Sai gashi ta dawo baya da sauri tare da tambaya Nawa za a biya Ni?

Mummy ta kalli Aamna sama da kasa Tace daga dubu Hamsim zuwa sama,Aamna ta Bude Baki Tace yanzu idan yau na fara jinya aka sallameki gobe dubu Hamsim Zaki bani? Ahmad yace kaji barauniya, Mummy ce ta kalli Aamna ta daga Kai Alamar ae,Aamna Tace Alhmdllh na karba zanyi Bari naje gida nayo Shirin jinya,Mummy Tace a dawo lfy tana rufe Ido sabo da da kyar take magana ba laifi Mummy ta Sha wahala.

Agurguje Aamna ta koma gida ko abinci bata ci ba ta sanarwa Mama komai,Baki ta tabe Tace yo tunda kinki aure ai sai kici gaba da neman kudin tunda ke kudi ne a gabanki,Baba kuwa Baki ya tabe yace ba abinda kika sani sai neman kudi to a dawo lfy dama bikin Zuhra ya cinye Mana

komai,ita dai Aamna kayanta ta bukata ta hada a karamar Akwati tayi wanka tare da yin Sallar Isha sannan ta wuce Asibitin abinta,tana tafiya kamar Namiji sabo da Tace ta daina Zama ta kirki.

Tana Shiga ta Iske Ahmad ya jibgo kayan ci da Sha da duk wani abin bukata,Kallon Aamna yayi tare da galla Mata Harara cikin kallo na wulakanci,Aamna ta kalle shi itama tare da tabe Baki ta shiga rera Waka lalatacce....lalatacce ne ko a gidan su,da sauri ya kalle ta ransa a bace gashi ba damar fada Amma duk da Haka sai da Yaja Tsaki yace Talakar banza barauniya,Aamna tace ae naji da me kudi da talaka ai duk Allah yaga dama ya bawa kowa,You are very stupid....nayi magana dake? Ina wakata Zaki sa min ths your Smelling mouth,Mind your fucking  Business ya Furta da karaji Wanda sai da Mummy ta farka tare da dafe kanta,duk abinda sukeyi tana jinsu, Nishi tayi Tace Son gobe a canja min Hospital wannan akwai sauro gashi ba Ac,Ahmad Yana maganarsa ta Yan duniya sai kace wani Me wakar Raps yace comfirm Mum,ki Dade kiyi karko and ki mutu AC Mum,Allah ya ja da nisan kwana,Mummy tayi Dan murmushi Tace Ameen a hankali,Aamna ta kalla tace dauki katin Nan ki Siyo maganin da ba a karasa siya ba,Ga kudi Nan a jaka ta,Aamna ta zuge jakar Mummy zata dauki katin da kudin,Ahmad ya fisge jakar ya dauko katin tare da zaro kudi a aljihunsa ya Watso a jikin Aamna yace Jeki,Aamna tayi murmushin bacin Rai Tace ba komai ta Eba ta fita,wurin siyen maganin taje ta Mika katin wani yaro matashi ne a ciki Yace dubu Uku da dari biyu,Me bada maganin da hantara yace ba canji malama,Dan Rainin hankali baza ki samo canji ba.

Aamna ta Bude Baki tana kallon yanda yake masifa,Kai Malam kayi hankali da Ni Kanwar uwarka ce Ni da zaka dinga min magana Anyhow,Uban me kika Isa kiyi,Tas kake ji Aamna ta zuba Masa Mari Tace fito mu Buda wallahi Naga baka da tarbiyya,Wanda suke wajen ne Suka fito tare da raba fadan sannan Aamna ta wuce abinta ta siyo maganin a wani chemist dake wajen Hospital din,tana masifa an fada musu Ina tsoron fada da Namiji,In cakwumi Namiji,inci kwalarsa,muyi dambe ba komai ne a wajena ba,girman Kauye ce Ni,har yanzu da ragowar Tuwon dawa a jikina cewar Aamna har ta Shiga dakin da Mummy take tana fada cewar in Balla Namiji ba komai bane a wajena,In samu mutum in farke Masa makoshi Dan uban mazaje,Ahmad ya bita da kallo sororo Yana mamakin mace da tsaurin Ido Haka,Tsaki Yaja yaci gaba da latsa wayarsa.

Amma ita Aamna ta manta ma da wata marar lafiya take jinya taci gaba da cewa ko wanne Namiji Dan iska,to Billahillazi girman Kauye ce Ni sai na soke mutum da kwalaba,Ahmad ya sake zaro Ido a ransa yace tab Wanda ya auri wannan yayi bye bye da duniya kawai,irinsu ne masu kashe mazaje,Aamna Ta fake da wayo tana zagin Ahmad Tace Dan Iskan mutum Dan Kawai Yana da kyau da kudi ai muma Muna da kyan,ae munji mu talakawa ne sai akayi kaka? Duk kudin mutum Dan ubansa malaikan mutuwa Yana Nan zuwa duk tsayin katanga da katon gate haka zai haura ya zare ruhin mutum,abi duniya a Sannu,Duk wani shiga katuwar mota Haka mala'ika zai zaro ran mutum,Wani mugun razana tayi sakamakon tsawar da Ahmad ya buga Mata,shut up kina min Ihu akan maralafiya Zan fa barar dake,Zan Baki certificate wlh watch your words,Mukus Aamna tayi a ranta Tace wannan shege ne shima.

Babu yanda Mummy  Bata yi ba Akan Ahmad ya tafi gida Amma yaki yarda ya tafi Yana Nan

ya kafa ya tsare.

AsmaBaffa
10/26/21, 8:51 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA🌵🌵

11-15

DUNIYATA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

NA KUDI NE

GA MASU BUKATAR SHIGA GROUP DARI BIYU 200 NE

ACCOUNT NUMBER TA
0175487861
ASMAU GARBA MUHAMMAD

MASU TURA KATIN MTN KO VTU GA NUMBER
08033933642

'YAN NIGER KU NEMI WANNAN NUMBER
+227 90 79 59 39

Official

By
AsmaBaffa.

Page naki ne

Yana Zaune a gefen Mummy ita Kuma Aamna tana zaune a wata kujera,Mararta ce ta sake murdawa da sauri ta rike mara tare da kwala Ihu Mummy sai da ta Bude Idonta,Da Sauri Aamna ta samu gadon da ba kowa ta kwanta tana Nishi tare da Kiran Doctor,Likita ya shigo yace to yanzu me jinya ce zata Yi Jinyar wata? Aamna tana cije lebe Tace zanyi Haka Kai Likita ba ruwanka yawwa kayi aikinka Kawai wannan kudi Ina Zan bar shi,Dariya Likita yayi yace Aamna kike ko? Tace no Amy karka sake ce min wani Aamna Aemy(Amy)Baki Ahmad ya tabe tare da Bude wata Leda ya fito da manyan kwalaban giya masu tsada Yana korawa Abinsa Yayin da Mummy take ta bacci,tana  kwance ta juyo tana kallonsa bata Gane giya bace tayi tunanin wani lemo ne me Dadi na masu kudi,tana ta Kallonsa tana faman Hadiyar yawu,Aamna Tace Wanda yaci shi kadai shi kadai zai mutu,kafin ta rufe Baki yace da Ubanki za a sani a kabari da? Aamna Tace wakata nayi fa,Nima ai wakar nakeyi ko na kulaki? cewar Ahmad Yana cin magani kamar zaiyi Naushi.

Aamna ita kanta Tsoronsa take Yi Amma karfin Hali Irin nata yasa take maida Masa martani,Mummy tana kwance tana numfarfashi tasan me yake Sha sabo da taji warinta,baya kunyar uban kowa,sai da ya Gama Shan wacce zai Sha ya Mike Yana saka wayarsa a cikin wani Crazy 3qurt Jean Kan Mummy ya shafa tare da furta Allah ya Baki Ify Bari naje gida nayi wanka Zan dawo,Mummy Tace baza ka canja ba ko son so kake bakin cikinka ya kashe Ni? Murmushi yayi Kawai sannan yace Zan dawo Mum yanzu 11pm Zan dawo a Nan Zan kwana,aci gaba da Mana Addua Ina so na shiryu Amma Ina,A gabanta ya tsuguna,Mummy ta daura Hannunta a saman sumarsa tare da furta Allah ya shirya min kai Ahmad,Allah ya maka Albarka Allah ya tsare min Kai,Ameen My sweet Mum ya Furta Yana Jin dadi sannan ya Mike ya fita Yana takunsa da wani takama da Isa kamar Dan sarki,Machine dinsa ya hau tare da Bude wuta kamar zai tashi sama,Direct gidansa ya nufa ko da ya Isa gidan Toilet dinsa ya wuce ta Sha gyara ya sakarwa Kansa Shower tare da wanka da wani liquid soap me tsada da kamshi,Bayan

ya Gama a gurguje yayi Sallar Magriba da Isha sabo da akwai Wasa da Addini,Yana Idarwa ya daga Hannu sama Yana Adduoi tare da rokar Allah Allah ka Bawa Mummy na lafiya.

Yace cikin adduar Allah duk da ba Adduar Nan nake Yi ba kullum Allah Ni me laifi ne a gareka ya Rabbissamawati Wal ard Allah ka yafe min laifuka na ka shirye Ni,Ina so na shiryu ya Allah Amma na kasa ya Allah ka dafa min na shiryu,Allah kasa mu mutu Muna Musulmai masu Imani,Allah karka Bari muyi maka shirka,Ka rabamu da Wutar Jahannama,Ka Bamu Ify da tsawon Rai,Allah kasa nayi tsawon Rai Allah bana so na mutu da wuri ka ja kwana na,Ka rabani da cuttuttukan zamani, ya Allah ka raba mu da talauci ka Bamu dukiya ta halak me amfani,Haka ma ya yiwa Daddy da Yan Uwa da Musulmai,karshe yace yace Allah duk da ba damuwa nayi da Mata ba Mummy ta tana so nayi aure Ya Rab ka bani mace ta gari me so na tsakani da Allah,me Ilmin Addini Dana zamani,wayayya,ba Yar Kauye ba,Ya Rab zukekiya ko ko fara ko light chocolate wacce idan na kalle ta kawai Zan washe Baki ba tare dana shirya ba,mace Yar dagwas wacce ta Dan dire ta Dan baje daga kasa.

Har zai tashi sai ya koma ya sake daga Hannu sama yace Ya Hayyu ya Qayyum na kawo karar Daddy wajen ka Allah kasa ya daina min fada kasa ya dinga so na,Allah kana gani dai Tsoho Nan nawa ya tsane ni kamar ba a son ransa aka haifo Ni ba,to Allah Kaine ka halicce Ni ya zaiyi Dani Allah kasa ya daina tsanata Yana gamawa ya Mike tare da zare jallabiyar da ya saka domin yin Sallah,ya dakko gajeren wando wani me tsada iya gwiwa ya tsaya Masa me Dan Fadi Yana da Aljihuna kala kala a jiki gashi Kalar ruwan kasa yasa Riga Armless baka me rubuyu a jiki da zanen fari,Pcap ya saka Kalar wandonsa Takalminsa ma na Yan gayu Wanda suka San mene wanka ya saka Kalar wandon,wow ba karamin kyau yayi ba Kamar a sace shi a gudu,damatsan Nan gasu Nan na mazaje mul mul irin na Wanda ke Dan Gym,turare yabi jikinsa sannan ya dauki key din machine dinsa ya fita,time ya duba 12am wani 24hrs shawarma joint ya nufa,Ko da ya Shiga ga mutane Nan Kamar Rana,Ana ta shige da fice,wasu Kuma suna ta Shan Shisha shi baya Harkar Hayaki,Take Away yayi na Abubuwan ci sannan ya nufo Hospital wurin Mummy.

Bayan Tafiyar Ahmad daga Asibitin Mummy ce ta Dan yiwa Aamna magana da kyar Tace 'ya ta kin iya cire kudi a bank? Nan take tace ae,Tace duba handbag Dina ki dauki Atm card Dina ki ciro min dubu dari,Mamaki tayi lallai masu kudi ne,Haka ta dauka tana mamaki da Bata Santa ba Amma har ta yarda Da ita, Code dinta ta fada mata ta fita da sauri taje ta ciro,Handbag dinta ta sa ta zuba kudin da Atm card din,lokacin Likita yazo yace Hajiya anyi komao dakin da kike bukata ya Zama ready aje a biya kudi sai ku koma ciki.

Yana zuwa ya Iske an canja wa Mummy daki Already Kuma dakin na masu kudi ne Idan kana da kudi sai ka biya kudin daki Guda karami a baka Kai Daya,Gado ne daban na me jinya a dakin da Kuma me cutar nata daban,cikin abubuwan Daya siyo ya Bari masu yawa ciki ta Bude ledoji Aamna taga Naman kaza gasashiya ga tsire daban,ga wata Hanta me ruwa ruwa,sai pounded yam da Miyar Egusi shima a take away daban,Sai Lemuka kamar hauka da fruits ga kayan tea,ga plates da spoons,cups etc,komai an tanada,Ido Aamna ta zaro kenan,Mummy duk jikinta inda taji rauni yayi tsami ko Ina ciwo yake Mata Allah yasa Bata karye ba Sannan Bata Yi Mummunan rauni ba Wanda zai wahalar da ita,Dan Nishi tayi Tace Yar Nan zo ki taimaka min naje bayi,Aamna ta Mike da sauri tare da Rike Mummy ta taimaka Mata tana sannu...Sannu

Baiwar Allah Sannu Hajiya me kudi Allah ya tashi kafada,Mummy sai da Aamna ta Bata Dariya yanda take Abu kamar tsohuwa,Mummy tace Yan Mata Kamar tsohuwa,Aamna Tace ai itace Hajiya shekarata ashirin da Hudu Babana yace na tsufa gashi naki aure,kin San Baba a Kauye ya taso shi yasa halinsa Bai canja ba,Mummy Tace Uhm,Bayan ta kaita har Toilet sai ta rufo Mata kofa ta fito,Mummy Tace Miko min brush da toothpaste Zaki gani Dana ya kawo,Aamna ta duba ta dakko ta kawo komai da Mummy ke bukata ta Kai Mata,duk Abinda Mummy zata Yi tayi ta fito,Aamna taje da sauri ta taimaka Mata ta kwanta saman bed,a Haka ta samu tayi sallolin da ake binta tayi Addua sosai,Aamna Tace Abinci fa Hajiya?Mummy Tace bani pounded yam din na Dan ci,Amma ta dakko ta zuba a plate tare da cokali ta Bude Hanta da kaza tare da tsire duk a Gaban Mummy,Fruits ma ta yanka sannan ta hada Mata tea me kauri ta zauna tare da sa Mummy a gaba kamar ta samu Yaron yaye,Tace yawwa mashaallah Bismillah ta yanko sakwara da Miya Tace to Hajiya ayi hankali gashi Naga gefen bakinki kin danji rauni tana ta Bata a Baki sunyi Shuru kamar ba kowa,Mummy tana ta ci Tace Baki magana ne? Me zance Mummy sai dai idan tatsuniya Zan miki,Mummy Tace sai kace wata yarinya bana so,Sai da Mummy taci da yawa sannan Tace na koshi,Aamna Tace to Naman fa? Ta Furta tare da ballo cinyar kaza ta mikawa Mummy.

Mummy Tace Alhmdllh na koshi,Aamna ta zaro Ido Tace Kazar Hajiya?kaza ce fa,Mummy ta girgiza Kai Alamar Bata ci,Aamna Tace inda ake arziki ba a tsiya Ni Bari na aikata,Nan Aamna taci Kazar Nan ta gaji ta ajiye sauran,taci tsiren taci duk sauran,Mummy kuwa kankana ta Sha taci Banana da Red Apple,Aamna Kam yau harka ta samu sai da taji zata yiwa kanta Illa sannan ta hakura,ta Mike kenan Tace Bari na wanke Hannu da kwanikan tana juyowa gabanta ya yanke yayi muguwar Faduwa ganin Ahmad a tsaye a jikin Kofa da Alama ya Dade a wajen,Fuskarsa ba kwayar Rahma a ciki,Idonta ta dauke a Kansa ta rabe ta gefensa zata wuce wani kamshi Wanda ba irin na dazu ba ya daki Hancinta sai da ta lumshe ido ba tare da ta shirya ba Haka ta wuce da sauri tayi waje,sai da ta wanke komai sannan ta dawo da su ciki ta Adana a tsaftace ta Iske Mummy da Ahmad suna magana da,Mummy tana ta Masa fada ya Bata Rai yayi Shuru,Aamna tana dawowa Mummy ta bar zancen,ita kuwa Aamna saman gadon da ba kowa ta kwanta tare da dakko Wayarta wacce take Ringing tana bukatar a kawo Mata dauki.

Ganin kanwarta Zuhra ta daga da sauri,Tace Amarya bakya laifi,Zuhra ta zuba murmushi tana kwance jikin Angonta Adam tace nayi missing naki sis yau naji ban Iya bacci sai naji muryarki,Wallahi Aunty Amy Aure Niima ne,sai yanzu nasan Ni mutum ce Ashe a baya gunki ce Kawai,da ace nasan Haka ne da bazan Dade Haka ba zanyi Aure,Aamna Tace to me yasa bakiyi ba Ana Haihuwar ki ba,ai sai kiyi tun kina jaririya,Ke Aunty Aamna ke fa adawa kike da Aure,ki daina min sharri wa zai ki Aure? Kawai Ni abinda nafi so a aure shine na ganni Ina fasa kwai a kitchen Zan soya Ina kwas kwas a kitchen,Dariya Zuhra take yiwa Yayarta Kamar me,Aamna Tace ban San Iskanci Dan na fada Miki Buri na a Aure shine kike wani dariya,To Ni ba abinda nake so a aure face in cakare da kwalliya Ina kitchen Ina fasa kwai,Mummy tana bacci Ahmad Yana jinsu Amma wayarsa Kawai yake dannawa,Zuhra Tace Aunty to babbar Harkar fa ta soyewa? Aamna Baki ta tabe tare da Furta Dan tani a yanke shege na kowa a duniya a jefar,Ahmad Yana jinsu wannan Maganar Bai Gane me suke nufi ba.

Zuhra Tace Aunty Amy  Allah ya Baki kema Kalar da kike so Wanda zai biya sadakinki da shegen tsada,Aamna Tace ke na rage tsada na zaftare farashi na yanda su Baba suka damu Ina Ni Ina zaben Yawan Sadaki,Adam ne ya kwace wayar dake Hannun Zuhra tare da Furta sai da safe Aunty kitt ya kashe wayar Baki daya sannan ya ja Amaryarsa Suka kwanta ita kuwa Aamna kwanciya tayi itama tana latsa Wayarta gashi ta kasa bacci sabo da Ahmad Yana ciki Ta kasa kwanciya bare tayi bacci,Bacci ne ya dameta Haka ta kwanta tare da rufe jikinta da katon Hijab Nan take bacci yayi gaba da ita sai Ahmad shi Daya baiyi bacci ba,sai wurin 2am sannan ya bar Asibitin ba tare da kowa ya sani ba.

Washe gari da Asuba Mummy ta farka da karfi a jikinta sosai kamar ba ita ba,Kawai rauni ne da Bai warke ba Amma jikinta fes taji,Da kanta ta lallaba taje Bayi gaba Daya kyankyamin Asibitin take Yi shi yasa ta kasa wanka,Sallah tayi itama Aamna Haka Bayan sunyi Brush da komai suna Azhkar Sai da suka Gama sannan Mummy Tace Aamna kike ko? Aamna Tace ae Tace Yau Zan sa a sallame Ni naji sauki Zan iya karasawa a gida tunda Ina da masu Aiki masu kula da Ni,Aamna tana murmushi tace mashaallah Alhmdllh Haka ake so Allah Kara Ify,Ameen Mummy ta furta,Biro da takarda Mummy ta mikawa Aamna Tace rubuta min Address dinki full sai accnt number dinki,Aamna ta karba ta rubuta komai,Nan take Mummy ta kunna Wayarta tayiwa Aamna transfer na dubu Hamsim,Farin ciki ya lullube Amy Tace Hajiya naji kararrawa na gode Allah ya Kara budi,Ameen Mummy ta Furta tare da mikawa Aamna katinta gashi ko Watarana Zaki neme Ni,Aamna ta karbe jiki na rawa.

suna Haka sai ga Ahmad ya shigo cikin jallabiya fara Kar ta kirki,yayi mugun kyau,Nan take Aamna ta bishi da kallo a ranta Tace wannan Dangin Larabawa ne gaskiya,ko kallon Inda Aamna take baiyi ba ya koma wajen Mummy dinsa suka gaisa Yana ta murna taji sauki,Itama Aamna Bata kula shi ba ko gaisuwa,Kayan breakfast lafiyayye ya musu take Away Suka ci tare da godiya ga Allah,Wasa Wasa Mummy ba a sallame ta ba sai 4pm,Aamna tana gani Wata galleliyar mota tazo tare da tafiya da Mummy,Suka Yi Sallama Aamna ta shiga Napep sai gida,ta samu yan kudinta Bata da matsala abinta.

Bayan Aamna ta dawo gaba Daya kayan da taje asibiti da su har na jikinta ta cire ta wanke fes tayi wanka dama a koshe take,Zama tayi a gefen Mama,Lokacin Baba ya fito daga daki yace yanzu Zuhra tana can a dakin mijinta tana zamanta Ify Abinta,abin kunya Yaya Guda Bata da ko saurayi ko me Gadi babu Wanda ke zuwa zance,Mama Tace an Rubuta Hatimin Annabi Yusufa har an gaji Shuru kake ji sai Neman kudi,Iskanci ne Kawai da samun waje shi yasa Taki fitar da mijin,laifinta ne cewar Mama Kuma kudinki kwandala mun daina karba kije da abinki,Aamna tayi Shuru har Suka Gama ta Mike tayi waje zuwa Kofar gida a kasa ta samu ta zauna dirshan tare da kurma Ihu iya karfinta tana wayyooooo.....Allah.....na shiga Uku na lalace.....Ina samari suke ko Dattawa ku fito ku Aure Ni,Dan Allah gani sadaka ga me bukata,,Ko me tallan rake ko Shoe shiner ko me Gadi,me Mata uku ma yazo Zan Shiga a ta hudu.

Wasu ma tunaninsu tabin kwakwalwa ne ya kamata,sai Dariya akeyi Amma Aamna ko a

jikinta,sai da taji Rana ta ishe ta sannan ta koma gida,tana Shiga Baba ya rike ta ram tare da zaro katuwar Sanda ya samu Aamna Kamar Allah ya Aiko shi ya shiga jibgarta kamar zai kashe ta,Mama tana Kara Mata Yar Iska mu Zaki kunyata a Unguwa,Ihu Aamna takeyi ga Yan hayar gidan ba kowa,Karshe ta tashi da kyar ba Mayafi  jikinta duk kulun Sanda ne ko Ina da gudu tayi waje tana ihu,Baba baya gudun Abin kunya Kawai ya bita a million Suka zuba tsere layinsu rigarsa tana tashi Kamar mahaukaci Ana ta kallon ikon Allah,har saman Titi suna falfala gudu Baba Yana na koreki a gidana karki dawo daga Nan kiyi gaba,Aamna tana gudun masifa tana cewa wallahi sai na dawo me yasa aka haife ni,Ni Nace ku haife Ni Ina ruwana,Suna Haka zugar machininan su Ahmad Suka taho gaba Daya Suma sun kure wuta,Ganin Baba da Aamna suna falla gudu,Dariya ta kwacewa su Mashkoor, a wajen Suka ci birki,Ahmad ne ya bi Aamna da machine tare da sa hannunsa me laushi ya cafko Hannunta da karfi ya daga ta Kamar ya dauki tsinke ya cilla ta a bayan machine ta zauna daram,tana Jin dadi har da godiya Amma sai taga Ahmad yayi reverse ya juya da ita wajen Baba,Ta saki Ihu shi kuwa Baba zuciyarsa Dake tafarfasa yace Alhmdllh ya tsaya cak,a gabansa Ahmad ya Zana wani shegen kwabo da machine yaci birki sannan Aamna ta dire zata gudu Ahmad da shishigi ya samu ya yarfawa Aamna Mari ji kake gauuuu.....Nan take fuskarta ta kumbura ta zube a wajen kuwa,Baba yace na gode Dan Albarka,Ahmad ya kalli Baba da tsageranci yace Gata Nan Yi Mata dukan tsiya Ina Nan ba inda zata je,ko Kuma Ni yanzu nayi maka maganinta,Baba ya saki Baki yace Kai Malam Taya zaka marar min yata, Mace Budurwa ka mareta kalli yanda ka kumbura Mata Fuska,baka da hankali ne? Wata Mahaukaciyar Tsawa Ahmad ya yiwa Ba ba,Hey....tsoho,da sauri Baba ya rufe Baki jikinsa na mazari.

Da yatsa Ahmad ya nuna Baba yace Kai tsoho baka Sanni ba Zan sa yarana su babbalaka,Baba yayi Mukus,Su Mashkoor suka saki Ihu da sowa,Kallon Aamna Ahmad yayi tana kuka,Tsawa ya buga Mata Dan Uwarki Ina Mayafinki? Irinku ne kuke sawa Ana yiwa Yara fyade a kasar nan,Dan uban Babanki Ina Mayafinki eyeeee yayi kanta da hargowa,Aamna ta Mike tsaye tana kuka Tace baka Gane Ni bane nice fa wacce nayi jinyar mahaifiyarka,wani dariyar hauka yayi yace ke dalla Ware so what Dan kinyi jinya,kyauta kikayi? Bar Nan wajen ko yanzu na Tara Miki gajiya,Aamna Tace wallahi sai dai mu Tarawa juna gajiya,Kai Malam Nifa ba ruwana muyi kokawa ba komai bane,baka Isa kaci min mutunci da Mahaifi na ba,sai mu Buda Nima fa Yar Tasha ce,tashancin Nan na Iya shi ta Furta tana dukan kirjinta,Tace baka San har yankan Aljihu nayi ba a kasuwa,su Mashkoor suka hangame Baki,Suka ga Kuma Ahmad Bai sa sun Mata duka ba,Jibson da Maganar Yan kwaya yace King kana fa jinta kana kallonta ka bamu Dama mu sassarata.

Mutane tunda suka ga su Ahmad babu Wanda yayi gigin zuwa kallo Dan sun San halinsu,Baba ne ya cire Rigarsa daga shi sai wando dogo da Singlet ya mikawa Aamna yace lulluba mu tafi gida,Aamna Tace Ni a Haka Zan koma ba Kaine ka kwance min zani a kasuwa ba,ka biyo Ni Muna ta tsere Ana kallo duk da dama ai mun Saba,Baba zuciyarka bata da control Wai? Baba yace ai kece Aamna Yar Iska ce,kiyi aure kinki Ni fa duk na washe ki ma wallahi,shekara ashirin da Hudu zuwa da biyar ba ko saurayi,25yrs shine girma tsoho? Mashkoor ya tambaya,Baba yace ae ,to Jibson Yana tangadi yace to ke kiyi auren Mana,Aamna sai da tayi Dariya yanda ya fada da muryar maye,Baba yace ai Bata iya magana ba,Bata waye

ba,kwana Nan Muka dawo birni,shekarar mu hudu kenan a birni,sai cin mutuncin samari takeyi na rasa yanda zanyi da ita tafi karfi na,Ahmad yayi Murmushi tare da da shafa gemunsa Yana wani rangaji ya furta Tsoho Bari na kaji idan tayi laifi Kawai ka kirani ka fada min har gida zanzo na kera maka ita,Baba yace na gode Dama ta ishe ni,ta gagareni,Aamna mamaki ya kamata,Tsawar data razana ta taji ance yafa rigar tsoho,jiki na Bari ta karba tare da yin Mayafi da ita,Tace wallahi sai na Rama Nima na iya tashancin,Baba yace kuce Mata ta taho mu tafi gida,da yatsa Ahmad ya nuna Mata Hanya ta juya salin alin tabi Baba suka tafi.

Su Aamna suna tafiya wata Budurwa ta taho da gudu wajen Ahmad Tace Dan Allah kaga wani can Haka Kawai ya dameni da naci sai Maganar Batsa yake min nace bana sonsa yaki hakura Wai sai na bashi kaina ko yayi min fyade Dan yaga Kawai Ina tallan gyada tunaninsa Yar Iska ce Ni ta karasa da kuka,Ahmad Fuska a Murtuke yace Yana Ina guy din? Da yatsa ta nuna musu,Ahmad yace Boys kuje ku min maganinsa,ai kuwa Suka tafi Kamar an Aiko su Suka hau jibgarsa,sai da suka Masa ligi ligi sannan Ahmad ya karasa wajen tare da yarinyar,yace Kai Dan uwarka wannan kake so?Kai Dan Iska ne?zaka lalata Yar wasu Tace Bata sonka dole ne? Matashi Yana Nishi jikinsa duk jini Ahmad yace daga yau idan kaga wannan yarinyar hanyar da take idan kabi wallahi sai na yankaka,Matashin yace bazan sake ba,Zan gyara halayena,ayi Hakuri Oga,Ahmad ya Shure shi da kafa yace bace a Nan,ya tashi ya fece da gudu,Yace wa Yarinyar ki dinga saka Hijab idan Zaki talla,Tace to na gode yanlabai,ki daina talla ki Shiga makaranta ko kiyi aure,Tace to ai an kusa biki na Kuma Ina Islamuyya yace Good Ware ke ban son surutu,da sauri ta tafi tana murna.

Tafiya sukayi sunyi nisa Suka samu wani yaro ya fisge Wayar wani a Hanya,Ashe Ahmad yaga abinda Yaron yayi ya arce,Sai da ya Bari Yaron yasha kwana sannan yabi bayansa,ya sauka a machine ya cafke Yaron a nutse ya dinga kashe Yaron da Mari yafi a irga tun Yana gani sai da Yaron ya sume,Wayar da Yaron ya fisge Ahmad ya karba tare da kwarawa Yaron ruwa ya farfado yace Kai barawo ko Nan take ya Kira police Suka Yi gaba da Yaron shi Kuma ya maidawa Babban mutumin da aka satar Masa,mutumin ya dinga godiya,yace yaro daga an kirani na dakko waya Kawai naji ya fisge,Ahmad Bai kulashi ba ya wuce gidansa Kawai su Mashkoor suka rufa Masa baya.

Tunda suke tafiya Aamna kuka takeyi jikinta duk rauni,Baba yace kece dai kika jawo Kuma kin San Halina wallahi Sai in Miki jina jina,Aamna taci gaba da kukanta tana tafiya,Baba yace Jeki ki Siyo kayan Miya da Salat ki Shiga da shi gida,Aamna Tace bani kudin tana kuka,yace a aljihunki Ni Ina da kudi ne an fada Miki,Nima yau bazan ciyar da kowa ba wallahi tunda aka Dake Ni ta furta tana shesheka,Zan tsine Miki wallahi Aamna Naga kin rainani,Aamna tayi banza da mahaifinta,kwafa Yaja ya juya ya tafiyarsa inda zai je yace yunwa ta kashe ku, Zaki sani Zan dawo gidan ne,Aamna tayi tafiyarta da rigarta a kanta har Gaban me kayan miyar kusa da gidansu tana goge Hawaye tana sheshekar kuka Tace Dan...tala....Dantala... ba....bani kayan Miya na dari hudu.....Salat na na ... Naira dariiiiiiiiiiiii......sai ta karasa da sakin Kuka me karfi a Gaban Dantala,Dantala ya saba da halin Aamna yasan Kuma yanda dama suke fada da Babanta,Yace kiyi Hakuri,ita rayuwa ko da wa zaka zauna sai kayi Hakuri Aamna,da girmanki da shekarunki haba Haba,Aamna ta sake fashewa da kuka Tace Wal....wallahi....wallahi tallahi

yau bazan ci abinci ba da yunwa Zan kwana,Kuma na rantse bazan Taya Mama Aiki ba,Dantala Ina da zuciya,Kawai duk an bi an tsaneni akan ban samu Miji ba,a kauyen mu kowa sai ya fada min bakar magana bana Iya Shiga cikin dangi na sakata na Wala,Haka a gida ace Iyaye sun tsaneka,Dantala yayi Dariya yace sai hakuri Aamna,Tace wallahi Watarana za a ga na mutu a tsinci gawata Kawai,kiyi Hakuri cewar Dan tala ya zuba Mata kayan Miya ta bashi kudin ta tafi gida.

Tana yin Sallama Mama ko kallonta Bata Yi ba,kayan miyar ta Ajiye zata juya Mama ta rike Hannunta caraf,Tace wa kike wa raini Wai? Waye sa'anki a gidan Nan Dan Kan uwarki,Aamna tayi Mukus Mama ta shiga zuba Mata Rankwashi ba adadi sannan ta saketa Tace tashi ko na nayi ball da ke, Aamna ta Mike ta fada daki tare da sake fashewa da kuka,Ita kuwa Mama girkinta ta shirya shinkafa da Miya da salat.

Wato Islamiyyar Asabar da lahadin ma kin daina zuwa ko Aamna cewar Mama,Aamna Dake kwance a katifa ta fito Fuska a kumbure Tace na girmi Islamiyya Ni,Duk abinda ya kamata na sani na sani na addini sabo da Haka zanci gaba da saurarar wa'azi Kawai a gidan Radio ya isheni zaman duniya,a kyale Ni inji da matsalata,Ni yanzu ba karatu ne a gaba na ba,Alhadisissani,salisu duk na Iya ya ishe Ni,Sira da Ishmawi na haddace quarter,Zikiri na iya,Qurani saura Izu goma nayi sauka to me Kuma zanyi,gishirin zaman duniya na sani ya ishe Ni,Mama ta rike Baki Tace tab ke Baki ji kunya ba 25yrs Baki sauka ba,to ai da a sauke ba a Aiki da shi gwara ka samu Izu goma kayi Aiki da shi,Bulala Mama ta dakko Aamna ta jawo kujera ta zauna daram Tace a tafke Ni ai na Saba,kamata kullum a Duke Ni to a Dake Ni,Mama kuwa itama akwai zuciya Nan ta dinga tsulawa Aamna Bulala iya karfinta,har ta Gama Aamna ko motsi Bata Yi ba ta tashi a nutse ta shige dakinta,Haka Baba da dare bala'i yakeyi Kamar me,Ita kuwa Aamna washe gari sai da taje chemist aka Bata magunguna,tana dawowa ta Hado kayan sawarta a Akwati ta fito sanye da Hijab Tace Zan bar muku gidanku gwara na shiga duniya.

Baba ko a jikinsa yace a gaisar da Yan bariki maza Kar dare yayi a dawo lafiya,Mama ta tabe Baki Tace sakarai,Aamna tana ta jira a lallashe ta ko ace Kar ta tafi Amma taji Shuru,Tace Zan tafi fa bazan dawo ba,Baba yace to,Duniya fa Zan shiga Mama,Mama Tace madalla,Juyawa Aamna tayi ta fara tafiya ba Wanda ya kulata har taje bakin kofa,Tace baza ku kirani ba Wai? Tsaki Baba ya ja,Aamna tayi waje kenan taga wata dalleliyar mota me tsada,Wata Dattijuwa ce ta fito a motar,da wani Dattijo shima fari ya fito,Aamna taji an kirata,Matar ta kalla sai taga Mummyn Ahmad ce cikin shiga ta Alfarma,Aamna fara'arta ta karu har kasa ta zube tare da Gaida su,Mummy Tace ga Baban Ahmad,Aamna ta sake Gaida shi tare da rike Hannun Mummy Suka Shiga gidan.

Baba da Mama sunga masu kudi Nan Suka rude,Baba yace laaaaaa Alhaji Ja'afar Kaine a gidan Nawa? Wanda aka Kira da Alhaji Ja'afar yace ikon Allah Malam Hussaini Umar dama a Nan kake yanzu? Baba yace ae wallahi,me ya kawo ku?Aamna dai da Mummy suna mamaki aka shimfida musu Tabarma,Aamna ta kawo musu pure water da lemo,Nan ta ebo musu shinkafa da Miya da salat ta Ajiye,Tace Baba kasan su ne? Baba yace kwarai kuwa zauna kiji labari.

Labari

AsmaBaffa
10/26/21, 8:51 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA🌵🌵

16-20

FREE PAGE

DUNIYA TA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

NA KUDI NE

GA MASU BUKATAR SHIGA GROUP DARI BIYU 200 NE

ACCOUNT NUMBER TA
0175487861
ASMAU GARBA MUHAMMAD
GTBANK

MASU TURA KATIN MTN KO VTU GA NUMBER
08033933642

'YAN NIGER KU NEMI WANNAN NUMBER
+227 90 79 59 39

Official

By

AsmaBaffa

Page naku ne

MAMAN SAMHA
ZAINAB SABO
BK
UMMEEN SADEEQ
BASMAM GLAM
ALHUSNA(MRS IDRIS)

Ni Hussaini Umar kamar yanda kika sani mu Uku Mahaifiyar Hajiya Maryam ta haifa,Kuma mu kadai ne a wajen Mahaifinmu Malam Umaru,Ni Yan biyu aka haife mu Ni Hussaini da Hassan,Hassan tun Muna jarirai Allah ya Masa Rasuwa sai Ni,daga Ni aka Haifo Kawunki Isma'il sai Kanwar mu Kursum wacce kika Sani a kauyenmu Sokoto take aure,Munyi karatun Muhammadiyya har muka girma Noma da kiwo muka gado, tun baya dama mu Bamu taso a cikin kudi ba sai rufin asiri,sai da muka girma lokacin aka hadani aure da Aishatu Yar Uwa ce itama auren zumunci ne,daga Nan Bamu samu Haihuwa ba har Ismail yayi Aure shima a can kauye,sai da ya haifi Yara uku sannan aka yiwa Kursum Aure a kauyenmu itama ta Haihu Daya,duk Ni Allah Bai bani Haihuwa ba har Iyayenmu Suka rasu sai Yan Uwa da dangi,wannan da kike gani Shine Alhaji Ja'afar Wanda shima a Sokoto na sanshi Amma Asalinsu Yan Yemen ne kasashen Larabawa,kasuwanci ya kawo su Nigeria Sokoto suna da company Wanda a lokacin suna da Company na Yogourt da Kuma kamfanin Dake sarrafa Fulawa,sabo da Haka suna bi kauyuka suna siyen madarar shanu da Alkama Wanda a lokacin sana'ar mu kenan a wajen mu suke siya,mun Saba sosai muna mutunci da Alhaji Ja'afar lokacin ya Dade da Auren

Mummy har da yaronsu Ahmad Yana shekara bakwai lokacin,su dama masu kudi ne da danginsu duk suna zuwa,ita Mum Yar Sokoto ce,bafulatana ce ya ganta ya aure ta sabo da sonta da yake Yi,Tun Bai Jin hausa har ya koya ya Zama Kamar bahaushe shima ga matarsa bahausa,Tunda yayi Aure ya dawo Nigeria gaba Daya da Zama Amma yanayin Lagos ya fiye Masa Dadi shi yasa yayi gida a can komai nasu a can,Ni Kuma mun Saba mun Shaku,Ja'afar yana tausaya min rashin haihuwa,lokacin akwai wata Yar Uwarsa Hajiya Sumayya,Sumayya marainiya ce gaba da baya sai Dangi Su Ja'afar kenan, Danginsa ce Amma Iyayenta sun rasu,a cikin Dangin Summayya Ja'afar shi ya taho da ita Nigeria ta Dan zauna a Wajensa na Dan watanni, a Nan ta samu wani Wanda shi a Nan Nigeria yake shima Kuma a Sokoto Amma shima asalinsa Dan Sudan ne,ganin balarabiya fara sai ya zauce sabo shi Yana da duhu ma bakin Balarabe ne,aka hada su Aure da Sumayya,Dan Sudan dai yayi Aure Bayan shekara Uku Sumayya ta Haifi Yarta mace kyakyawar gaske aka sa mata suna Aamna,Idan baza ki manta ba Aamna Ina zuwa dake wani gidan Yan Sudan a Cikin garin Sokoto birni,duk Hutu Ina kaiki wajen wasu Dattijai,Aamna Tace ae,Baba yace to kakanninki ne na wajen Uba Aamna,Wannan Ja'afar da kike gani Shine Dangin mahaifiyarki Sumayya wacce ta Dade da rasuwa,Katsam Bayan ta haife ki da shekara Biyu Babanki Rahil menk ya gudu ya bar kasar,aka Neme shi aka rasa,sabo da taurin Kaine da shi,bashi da tausayi, Jaafar ya Shiga Bincike

Ashe karya yayi ya auri Sumayya matansa Uku a Sudan da yaransa manya,Ashe Auren sha'awa yayi ya gudu ya barta,lokacin Jaafar ya bani Amana Kan na kula da Sumayya,Muna Haka ciwon Hawan jini ya kamata daga Nan sai ta kamu da ciwon sugar Bata Dade ba sai ta rasu,Ja'afar yayi kuka dangi suka zo suka tafi da gawar mamanki aka binne ta a can kasar su,ke Kuma kina Yar shekara Biyu Ja'afar yace tunda bani da Yara Allah Bai bani ba Kawai na dauke ki ya bani ke halak na kula da ke.

Ni da Aishatu munyi murna muka dinga kula dake sosai sabo da Alkawarin Dana dauka shi yasa kika ga na barki kinyi har HND na dage na biya Miki sabo da bana so kiyi kukan Rashi,sannan takurar Aure da kika ga mun dage sai mun Aurar dake muna gudun kar wata masifar ta afka Miki ya Zama kin lalace a Hannun mu,shi yasa muke so mu rabu lafiya,Aamna Hawaye ya shararo Mata Tace Amma Baba ita Zuhra fa Kuma me yasa kuka fifita a kaina? Baba yace Zuhra Bayan kin shekara Hudu a Hannun mu Allah ya bawa matata ciki ta Haifo min Zuhra,kin San zuciya da Kuma son Kai da son da na daban ne,wallahi bazan boye Miki ba,muna haifar Zuhra gaba Daya Muka ji tafi shiga ranmu,a Haka ma kokari mukeyi muna danne zuciyarmu Dan kar ace kin lalace a Hannun mu Amma har ga Allah Aamna munfi son Zuhra da ke,shi yasa Baba Ni ka Bari nayi school Wato na lalace ita Zuhra iya secondary tayi aure,sannan har Sweety Zuhra kake ce Mata fa.

Mama Tace ae ai munyi kokari ma duk abinda kike Mana ke rike kin ma ai munyi kokari bazan ji tsoron ki ba,Aamna Tace tunda na taso nasan Kuna duka na ku hantare Ni Ashe duk fakewa kukeyi da naki aure Ashe dama tsana ce?Mama Tace ke dalla fitsararriya lokacin da Danginki suka Yi watsi da ke shi Kansa Alhaji Ja'afar din gashi Nan ya sake zuwa ko duba ki,in Banda Dangin Babanki da muke kaiki kaf Dangin Uwarki ba Wanda ya sanki domin tunda Ja'afar ya Bamu ke ya tafi sai labari muka samu sun bar kasar ba a San Ina suke ba,sai dai Hana

rantsuwa Muna Jin sunansa a Radio Yana tallafi iri iri a kasar nan.

Alhaji Ja'afar dattijon kirki me Kamala yace Bari Nima nayi magana,lokacin Dana Baku Aamna yarda da aminci tare da tausayawa yasa na Baku ita Amana,ku kanku Kun San Ina da arzikin rike ta,Kuma Dana Baku ita sai Dana Baku makudan kudade Wanda Aamna zatayi karatu har matsayin Degree,Kuma Ni bazan ce ba kuyi kokari ba koma Mene kunyi kokari Kuma mun gode Allah ya saka,Amma Kun San dai Aamna na bada gudunmuwa na kudin daukan nauyinta,Baba yace kwarai muma min Sha wahala da ita,Bata da kunya Bata da tarbiyya gata Nan,Aamna Tace ai tarbiyyar kuce Ni Kuma wallahi Ina da tarbiyya, Haka tunda na taso nayi wayo nasan Kuna nuna banbanci tsakanin Ni da Zuhra,Ni za ayi ta dukana har girma na,Ja'afar ne yayi murmushi yace ya Isa Haka,ke Aamna Har abada Iyayenki ne ban son sakarci,Mummy Tace ikon Allah Ashe Aamna ce Yar Sumayya shi yasa na rasa Ina na santa mashaallah,Ja'afar yace lokacin da Muka Baku Aamna bayan mun koma lagos Arziki na ya bunkasa,daga Nan Kuma Mummy ta Haifo Kanin Ahmad Saddeeq,na tattara Muka koma Colombia da rayuwa,a Nan aka haifar min Auta Humaira Wanda Candy zata Yi kwana Nan,Haka Saddeeq shi nutsatse ne yayi aure da matarsa harda yarsa,Zaman da Muka Yi a Colombia shi ya jawo Babban Dana Ahmad ya lalace da shaye shaye,na rasa yanda zanyi da shi wallahi,mun rasa ya zamuyi ya shiryu,abin ya dame mu,Alhaji Ja'afar ya nisa tare da cewa yaki aure bare yayi wani Aiki Sai dai kashe kudi ya sani Kawai da shaye shaye.

Baba yace tab Ahmad din?Aamna Tace Baba shine fa Wanda ya mare Ni ranar Nan da ka bini Titi zaka Duke Ni ka tuna,Wanda ka karbi number dinsa Wai zai koya min tarbiyya? Baba ya daura hannaye a Kai yace lailahaillallahu wannan kwallon shegen Yaron Dan giya? Ai yayi suna kaf gari an San da zamansu,sai dai Kuma Yana da Dan Hali me kyau ta wani bangaren,Daddy ya kwashe duk abinda Ahmad keyi ya fada musu yace wani abin ma Sai Kun gani da idonku wallahi na rasa yanda zanyi,Ashe Aamna ke kika Yi Jinyar Mummy? Dariya Aamna tayi Tace ae Daddy,Baba yace ja'ira Ashe ma Dan uwanki ne,Baba ya kalli Daddy yace game da matsalar Danka Ahmad Kawai a bashi Auren Yar Uwarsa Aamna a daura musu Aure ku Kai wa shege ita gidansa,Ni Kuma nasan Aamna itama irinsa ce Dan ba mutuncin gareta ba suje can suyi ta fadansu har a samu ko Allah zai shiriyarsu sabo da itama Aamna ba wata ta kirki bace Tace ta daina Zama ta gari,Nan take Daddy yace Kuma fa Haka ne Ahmad Yana bukatar jajirtacciyar mace marar tsoro,Mummy Tace hmm ai Ni Naga Drama a Hospital suka dinga fada da juna ba Wanda ke barin wani idan Haka ta faru zanfi kowa murna,Aamna kuwa Hankalinta ya tashi matuka sabo da tasan ma Ahmad kashe ta Kawai zai yi,Kuka ta saki Tace yanzu Dan shaye shaye za a bani? Sabo da anga Uwata ta mutu ubana ya gudu ya barni shine za a min Haka,Mama Baki Bude Tace Aamna mene Haka? Dan Uwanki ne fa,ai Hannunka baya rubewa ka yanke ya Yar, yo tun yaushe da azaba ta ishi mutum Nawa aka Yi Hannu da kafa mutum da Kansa zai kai Kansa Asibiti yace wayyo Allah Likita yanke min na huta cewar Aamna,Mummy Hannun Aamna ta riko tare da mikewa ta ja Aamna gefe tana Mata magana a kunne cikin Rada,Aamna ta washe Baki Tace to na yarda.

Baba ya tabe Baki yace Alhmdllh Allah ya yanke Mana zaman Yahudanci,Daddy kuwa Dariya yayi kawai sannan yace akwai wani gidana Babba ne Dana Gina a Nan Kaduna ba nisa

da Nan Unguwar Taku na mallaka maka shi halak malak,sannan Zan baka Million Uku ka ja jari,Baba Hanci ya rike kamar mace ya rangada Guda Ayyiririri....,Dariya Aka dinga yi,Ranar dai sai da suka Gama shirya komai Har dangi an Kira a waya cewar Nan da sati Daya za a daurawa Aamna Aure, kowa yayi mamaki,ikon Allah Wato aure idan yazo wani shi kanshi a shekarar Bai San zaiyi auren ba,Aamna dai ko a jikinta sabo da sun Gama shirya sirrinsu da Mummy ba Wanda ya sani,Gidan da aka bawa Baba Suka tafi har furniture an zuba a gidan, flat madaidaici me dauke da part biyu,ko Ina yasha tiles ga flowers da komai,gidan a kalla zaici mota Hudu a ciki iya wurin parking,Aamna da Mama sai Murna,ranar Abba ya bada kudin auren Ahmad dubu dari biyu Suka tafi cike da murna,Zuhra Suka sanarwa komai murna Kamar me Ita kanta Zuhra dama ta Dade da sanin basu da Alaka da Aamna ko a kamanni Aamna da Larabawa take Kama,Ita kuwa Zuhra Ana ganinta anga Yar Mama da Baba,Yan Uwa da abokan azirki Suka dinga zuwa ganin sabon gidan su Baba,Aamna a waya ta Kira Kawarta Siyama ta fada Mata komai,ai Siyama Murna Kamar tayi hauka ga Kuma mamaki Aamna ba Yar su Baba bace Ashe Shuru akayi,Amma duk da Haka Aamna ta Sha Jin zancen a Kauye,idan ta tambayi Mama ko Baba sai suce karyar mutane ce,,Aamna zata ma riga siyama Auren ma Ashe,Washe gari tare da Siyama aka maida kayan su Aamna na bukata sabon gidansu,Faisal saurayinta shine ya dinga jigila da motarsa har Suka tare,Baba Kuwa Ya samu ya fara Harkar Sana'arsa ta siyar da kayan masarufi jari ya samu.

Tunda an San Auren da za ayi ba Wani shiri aka Yi ba,Saura kwana biyu daurin Aure Mummy,Daddy,Mufida matar Saddeeq da Yarta,sai Humaira Auta da Sadeeq Suka taho Kaduna gaba Daya a gidan Ahmad Suka sauka,Yana ta Fushi shi fa an takura Masa da zuwa Masa gida,Bai San Aurensa za ayi ba.

Ranar cikin dare Mummy ta haura sama Bedroom dinsa, Yana kwance Yana latsa wayarsa me tsada ga barasarsa a gefe Yana korawa,Mummy ta kalle shi tare da Zama saman Bed din,Yana ganinta cike da shagwaba ya dawo da Kansa saman cinyarta,Yana kallon Fuskarta Idonsa sai wani lumshewa sukeyi sunji kayan maye,Wata kwaya ya dakko a kasan Pillow ya watsa a cikin kwalabar giyar ya jijjiga,Nan take kwayar ta narke a ciki Yace Mummy Dan Sha kiji Zaki samu nutsuwa yanda na ganki nasan akwai damuwa,Murmushi Mummy tayi Tace please ban son hauka Ahmad,Ni zaka kalla ka Bawa kayan Maye?Dariya yayi yace to Mene ciki Dan kin Dan caake kema,Tsaki ta ja,Tace Magana nake so muyi,Ahmad yace Ina jinki Beautiful Mum,Harara ta watsa Masa Tace gobe ka shirya zamuje gidan Wasu Yan Uwan mu a gaisa,Nazo maka da manyan Kaya su zaka sa muje kaji?Baki ya turo yace kin San dai Ni bana gaisar da mutane,idan so kike kiji kunya Kuma to kije Dani Dan wallahi babu Wanda ya Isa nace Ina kwana ko Ina Yini bani da wannan lokacin,Mum Tace ae naji muje Haka,Yace sannan Kuma zanje da Giyata ne kin San bana Free karki ce ban fada Miki ba.

Mummy ta jinjina Kai Tace Ahmad me yasa baka da tarbiyya da biyayya ne Haka? Ina mahaifiyarka duk abinda kaga dama fada min kakeyi,Baki ya tabe yace kin San dai bana karya gwara na fada Miki gaskiya,Kansa ta zame Dake kwance a cinyarta da sauri ya rike Mum yace please Mum zauna ki Sosa min Kai nayi bacci,sai kayi aure idan Haka kake so ai, Dariyar Yan giya ya shiga Yi ba ji ba gani yace Aure....Tab ai kuwa sai dai a dauki gawar matar,Mummy ta

tsorata Tace Idan Muka daura maka fa Auren da ita sai me? Yace kisa ne hukuncinta,kasheta zanyi,Ni na tsani mata bare wani Aure Dan Allah Jeki Good Night ya furta, Tsaki taja Tace wannan Drugs din da kake Sha sune suke kashe maka sha'awar Mata fa,zaka yiwa kanka Illa,Murmushi yayi yace ai gwara Haka akan nayi Zina,Tsaki ta jasannan tayi ficewarta.

Washe gari da Yamma Mummy ta kulle Ahmad a bedroom ta hanashi fita,Yana ta dukan kofa a bude shi Amma Mum Taki,yace aski zanyi fa yanzu I promise you wallahi Zan biki muje can,Sai lokacin Mummy ta Bude shi ya Sha ya bugu Yana tangadi ya fito ya fice,Machine ya Haye sai wurin Aski,Ai wani gashi Attach ya Siya Red and green yace ayi Masa calaba kitso me kyau,Gefe da gefe an kwashe gashin kadan,daga sama Kuma gashi Nan da yawa,Ai kuwa aka Masa calaba me Dan tsayi Suka zubo a kafada kadan,gemunsa ma Haka aka Masa Yar karamar calaba daga tsakiya da red attach,Kyawun da yayi ba a magana ka rantse daga England ya dawo,Kowa ya kalle shi zai rantse wani mugun arnen bature ne ba musulmi ba,Amma Fadin irin kyan da yayi Bata Baki ne sai dai ba tarbiyya idan an gani,duk inda ya gifta da machine sai Kallonsa akeyi,Mum suna Palo Suka ga ya dawo,Su kansu sunga kyan da yayi Amma Kuma bana Tarbiyya bane,Mummy tasan Halinsa Tace Kayi kyau,yace naga gidan da zamuje kin dauke shi da muhimmanci shi yasa nayi gyara na musamman.

Sadeeq ya tabe Baki yace Amma ba tarbiyya ba,Zan ci Uwarka yayi Kansa Mummy ta rike shi,Mufida Tace Kayi kyau,yace yawwa matar mu,Humaira ma Tace Yaya Allah ya bani Miji me irin kyanka,Hannu ya Mika Mata Suka tafa yace Ameen,Ai Ni Handsome King ne,Daddy ya tabe Baki yace Kai dalla sakarai je ka shirya mu wuce, Ahmad Daddy yayiwa wani kallo ya Haura samansa Yana cewa azo gidan mutum a Dame shi,Gidanka ne Dan Ubanka gida na kace gidanka cewar Daddy shima,Mummy Tace Dan Allah karka jawo ya fasa zuwa ta bi bayan Ahmad tana lallashinsa Kar ya biyewa Daddy.

Toilet ya Shiga tare da banko Kofar kamar zai ballata,Wanka ya sheka ya fito,Mummy tana gefen bed,ya shafa lotion ,Fuska ya Bata yace Mummy Zan cire Towel ki fita,Mummy tayi Dariya Tace to Babban mutum,Sai da ya Gama kalailaitarsa sannan ya kwalawa Mummy Kira,ta shigo da sauri da wata Arniyar farar Shadda me tsadar gaske Gezna,Harda Hula yace ohhhhh.....wannan Zan saka?....na shiga Uku wayyoooo ya Furta Yana zaga dakin kamar zai saka wuta a jikinsa.

Ohhhh Mum....Mummy... Mummy....Mummy yake furtawa Yana zagata a dakin,Tace Ahmad Ni din ko? Fuska ya Bata yace na fasa zuwa akan na saka wannan kayan,Tace Dan Ni fa zaka saka,Ohhhhh.....ya sake furtawa Yana girgiza kafadunsa kamar Yaron yaye, Dariya Mummy tayi tare da fisgo Hannunsa ya zille Yana ta Bata wahala sai da kyar ya tsaya ya saka Boxers Kamar zaiyi Ihu Haka ya saka wandon Shaddar wani dai dai shi cif kamar an gwada dinkin zamani fitted na matasa,Singlet Mummy ta bashi ya saka sannan ya saka Rigar Shaddar me Hannu dogo links cif cif shi,ba karamin Arnen kyau yayi ba,Hula kuwa Mummy sai hakura tayi yace bazai saka ba,Haka ta barshi,tana kallo ya dakko farar sarkar Azurfa ta maza wata Yar siririya karama ya saka,Mummy Tace Kayi kyau kuwa Amma sai dai a hausawa ba tarbiyya bace,Yace Mum ku ai local ne Baku San wanka ba Sam,takalmi fari half shoe ya saka,wayarsa kuma Silver color,Glass Brown and white ya saka,Kowa ya kalli Ahmad yasan ba karya Allah yayi halitta a

Nan,Mummy tana murna ta fesa Masa turaruka ya tsaya a gabanta yace ya kika gani,Babban yatsa ta daga Masa,Murmushi yayi Suka fito,Ai duka su Daddy sakin Baki Suka Yi suna kallon yanda yayi azabar kyau,Daddy farin ciki ya kamashi Allah sarki mahaifa,yace da ace Haka kake Yi duk da dai kitson da sarkar ba tarbiyyar hausawa bace ai da yafi sauki sauki, Sadeeq yace the Handsome King,Humaira Tace wow I'm proud of you Yaya King,Comfirm...Confirm ya Furta Yana wani basarwa yace Ina Mufida? Da sauri ta fito dauke da Yarta sun Sha gayu Suma,yace kinyi kyau matar mu, Sadeeq yace Kanin miji ne ke wannan wasan ba yayan Miji ba,Baki Ahmad ya tabe yace ku kuka San wani Kani da Yaya.

Ko da aka zo shiga mota Ahmad yace Bayan anyi min gorin mota harda kwace motoci na a machine Dina zanzo,Daddy ne ya balbale shi da masifa Kai wanne irin banza ne Wai? Ana gabas kana Yamma dalla je ka shiga waccen motar,Ahmad yace wancan bakar Haba ai sai dai ku ku koma cikin bakar Ni da Mum mu Shiga fara ko na fasa tafiyar wallahi ku baku san wanka ba,Dole Haka Daddy ya kwashe sauran a Daya motar baka Sadeeq ya tuka su,Mummy kuwa suna fara ita da Ahmad sun hakimce a Bayan mota Driver Yaja Suka wuce sai sabon gidan su Aamna.

Aamna kuwa dama Mummy ta sanar musu da zuwansu sabo da Haka ita da Siyama Suka shirya abinci iri iri sannan suka Yi wanka,Aamna ta shirya cikin wata sabuwar bakar Truskysh gown me adon Golden,tayi masifar kyau sai ta fito Kamar wata balarabiya,Baba ma Tasha shaddarsa,Mama tasa Atamfarta maroon,Siyama kuwa an zuba lace dark Green,Mama ce ta ja Aamna Bedroom ta zaro wata laya ta makale Mata a kanta cikin gashinta,Aamna Kamar tayi kuka Tace Mama har yau Kuna wannan shirkar ga ta Rannan a kaina kin hanani cirewa layu har biyu,Mama Tace ke dalla ta farin jini ce,Haka aka sawa Aamna dole ta yafa mayafinta Wanda ta Sha acuci,Wani guru Mama ta sake dakkowa tace lallai sai Aamna ta Daura a Hips dinta, Aamna zata Yi kuka Tace wallahi kin San naci kashinki da fitsari idan na tsine Miki sai ta Kamaki,Zan tsine Miki idan Baki daura ba,Aamna tana gani ta dage Riga har wandon ciki aka daura guru sannan ta maida kayan ta fito palonsu hadadde Kamar zata Yi kuka ta zauna tana Danna Yar Wayarta Vivo.

Suna Haka Suka ji shigowar motoci,Aamna gabanta ya fadi,Siyama kuwa tuni ta leka ta window har Sanda Ahmad ya fito ta haukace gaba Daya tana lallai Aamna wallahi ku Larabawa ne da gaske gashi na gani,kalli danginki Kan uba kaga wani tantirin Dan Iska Amma duk yafi kowa kyau da iya wanka,Aamna ta Mike ta leka itama tace ai shine Angon,Siyama Tace Yau mun Shiga Uku kashinki ya bushe da gani Zaki ci Ubanki,Aamna Idonta ya kawo kwalla Tace wallah bazan taba sonsa ba,Dan giya ne,idan Kuma ya shiryu fa cewar Mama,Aamna Tace Idan ta dalili na ne sai na yarda Ina sonsa idan ya shiryu sai na gudu na barshi Kinga na taimaki Iyayensa,ko Dan Iyayensa Zanyi sabo da yanda suke mutanen kirki masu taimakon musulmai Bai ci ace suna da Dansu irin wannan ba,Siyama Tace bafa a Wasa da so,karki Bari ya kamu da sonki kice Zaki Wasa da zuciyarsa idan ya Gane ba sonsa Zaki ba kin Gama yawo,na Baki shawara idan Zaki so abinki ki soshi karki ce ban fada Miki ba Aamna ba a Wasa da zuciyar mutum a so,Aamna Baki ta tabe Tace wannan Zan so? Zan dai je da yanda Mukayi magana da Mum,ba ruwanku.

Sallama sukayi aka amsa kowa ya shigo a nutse,Baba Yana musu Sannu da zuwa,Nan da Nan Su Siyama suka cika gabansu da Abinci sai lokacin Ahmad ya shigo ya tsaya Yana waya a waje,Ganin Aamna ya bashi mamaki yace Kai keeee......Aamna ma Tace kaiiiii......Ran Ahmad ya baci yace Wai Mum dama gidan wannan zamu wani zo? Daddy yace zauna Malam,Ahmad yace Ni bazan zauna ba Ku Gama mu tafi Ina da abin Yi,Siyama Tace tab a ranta,Zuhra ce ta shigo Amarya taci gayu Adam ya sauke ta,Itama gaisawa akayi ta zauna,Ahmad fafur kin Zama yayi ya zuba Hannu biyu a Aljihu ya tsaya kerere Kuma ba Wanda ya gaisar ko kallon arziki Bai musu ba,Baba shi Kam murna yakeyi Aamna ta samu Miji sai ya kalli Ahmad yace Sannu Sarkin matasa,na baka Sarautar Sarkin matasan Nigeria,Ahmad wani murmushi ya saki ba shiri,Aamna ta wani washe Baki itama ganin irin kyan da yayi,a Haka Daddy ya bada tarihin Aamna da dangantakarsu da Ita,Tsaki Ahmad ya ja tare da zaro Yar karamar kwalabar giyarsa a Aljihu ya kwararawa makoshinsa,Aamna ya kalla ya galla Mata Harara tare da cewa daina kallo na,Tace na kalleka din Kai da wanne idon ka kalleni,ransa ya sake tunzura ya kwada Mata Mari a saitin Idonta Nan take ta durkushe ta saki kuka,Da sauri taro ya watse aka dauki Aamna zuwa Asibiti,shi kuwa Ahmad a waya ya Kira Mashkoor ya dauke shi a machine suka Yi tafiyarsu.

Daddy kamar bakin ciki ya kashe shi ransa ya baci ganin yanda aka mannewa Aamna Ido Daya da auduga da plasta Kuma akace Nan gaba sai an Mata aikin Ido,Tunda suka koma gida Basu ga Ahmad ba har kwana biyu ta cika Wanda itace Ranar daurin Aurensa Bai Sani ba.

Mummy a waya ta Kira Ahmad ta sanar Masa da Aurensa,ya zaci Wasa ne ya dinga dariya yace Mummy kina da abin Dariya to idan hakane a daura Auren na Amince, Mummy tayi Dariya Tace ka yarda kace? Yace Yeah..Yana dariya Wai Wasa ne, Daddy kuwa ya tattara mutanensa Dana Baba a masallacin Unguwar har Mashkoor ya sa aka Nemo su duka sabo da Suma su Zama Shedu,Ahmad Yana can gidan Mashkoor Yana ta sheka bacci, Ranar Juma'a Ana Idar da Sallar Juma'a da Shedu walliyan Amarya da wakilin Ango suka karbi Aure Nan aka Daura Auren Aamna Rahil Menk da Ahmad Ja'afar Yabalash, Kan sadaki dubu dari,Su Mummy lefe suka yiwa Aamna na gaske Akwati goma Sha biyar,Ahmad ranar ya dawo gida sai gani yayi su Baba duk sun Hada kayansu zasu tafi ba Wanda ya kulashi,Mummy ce ta shigo Bayanta Aamna Amarya ce sanye cikin wani material Brown yasha kyau,idon Aamna Daya yasha plasta a manne da Daya take gani,Yana ganin Aamna ya Mike yace me wannan takeyi a Nan Mum?Mummy ta Bata Rai matuka Tace matarka ce Ahmad,Daddy ya shigo yace yau Shedu sun sheda an daura maka Aure da Aamna Yar uwarka Kuma marainiya sannan da Amincewar aka daura, ta Zama Amana a wajenka,ka sani Aure ba Wasa bane,idan kayi shirme Allah bazai Barka ba,Kuma wallahi ka koreta ko ka Mata Illa ban yafe maka ba Ahmad.

Mummy Tace gata Nan wallahi kaji bazan rantse a banza ba babu Wasa yau aka Daura muku Aure shi yasa nace Rannan ka bimu muje na kaika ne Dan kaga surukanka,Nima kaji na rantse Idan ka koreta ko kayi gigin sakinta bani ba Kai ban yafe maka ba,Kuma Matukar ka saketa Allah ya Isa Nono na daka Sha,sabo da Haka gata Nan Amana da kayanta,Nan Ahmad yaga me Gadi Yana ta shigowa da kayan lefe Yana kaiwa sama Daya dakin da ba kowa Wanda Mummy ta zabawa Aamna a matsayin nata,duk abin bukatar Aamna an kawo Mata abinta,daga Nan Mummy Tace Mashkoor ku shigo,Suka shigo suna tangadi,Mummy ta kalle su Tace gwara

da kuka zo yau nasan ku shaida ne a gabanku aka Daura Auren Ahmad sabo da Daddy da Kansa ya gayyace ku Kuma Kun gani,Mashkoor yace kwarai King a gabanmu aka Daura muna ta so mu fada maka Amma wayarka Taki Shiga gaskiya ba a kyauta Mana ba,anci Amanarka King a gabanmu muna gani aka Daura Sadaki dubu Dari Daddy ya bada cewar Jibson.

Bash yace Kuma Daddy yace kayi aure yanzu mu rage zuwar maka gida wannan fa ba Adalci bane King,Ahmad da yayi mutuwar tsaye yace shima cikin kwaya me yasa Baku Hana an daura Auren ba,me yasa Baku rotsewa liman Kansa ba,Daddy ya kawo securities ko Ina King,Ahmad yace Good za aga abinda ba a so kuwa,Mummy Tace kaji dai gargadi Kai ka sani,ta kalli su Mashkoor tace lalatattun banza ku fita muje marasa tarbiyya,Haka Suka fito ransu a bace,Ahmad Yana kwalawa Mummy Kira kizo Mummy ki tafi da Yar mutane,Zan Mata Illa,Zan kashe ta ne,kizo ki tafi da ita,Mum....Mummyyy.....Ahmad ya dafe Kansa kwaya ta motsa Nan ya Shiga hauka da tangal tangal a palon,Aamna tana kallonsa a ranta Tace kaddara ta hau kaina na shiga Uku,me yasa na yarda aka Daura Auren,Wayar Hannunsa ya tarwatsa da kasa,Wandonsa Kamar zai Fado zabar Ass down na iya shege,Ya kalli Aamna yace ke bi Mummy ki tafi kafin na kashe ki yanzu,Aamna Tace wace zata bi Mummy? Ai wallahi Zama daram sai dai mu mutu tare,Zan Miki Illa fa,Illa ai ka rigada kayi min ita tunda ka nakasa Ni ka maida Ni me Ido Daya,waye zai aure Ni a Haka,ai Ina Nan a matarka Zama daram wallahi yaro baka Isa ba kayi kadan Aamna ta Furta da karaji tana dukan Table,yace ke Ni Zaki nunawa hauka,Kai din wa Kai din me,me ka Isa kayi,Ai ransa ya Gama baci ya bita da gudu Suka tafi tare,ta haura Sama da gudu zuwa dakinta tana shiga ya damko gashinta,Tace wallahi ai dambe ne Nima na Iya Suka rukuma kokawa.

Kici kici suna Nishi Kamar zakaru,ya dauketa ya makata a saman Bed,ya bita zai jibgeta ta samu tare da makalkale shi ta cikwikwiye shi,Taki bashi damar dukanta,gata da karfi itama Suka dinga kokawa Baji ba gani,sai da suka gajiyar da kansu sannan ya saketa ya dawo Palo ya zauna a kujera Yana maida numfashi kamar Wanda yayi tsere Itama palon ta dawo gashinta ya watse ta zauna tana Nishi itama taji jiki.

Yana Nishi yace kin gaji kenan?,Tace na gaji a Ina ai ban gaji ba sai dai mu mutu wallahi,yace to Bari na huta na samo power kiga yanda zanyi da ke,Aamna Tace Nima Bari tawa power din ta dawo ka gani idan Zan kyaleka.

AsmaBaffa
10/26/21, 8:51 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA🌵🌵

21-25

FREE PAGE

DUNIYATA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

NA KUDI NE

GA MASU BUKATAR SHIGA GROUP DARI BIYU 200 NE.

ACCOUNT NUMBER TA
0175487861
ASMAU GARBA MUHAMMAD
GTBANK

MASU TURA KATIN MTN KO VTU GA NUMBER
08033933642

'YAN NIGER KU NEMI WANNAN NUMBER
08033933642

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne

BESTYNBEELAT
UMMU LATEEPHA
M BELLO
SA'ADATU TIJJANI
UMMI DEEJAT
NAFEESAT UMAR MUHAMMAD.

Yana Nishi a ransa yace shegiya karfi ne da ita,Aamna kuwa mikewa tayi Tace Bari muje mu gaida Ubangiji wani kuwa sai dai su gaisa da barasa,a fusace ya Mike sai ta zura da gudu tare da fadawa dakinta ta saka key,Yana huci yace Zaki sani wallahi sai dai idan baza ki fito ba Useless kawai,Key din machine dinsa ya dauka tare da ficewa ya bar gidan gaba Daya,Ita kuwa Aamna wanka tayi tare da Gabatar da Sallar Magriba,tana zaune tana Azkhar har lokacin Sallar Isha yayi ta Gabatar sannan ta Mike tare Shiryawa cikin wasu kayan baccinta doguwar Riga ce red me sililin Hannu ta wuce gwiwa sosai ta Mata kyau,Kayanta ta Shiga Shiryawa sai da ta tsara komai fes sannan ta kwanta saman gadonta yunwa kamar zata mutu,Kitchen dole ta fito ta Nema Amma wayam babu ko Lipton a ciki bare wani Abu na dafawa,Kugu ta rike Tace Kan bala'i Bari ya shigo,Zama tayi tana jiransa Aamna Bata San shi sai safiya ko tsakar dare yake shigowa ba,Yana can Yana shaye shayensa.

Bangaren Ahmad kuwa tunda ya fita wajen su Mashkoor ya je Suka zauna Yana cewa Mummy Wai kamata Ni za ayiwa auren dole, aure ban sani ba, Mashkoor da maye Yana karkace Baki yace Mum sunyi fuck up fa,Muguntar Daddy ce Kawai cewar Ahmad,Bash yace karka kyaleta kaci uban Yarinyar ai wallahi zata gani ko mu ka Bawa dama sai munyi maganinta,Ahmad yace Guys the things is Mummy tsinuwa tayi min akanta fa,Yar Iska Wai Dazu Dani zata Yi kokawa,Jibson Yana zuka hayaki yace Eyyyeeee.....hey this girl get heart woooo....but show her you are our king,Sweet Boy just Sample the Beb,Ahmad ya kalle su, su Biyar suna ta korawa ya daga zundumemiyar kwalaba ya kurba yace gata da karfi har Elbow fa tayi min a kirji,La'ilaaaaah....cewar Mashkoor Yana dafe Kai yace aci mamanta Guys,Ahmad cike da Takaici yace Hmmmm me....me...me....Mum tayiwa haka,a bani Auren wata Ina Zan Kai wannan nauyin Kai wallahi ma dole ta karba,she must Collect...am....wayarsa ya zaro ya Shiga Kiran Mummy dinsa,Mummy lokacin tuni suna Lagos ma,ta daga Wayar tace Ya akayi Ango,Kamar zaiyi kuka yace Mummy kizo ki dauke wannan Ajiyar Taki Zan fa Iya kashe ta,Zan kashe ta ne Mum,karfa ki sa nayi mummunan laifi tam,Tsaki Mummy tayi tare da kashe wayar Baki daya.

Mikewa yayi Zumbur yace akan wannan trash din Mummy ta juya min baya,dole naci uban Yarinyar Nan,Zaga wajen ya Shiga yi,Ya dauki kwalabar Giya ya tarwatsa ta,kujerar da yake zaune ya dauka tare da yin jifa da ita,Su Kuma sauran sunyi tagumi kamar an musu mutuwa Wai Ana Taya Oga bacin Rai ne,Ahmad Bai koma gida ba sai 4pm ya shigo a make ya wuce palonsa tare da fadawa saman kujera ya kwanta Nan take bacci me nauyi ya kwashe shi,Ita kuwa Aamna da Yunwarta ta kwanta Haka da Asuba yunwa ce ta tasheta,Bayan tayi Sallah da Azkhar ta koma baccin Yunwa,sai 11am ta sake farkawa,Gidan ta hau gyarawa sai da ta Gama da room dinta da toilet sannan ta shiga dayan ta gyara,ta Shiga Dakinsa Nan taga Haduwar furniture gadon Kawai abin kallo ne, a Nan ta lalace tana kallo,sai da ta gaji ta gyara Masa ko Ina Neat Yana kyalli da sheki,Har Toilet duk ta Gama sannan ta dawo kasa a Nan ta ganshi Yana ta bacci hankali kwance,kitson calabarsa ta kalla ta leka Fuskarsa tana kallon Halittar

Allah Iya Halitta,Tace tab Allah yayi Kira a Nan,waye zaiyi wannan in ba Allah ba,cikin Creazy Jean dinsa fatarsa duk a waje fara Kar da gashi kwantacce luf luf,Aamna Tace Uhmmmm.....sunanka Dan Zarra daga yau,kayi Zarra wallahi kafin a samu me Kama kafarka a kyau sai an tona,Habarta ta tallafe Tace kaga Dan baiwa....Fresh dashi...karya suke wani sweet Boy...ai wannan ya wuce Sweet Boy sai dai Honey Boy,Aamna tana nuna shi da yatsa Tace See Nose Alqur'an,Juyi yayi tare da Sosa Dan wuyansa,Aamna Tace ga Chest lafiyayye,Lips dinsa ta kalla ta Bude Dan bakinta tare da lumshe Ido Tace kiss mukeyi da shi ita kadai ta cuno Baki gaba tana feeling Wai suna kissing,Wani Iri taji a jikinta,Tace Kai da gaske na fara Jin dadin,Tunaninta ta kautar Tace kalli dalla ya wani kwanta da takalmi a kafarsa,a hankali ta tsuguna a kasa tare da zare Masa takalmin kafarsa a hankali ba tare da ya farka ba,Aikinta taci gaba da Yi sai da ko Ina ya dau kyalli da kamshi sannan ta leka waje taga me kula da Compound ya Gama gyara ko Ina na wajen,da Hijab a jikinta ta karasa wajen me Gadi,ya gaisar da ita Tace Musa ya kakeyi da cin Abinci a Nan gidan? Musa yace ai Hajiya duk wata Bayan Oga ya biyani kudin aikina Yana bani kudin Abinci na wata wata safe,Rana Dana dare,ai Hajiya Oga mutum ne me kyauta,Baki ga yanda yake taimakon na kasa ba,abinda nake so shi nake siya naci,ga kyautar kudi akai akai Yana bani,idan zanje ganin Iyali na Sha Tara ta arziki yake min,wayata ma Tekno dubu Arbain da biyar shi ya Siya min sabuwa dal,Aamna Tace yanzu dai kullum siyo abinci kakeyi? Yace me dadi ma kuwa Hajiya,tafiya Aamna tayi yunwa kamar zata kashe ta,Tace Bari ya tashi wallahi dole Nima ya dinga bani kudin Abinci na,Palo ta koma da Idonta Daya a manne ta Iske ya koma Bedroom Yana ta baccinsa,Bai tashi ba sai 2pm lokacin Yayi wanka ya hada Sallar Asuba da Azahar yayi ya shirya cikin jallabiyya ruwan toka,Yana zuba kamshi ya sakko kasa da Niyyar fita,Aamna wacce yunwa ta Gama cinyeta ta Mike da sauri ta kulle Kofar palon tare da sa key ta datse ta jefa key din cikin bra dinta tana kallonsa da masifa Tace wallahi ba inda zaka je sai ka bani kudin Abinci,matarka ce Ni a gidan Mijina nake sabo da Haka hakkinka ne nauyin ka ne ka sauke,Kai ya girgiza yace kina Neman rigima Dani,bana son Wasa da shirme,Ina da aikin Yi bani key Zan wuce Aamna Tace wallahi bazan baka ba sai ka bani kudin Abinci,Kai ya girgiza yace karki Bari kwakwalwata ta dau chaji Zan Miki Illa,Zan Miki Illa ki bude na fita ban son wasa,Aamna Tace wallahi yau baka Isa ba sai ka bani abinci,ka nakasa min Ido sannan zaka kashe Ni da yunwa,yace Mum ce ta kawoki kije wajenta ta Baki ko Ni Nace kizo gidana,bana sonki na tsaneki Akan me Zan Baki kudi na dalla Bude min kofa ya taso da masifa,Aamna ta rike Kugu sanye da Hijab Tace wallahi bazan bude ba,yace look ni bana taba Nonon Mata jikinsu ma bana tabawa ki dakko key ki Bude min kofa kin San Zan iya kwata a cikin Bra din Taki Kawai ban son tabawa ne ya Furta Yana yatsina Fuska,Tace Bazan Bude ba wallahiiii.. ta karasa da kukan wahalar Yunwa.

Sauri yake yi zai fita sai ya koma Sama ya fito da kudi dubu Hamsim Bundle na Yan dari biyar biyar yace gashi Zan Baki badan Ina tsoronki ba badan Kuma tausayinki ba Dan Ina so na fita ne Ina da Abinyi,Kudin ta karba Tace da karka bayar Mana Idan ka Isa,kaji dai tsoro na Yaro woooooo......cikin tsawar data razana ta yace Open the door,Ba shiri jiki na rawa ta zaro key ta Bude Masa ya fice a fusace tare da banko Kofar kamar zai ballata.

Ita kuwa murna da farin ciki ya kamata ta dauki dubu biyu ko wanka Bata Yi ba ta gyara Hijab dinta tayi waje,ko me Gadi Bata aika ba ta fice daga gidan,a Unguwar tana tafiya taga wani

Resturant da sauri ta Shiga ciki tayi Order taje Away na Jullof rice with salat and chicken,ta siyo lemuka harda su Icecrewm Yogourt ta dawo gida ta baje abinta a Palo taci ta koshi tayi dam sannan taje tayi wanka tasa wani gajeren Wandonsa ta zabo fari ya Mata yawa Amma ta saka Haka,ta dauki t-shirt dinsa baka ta saka sun Mata yawa Amma abinka da me kyau sai tayi kyau,Haka ta gyara palon ta Karo karfin Ac tare da kunna kallo tana kallo ta wani can saman Hannun kujera baza ma ta zauna a kujerar ba ta tale kafafu tana Shan Iceream dinta tana ta Dariya a Haka ya shigo gidan ya sameta,Kallo ya bita da shi ganin kayansa a jikinta tana Shan Icecream,Wayar charger ya fisgo da sauri yace kayana are you Mad,Da gudu tayi cikin wani daki ya bita da kyar ta samu ta buya a toilet,yace Zaki fito ne,idan kin Isa kina ji ke kece ki fito,Tace kaima idan ka Isa ka shugo,baka kunya fada da mace,Namiji da Kai kaje kayi da maza Mana idan ka Isa a tumurmusa ka,Yace Zaki fito ne sai na Ballaki Kuma wannan kayan da kika sa wallahi sai dai a kone su ban Haka skin da ke Idiot ya juya tare da komawa palo.

Tunda Aamna tasan tayi laifi Bata sake Fitowa ya ganta ba sai washe gari ta fito sanye cikin wani Lace fari Riga da skert daf da ita tayi kyau sosai Sanda ta shigayi tana tafiya a hankali,a main Palo ta Iske shi yayi Order Breakfast ya hada tea lafiyayyen gaske ga chips and Egg da farfensun kaji Yana ci hankali kwance,Aamna ta hadiyi Yawu ta fito a hankali yaji motsinta Amma ko kallonta baiyi ba yaci gaba da cin abinsa,a gabansa ta durkusa Tace Ina kwana Yaya Ahmad,sai lokacin ya kalle ta kadan Yaja uban Tsaki,tace Nima yunwa nake ji,wata Uwar Harara ya aika mata,Dan Allah San min ko na fita na siyo? Dama jiya na fita na siyo Abinci na manta ban nemi Izninka ba ka yafe min,Cikin tsawa yace Ina ruwana da rayuwarki Ni da Zaki tafi ma bangon duniya Ina ruwana,wallahi bazan je bangon duniya ba salon idan tashin kiyama yazo yajuju da majuju su fara ta kaina,Kinga ki daina Shiga harka ta,na fada Miki kiyi rayuwarki Mummy ce ta kawo ki to duk wahalarki sai ki fada Mata,Yar wahala Kawai,Yar walagigi Kawai,Ai kuwa Ni gaskiya Raina ya biya da wannan Abincin naka ka fada min Inda ka siyo naje na siyo ai Ina da kudi sannan ko ka bani naka na ci,Tana Gama fadin haka ta janyo plate din chips din gabanta ta fara ci Tace Dadi,sai ta dauke plate din ta gudu daki ta sa key,Ahmad ya dura wata Ashirya yace yau ba abinda zai Hana ban karyaki a gidan nan,Sa'anki ne ni? Aamna Tace ae daga bedroom,Sai da ta cinye tas ta fito lokacin ya bar gidan ma,ta kalli kwanikan Daya Bata duk abincin ya rage Bai cinye ba duka,ta zauna gaba Daya ta cinye sannan ta hau gyara gidan tana mita mutum sai yawon jaraba kullum Yana waje.

Duk wani Aikinta sai da ta Gama sannan ta zaro Yar Wayarta Vivo ta Kira Mama suka gaisa da Baba,ta Kira Zuhra ma Suka Sha Hira,Siyama ta Kira karshe,Siyama Tace Amarya bakya laifi kin tafi kin barmu da Aiki a Resturant,Yaya Mutumin naki ko anyi abin ne? Aamna Tace Allah ya kiyaye na hada jiki da Dan giya,ke Siyama wallahi baya kaunar Mace,wannan ko tsirara Zaki zo gabansa baza ki birge shi ba,Dariya Siyama tayi,wallahi Aamna ga masifa kullum Fuskarsa ba Rahma Abu kadan Kuma sai masifa,wannan bazai shiryu ba,banga abinda za a Masa ya shiryu ba,to Ina ma yake Zama da har zai fahimci wani Abu mutumin da sai ya kwana a waje can ko sai cikin tsakiyar dare zai dawo,ga Dan Ido na Guda Daya a manne,Suna ta surutu har suka Gama ta fara karatun Qur'ani,Jin yanda aka banko kofa tasan Ahmad ne ko Sallama dama bayayi Yana shigowa yace ke koma dakinki kiyi karatunki ko ki koma masallaci ki tare,Ganin yanda ya shigo a buge sai ta tashi tsam tayi bedroom shi Kuma ya kwanta a saman

kujera,Ya kunna tv ya kure volume karshe kida ya cika gidan a manyan speakers Yana sani yayi Kuma dole Aamna ta hakura da karatun Qur'anin sabo da yanda kida yake dauke Mata hankali,Fitowa ta sake yi,ai kuwa ya Mike a fusace yace ba nace ki daina matsowa inda nake ba ya dauki Remote ya jefe ta da shi da karfi ji kake kwas a goshinta,sosai taji zafi wajen ya kumbura yayi Mata kulu,Itama ta dauka ta jefa masa a bayansa,ta gudu ya bita cikin zafin nama Amma ta kulle Kofa Haka ya rabu da ita yace Zaki fito ne.

Sai bayan Sallar Isha Aamna ta fito sanye cikin doguwar Riga Yar kasar masar,me shape sosai wata silver,ba karya tayi kyau,Mayafinta tayi Rolling ta dauki kudi ta fito,yau ma tayi sa'a sai ta ganshi a kwance Yana cin green Apple,Aamna cike da tsoro ta karaso inda yake wani kamshi yake na musamman,a gabansa ta tsuguna Tace Sannu da hutawa zanje siyo Abinci,Baki ya tabe sai da ya dauki mintuna yace Ina ruwana,mikewa tayi ganin masifa yake ji kadan yake jira sai tayi tafiyarta kuwa,taje tayi take Away sharp sharp ta dawo,Lokacin Yana Zaune Yana kallon wani American film, Sakwara da miyar kifi, ruwa Eva da fruits salat,tana ci tana kallon Film, .

Wayarta ce ta hau Ringing tana dubawa taga Mama,da sauri ta daga,bayan sun gaisa Mama Tace Aamna ga fa kudin sadakinki Baki karba ba,Aamna Tace Ina sane da abina,suna Rai na,a ciki ki dauki dubu Goma kyauta,ki Bawa Baba dubu Talatin,Zuhra a Bata dubu bakwai,Siyama kawata a Bata dubu Uku Kinga dubu Hamsin ta Kare ko? Mama Tace Haka ne,to dubu Hamsin din a ciri dubu biyar a bayar Sadaka Allah ya Kai ladan kabarin mamata sumayya Allah ya Mata Rahma,a sake cire dubu biyar Abba na Daya gudu ya barni ayi Sadaka nayi tawasili da ita Allah ya shirye shi ya canja Hali,Mama tayi Dariya Tace ai duk kin rabar da kudin ba Haka akeyi ba,Zan dai cire na Bawa kowa abinda ya Dace sauran ai naki ne,Aamna Tace to koma dai mene abinda aka barmin a kaiwa Kawu Isma'il can kauye ya Siya wake da Alkama a ajiye idan sukayi tsada sai na siyar na samu riba,Nan fa Ahmad yace tab Riba kudin riba ai masifa ne, ka siyi Abu ka boye sai yayi tsada kazo ka siyarwa mutane,Wannan ba Business bane,Aamna Tace Kai baka ga laifinka ba barasa kwalaba Nawa kake dirkewa cikinka wlh kayi hankali Kar Hantarka ta tabu tam,Hannu yasa ya murde Mata kunne ta kwalla Kara,Mama ta waya taji Kara Tace Ify? Mama wani kwaro ne ya firgita Ni.

Can Baba ya fisge Wayar yace ke Aamna Dan Ubanki kiwa fa mijinki biyayya,duk abinda yace kiyi bana son sakarci,Kuma ko me Zaki shuka ki shuka gaskiya kiyi gaskiya ato sabo da mu dangwali arziki da kyau,Aamna Tace yo Baba ai Gaskiya Ni a jinjina take da ita aka haife ni,dankwalin Aamna ne ya zame layar ta Guda biyu Dake soke a kanta suka bayyana,Ahmad Yana gani ya girgiza Kai a zuciyarsa yace mashirkiya,Ita dai Aamna abincinta take ci tana Dan juyowa ta kalle shi kadan sabo da faratansa na Hannu Dana kafa Daya Tara sunyi tsayi Kamar Arne Amma da gani suna Shan gyara wani fes da su sai dai ba a Yankewa,Allah yasa kayi bacci sai na yanke wannan uban faratan Aamna ta furta a ranta.

Ganin tana ta Kallonsa Yaja Tsaki tare da mikewa ya dauki key din machine dinsa zai fita,Aamna Tace Ina zaka je da daren Nan Haka?Ni tsoro nake ji gaskiya,Kwafa Yaja a ransa ya furta Mummy ta Gama Dani,idan na Mata Illa tsinuwa ta hau kaina,juyowa yayi a fusace yace

Allah ya taimakeki Ina son Nonon Mummy Dana yasha yabi lafiyar jikina Amma da kin Gane kurenki,Aamna ta kyalkyale da Dariya Tace au har yanzu Nonon Mummy Bai Gama bi maka jiki ba? Sanda aka haife Ni ko yaye Ni ba ayi ba aka samu cikin Saddeeq shi yasa ya cuce Ni na Sha gubar cikinsa,Aamna sake kecewa da dariya Tace ko shi yasa aka ce ka Dade a tsumbure baka girma ba Dan Mummy Tace har cutar koshokwo kayi Haka Kawai Aamna tayi karya Tace Mummy ce ta fada Mata,ai kuwa shi da saurin Fushi kwaya tana sashi saurin Fushi ai Kan Aamna ta rufe baki yace uwar Koshokwo nayi,Aamna ta Mike zata gudu Suka dinga zaga palon Nan sai ya kamata ya dake ta Itama ta guduwa,ta samu tayi waje Compound da gudu,fita yayi Yana huci ya hau lifan dinsa ya fice sannan Aamna ta dawo ciki abinta.

Bayan Sati biyu da Auren Aamna kullum fada sukeyi da Ahmad ba Wani mutunci, Mummy ce ta Kira Aamna Tace,bayan sun gaisa Aamna ta saki kuka Tace Mummy wallahi kullum sai munyi fada ya Duke Ni saurin duka ne da shi Kuma yaki siyo kayan abinci kullum sai dai naje na siyo ko na aiki me Gadi shima Haka Mummy, Dariya Mummy tayi Tace Kuma wallahi Ahmad ya Iya girki sosai a haka,kin San nice na sallami Peter me dafa Masa abinci, Aamna ki Kara Hakuri,bazan turo Miki kudin Abinci ba Yana da kudi,kece Zaki San yanda zakiyi Masa dole ya Baki kudi ki zuba abinci a store kin Gane,ae naji to ta furtawa Mummy,Bayan sun Gama Wayar Aamna ta zauna tayi tagumi tana saka Taya zata sa ya siyo Mata kayan abinci ko ya bada kudin ta siyo tunda kudin hannunta sun kusa karewa.

Bayan tayi Shirin bacci cikin wata Riga da wando farare masu laushi ta zuba kyau ciki,a Palo ta zauna tana jiransa ai kuwa taci sa'a yau Ana Sallar Isha ya shigo gidan Yana tafiya da kyar da yanda yake Gadara ya nuna yau baiyi shaye shaye da yawa ba,Sannu da zuwa Aamna ta Furta,ko kulata baiyi ba Direct sama ya haura ya fada toilet,wanka yayi ya fito tare da Gabatar da Sallar Isha ko Addua baiyi ba ya Mike ya saka wasu kayan bacci dark blue me digon fari Riga da wando,fresh milk ya sha sannan ya kwanta a Gadonsa Nan take bacci ya kwashe shi me nauyi,Aamna ta biyo shi dakinsa Wanda Bata shiga sai idan zata gyara,a hankali tayi knocking Shuru taji,tayi Sallama Shuru,sai ta bude Kofar a hankali saman bed ta hangoshi ya wani Yi dai dai Yana baccinsa,Aamna tayi murmushi Tace Allah sarki yayi bacci,a gefen bed din ta zauna a hankali gefen kafafunsa,Nan take ta tuna da taga faratansa ya Tara sun Sha gyara,Room dinta ta koma ta dauko razor blade sabuwa dal ta bare,a tsorace tayi shahada ta Dan rike Yatsansa kadan sannan ta fara yanke Masa farcensa daya Tara Yana gayu da abinsa,ta fara yanke su Daya bayan daya,gashi da nauyin bacci har ta Gama hannaye Bai ko motsa ba Kawai baccinsa yake Sha,ta dawo kafa ma ta yanke Masa tas ta gyara ta kwashe farcen data yanke ta zuba a trash da razo din duka,ganin Bai da Niyyar tashi ta hakura itama ta koma dakinta Bayan ta kashe Masa hasken wuta ta Dan rufa Masa blanket sabo da taji sanyin ac yayi yawa.

Itama komawa tayi dakinta ta kwanta abinta,sai 2am Wayarta ta tashe ta sakamakon saita Alarm da tayi, Mikewa tayi tare da Gabatar da Sallah Nafeela raka'a hudu tayi Adduointa sannan ta koma ta kwanta,sai Asuba ta sake tashi tayi raka'atanil fijr tare da Sallar Asuba ta zauna ta Gabatar da Azkhar sannan ta koma bacci,10am ta tashi ta hau gyaran gidan,Compound kuwa me Gadi ya Gama gyara ko Ina har Garden,Dakinsa ta shiga karshe taji

karar ruwa alamar ya tashi Yana toilet,bedroom din ta hau gyarawa komai ya koma neat dama shi Sam Bai da kazanta akwai tsafta,ko Ina kamshi ne ke tashi,toilet ya Bude ya fito daure da towel a Kugunsa karami Kuma a hannunsa Yana goge wuyansa ga kitson kalabarsa Nan sabo an canja Masa sabo sai wani sheki yake Yi Bai jika gashinsa ba sabo da Attachment aka saka yellow, red and green,Aamna jikinsa ta kalla lukwi lukwi sumulmul,Fuskarsa a daure ko kulata baiyi ba ya tsaya a jikin Mirror Yana karewa Kansa kallo,Muryarsa taji yace Sexy Guy,gemunsa da Sajensa ya shafa yace Fresh Guy,Aamna ta zaro Ido taga Yana ta yabon Kansa Yana kallon Kansa a mudubi Yana shafa kitson kalabarsa,Toilet din ta shige ta gyara masa a ranta tana jinjinawa tunda take gyara Masa gida Bai taba nuna yaji Dadi ba ko abin ya birge shi ba,harkarsa Kawai yake Yi,Tana wanke toilet taji Muryarsa Yana Kiranta Bush girl.....Bush girl....tsoro taji Kar Taki zuwa ya Mata duka a banza Fitowa tayi da sauri Tace gani,Wani murmushi ya saki me tsada yace Good girl Ashe kin Gane sunanki,da Hargowa yace Ina wani perfume a Nan sabo? Murmushi Aamna tayi tace ai na dauke shi Ni zanyi amfani da shi sabo da Naga na Mata ne Kai Kuma Namiji ne,wani Ashar ya dura yace kin San tsadarsa kuwa? Yo ba gidan mijina bane,Kuma ma kayan Mijina ai Nawa ne ta karasa da shagwaba,Tsaki Yaja yace why are you always looking for my trouble? Idan na balla ki hmmm common dakko min kafin Raina ya baci,Aamna Tace Idan kana son na baka ka bani kudin Abinci ko ka siyo kayan abinci a gidan Nan yanda Zan na girki da kaina.

Wani Takaici ya kamashi ji yake kamar ya harbeta yace bana Baki kudin abincin ba uban me Zan Miki,Aamna Tace Ni ka bani Dan Allah yau naje kasuwa na shirya store da kitchen dina,kana min fuck up fa a gidana,kanta yayo Aamna ta fisge towel dinsa ya Fadi kasa ya dawo zigidir, da sauri ya dauki towel din ya daura kunya ta balain kamashi,Abu na farko a rayuwarsa da yake Jin kunya Bai so aga tsaraicinsa Amma wannan Yarinyar ta cuce shi,Aamna takawa tayi zata gudu ya cafko ta ya dakko belt din Wandonsa tana Ihu ya riketa Kam ya dinga tafkarta iya karfinsa,tana ta Ihu tana cewa banga komai naka ba,kayi Hakuri,bazan fadawa kowa,bazan cewa kowa ga Kalar abinka ba,ganin zai Mata Illa a banza Tace Tsinuwar Mummy a kanka,Yana huci Idonsa yayi jajir ya tsaya cak Yana haki,Ita kuwa Aamna da Dan Idonta Daya a manne ta Mike tana kuka Wiwi,ta koma toilet din ta karasa wanke Masa tana kuka ta fito zata fita kenan ya shirya cikin wasu kana Nan Kaya farare tas marasa nauyi wandon pencil irin na shakatawa a gida da Alama ba fita zaiyi ba yau,rafar kudi Yan dubu dubu ya jefo Mata yace gashi Nan ki Siyo Uwar kayan girki,last warning ba ruwana da ke,karki sake Shiga harkata,ke magana ma ban so ki min,Aamna Tace ai wallahi baka Isa ba Mijina Guda ai dole na maka magana,Kwafa Yaja yace to kuwa Zaki ci Ubanki wallahi.

Key din machine taga ya dauka Ashe fita zaiyi

Ba zato Aamna ta sa key din kofarsa ta kulle ta cire key din ta jefa a bra dinta Tace Yau ma baza ka fita Muna dakin Nan zamu yini sai dai yunwa ta kashe mu,lips dinsa ya tamke tare da rufe Idonsa kam tsabar bacin Rai,yace ban so Tsinuwar Iyaye ta shafe Ni,sannan gwara nayi komai Akan na taba Nonon mace Bude min kofa ko yanzu na karasa Miki idon Daya,Aamna ta tsaya sanye da Atamfa Riga da skert na lefe ne sun kamata sosai,Tace tunda aka auro Ni baka taba ko Dan Rungume Ni ba,Please yau kafin ka fita Ina bukatar warm Hug,just ordinary Hug,Nima yau Ina so na motsa jam'iyata,kina hauka ne? Meke damunki,Ni zanyi Hugging naki?

wata Dariya yayi yace Ashe nine ma na ganki nace Ina so,kanki akwai motsi lallai,Aamna Tace to lallai zamu kwana a Nan,tsayawa Suka Yi a Gaban kofa har na tsawon minti biyar ba Wanda yayi magana,nisawa yayi tare da girgiza gashinsa yace open the door,Aamna tace Baby Hug me Mana ka fita abinka,tunani ya tafi idan ya duketa Mummy dinsa,idan yace zai kwace key sai dai ya zura hannunsa a Boobs dinta shi gaskiya Bai son taba Nonon Mata,Baya Yaja kadan yayi Dan tangadi sannan yace Okay ya runtse Idonsa sannan ya Bude hannayensa,Aamna tana murmushi taje ai kuwa ya cakumeta irin bai iya ba Kawai cakumarta yayi ita Kuma tana sani ta kankameshi ya fisge jikinsa da bala'i yace bazan tabaki ba din,kinyi kinji Dadi Bude min kofa,Tace yanzu kuwa ta dakko key ta Bude Masa ya fice a fusace,ya hau machine dinsa kenan sai ga Aamna ta fito da gudu tana wait wait...da masifa ya juyo sai yaga Ashe wayarsa ce ya manta,Tace ka manta wayarka Baby,fisge Wayar yayi tare da Mata wani kallon banza ya Bawa machine dinsa wuta ya fita,Aamna kuwa wanka tayi ta shirya tsaf ta Kira Siyama kawarta suka je kasuwa,duk kayan Abinci na more rayuwa sun siyo dai dai gwargwado,tare suka dawo a taxi Suka shirya kayan a Store tsaf,kitchen kuwa komai na amfani akwai dama,sabo da Haka Jullof rice sukayi da wake taji kayan lambu da nama,Zuhra ce itama tazo ganin Amarya suka zauna suka ci abinda suke so,sannan suka gyara wajen,Palo Suka dawo suna kallo,Zuhra Tace Kan bala'i gaskiya gidan Nan ya hadu ba karya,Siyama ta Mike a saman doguwar kujera Tace har wani bacci nake ji ga ac ta ko Ina,Suna kallon wani Indian Series suna Hira sai ji sukayi an banko kofa,Siyama da Zuhra sai da suka firgita,ita kuwa Aamna ta Saba ko a jikinta tasan shine,ya shigo dauke da Ledar take away a hannunsa,Yana ganin Baki ya sake daure Fuska Kuma ko Sallama baiyi ba Sannan kallo Basu ishe shi ba bare su sa ran zai musu magana,ba Wanda yayi magana yazo har inda Siyama ke kwance a doguwar kujera yace cikin tsawa keee....tashi Zan kwanta a Kan kujerata,ai da sauri ta hantsilo kasa ya haye tare da kwanciya ya wani  Mike Yana wata Mika,su Zuhra sai kallon kallo,Suka Yi tsit a palon sannan Suka ce Ina Yini? Banza Iska yayi da su,da Tsawa yace bani remote ya dakawa Zuhra tsawa,ta Mika Masa abinsa Wai Gadara yake gidansa ne.

remote ya dauka da Gadara ya canja Chanel suna kallo ya Shiga wata Chanel ta Yan Iska Wanda a tashar Watarana har Xxx suke saka wa,sannan sai tallan Magungunan maza Dana Mata na Kara karfin gaba,da tallan kayan sex,Shi Kansa Bai taba kallon Chanel din ba sabo da su Zuhra ya kunna,ai kuwa sai Suka ga Ana Nuno maza da Mata tsirara,sai aka koma tallan condom na maza,Yana kalla yayi wani murmushi yace mun gode Allah ya Kara basira turawa,ya kamata fa ku yo Mana wanda yafi Haka kauri wannan fashewa yakeyi Bama Jin dadin shiga da fita,Mata aka nuna daga pant sai Bra,Ahmad yace wow see Bebs wannan zata Yi min,Wata kanjamammiya aka nuna,yace ke dalla matsa Jibson ke son irinku, kunya ta lullube su Zuhra Suka Mike tsam tare da yiwa Aamna sallama,Tace tun yanzu zaku tafi Haba Dan Allah? Ai ko kulata basuyi ba suka hada karansu sukayi waje,tuni suka bar gidan.

Yana ganin Haka yayi Dariya ya canja Chanel  ya koma kallon kwallon kafa,Aamna ce ta dawo daga rakiyar su Zuhra,da kukan shagwaba ta shigo tana dire diren kafafu tana Haba Dan Allah....Haba...Dan... Allah Baby, wani Haushi ta bashi Takaici yasa Ahmad ya zaro Wayar charger ya kifa Aamna da ita ta gudu dakinta ta kulle Kofar ya dawo Palo Yana masifa Ni Zaki yiwa shagwaba,Baki San na tsani wannan haukan ba,aikin banza Kawai,wani Ihu ya saki Yana

kallon yatsunsa na kafa Dana hannu,Jin Ihu sa yasa Aamna ta yo waje ba shiri tana cewa lafiya? a tsorace yake lokacin shi yasa yace fingers Dina,farce na Dana Tara Ina ji da su an yanke min,jikinsa ya kalla tsaf yace Aljani ne,Amma wannan ya cuce ni,Dariya Aamna ta dinga Yi Tace nice ta fece da gudu daki.

Rasa abinda zai Mata yayi sabo da bacin Rai wuka ya dakko a kitchen ya ajiye a kusa da shi yace yau Zaki ga abinda Zan Miki ba ruwana da wata Tsinuwar Mummy.

AsmaBaffa

10/26/21, 8:52 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA🌵🌵

26-30

FREE PAGE

DUNIYATA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

NA KUDI NE

GA MASU BUKATAR SHIGA GROUP DARI BIYU 200 NE.

ACCOUNT NUMBER
0175487861
ASMAU GARBA MUHAMMAD GTBANK

MASU TURA KATIN MTN KO VTU GA NUMBER
08033933642

'YAN NIGER KU NEMI WANNAN NUMBER
+227 90 79 59 39

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne

AGRA
ANEESAH
UMMIN HIBBAH
ASMAU YUSUF
RAHMA
FARHAT MRS MJ
PHAATIMAH

Ranar Aamna Bata sake Fitowa ya ganta ba kullum sai ta tabbatar ya fita take Fitowa tayi abinda ya kamata har kwana Uku sannan yau Bayan tayi Sallar Isha taci abincin data dafa Tace Fitowa zata Yi ai ta San yanzu ya huce,a hankali ta fito sanye cikin wani Bum short sky da Riga t-shirt red ta zuba kyau ciki,tana Fitowa taga shima ya banko glass door din palon ma'ana yanzu ya shigo kenan,Yana ta uban tangadi ya fada saman kujera shirim Yana magana a hankali cikin maye shi kadai,Aamna ta kalleshi taga bacci zaiyi ta lallabo a hankali Tace ka koma bedroom ka kwanta,ya furta barrrr.......niiiii....aaaaa.....aaaa....Nan.....Aamna Tace no Nan bazai maka dadin bacci ba tashi ta Kama hannunsa kenan ya fisge hannunsa,sake rikewa tayi Tace taso ta janyo shi ya Mike da kyar Yana tangal tangal a Haka ta kaishi sama ya fada saman bed

dinsa,tsugunawa tayi ta zare Masa takalmansa a hankali,ganin har ya fara bacci ta Karo Masa karfin Ac din ta kashe Masa light ta fita ta barshi tana tunani,Palo ta dawo ta zuba Uban tagumi tana mamakin Ahmad kullum cikin shaye shaye baya Free Sam,Tace wannan wacce kaddara ce Haka ta sameni,da wacce zuciyar Zan iya daukan wannan masifa,gashi na Bari an daura Aure ya zanyi,Sam bana birge shi duk shigar da nayi Bai taba kallona ya nuna na tafi da shi ba duk da Nima ba so nake ya Yana ba.
Taya zai shiryu Haka,Ido ta lumshe ta kwanta a saman kujera tana ta sake sake a ranta.

Dakinta ta Mike zata tafi Bayan ta Gama kashe kayan wuta ta sake leka shi ta gani ta hango shi kuwa Yana ta bacci Amma ya dunkule waje Daya Yana ta Rawar sanyi kamar zazzabi ne a jikinsa,dama taji jikinsa ya dauki zafi dazu,kamar ta wuce sai ta fasa ta shiga bedroom din,a gefen bed din ta zauna tana tunanin me zata Masa,Tsaki ta ja kadan ta shiga zare Masa Riga a hankali,jikinsa ta taba zafi zauuuuu,Toilet ta shiga ta ebo ruwa a Bowl da towel karami ta shiga goge masa jikinsa a hankali,kirar jikinsa ta shiga karewa kallo tana Dan goge Masa jikinsa da Towel,ita mamakinta Sam a face baiyi Kama da me Shan giya ko wani Drugs ba,idan baka sani ba baza ka taba ganewa ba,sai dai acting dinsa yanda yake abu ba tarbiyya kana gani,Ac din ta kashe gaba Daya sannan taji zafin jikinsa ya Dan ragu,a hankali take girgiza shi tana tashinsa Me Burkutu....me Burkutuuu.......Shuru,taceme giyaaaaa.....Shuru,ta girgiza shi shuru, Kuma Yana numfashi sai da ta Dade sannan taga ya dafe Kansa da Alama ciwo yake Masa Yana Nishi kadan yace Ohhh my God,a hankali ya Dan Bude idonsa,ba a wani hayyacinsa yake ba,ya fara Mika Hannu jikin Drower yace i need to take my drugs,Drower din ta Bude da sauri mamaki ya kashe ta ganin kwayoyi iri iri Kamar hauka duk na Maye,Salati Aamna ta saki Hawaye ya shararo Mata ta shanye da kyar,ta Dan duba Drugs din sai taga paracetamol,shi ta ballo ta dakko Masa ruwa da sauri ta Mika Masa Yana daga kwance ya karba ya Sha abinsa a kwance shi ba Wani ganeta yake Yi ba.

Zama ta ci gaba da Yi gefen Bed din tana ta faman gyangyadi,so take Yi ta ga ya samu sauki,a ranta Tace ko Ina ruwana oho,Amma tunda dai lalura ce Bari na jira,tana Nan zaune taga ya fara Juyi ya hada uban zufa alamar zazzabin ya sauka,ac ta kunna Masa,cikin mayen baccinsa yace Mummy yunwa Zan Sha ruwa,Aamna ta kalle shi taga bacci ma yake Yi,da sauri tayi kasa ta hau dafa Indomie lokacin 11:30pm, sharp sharp ta Gama ta dakko da kankana wacce ta yanka Nan take,da sauri tayi sama,ta ganshi zaune a gadon ya jingina bayansa a fuskar bed din ya lumshe Ido,still ba Riga a jikinsa.

Aamna ita ke shirmenta ba ganeta yakeyi ba ya bugu da yawa dishi dishi yake hango ta shi yasa ya kyaleta da lafiya yake da tuni taci duka,sabo da samun waje saman bed din ta haura ta zauna a gefensa Tace ga abincin,you have to eat something sabo da kafi Jin sauki,a hankali ya juyo ya kalleta ya turo lips dinsa gaba,Tace haba na Mummy ci Mana karka kwana da yunwa akwai Dadi wannan Indomie taji Hadi kaci sai kayi Santi,Kansa ya dauke can gefe,Aamna Bata hakura ba harda rera waka Wai Dan tuzuru....ya dawo mata,.....yanzu....da ba'ayi maka aure..... ba wa zai dafa maka....Oya Fadi kaima tana tafi,Dake a bige yake sai yace shima Nine Tuzuruuu......yawwa to Bude bakin ta furta tare da ebo Indomie a fork,.....ya Bude da kyar Yana kumbura,ta zuba Masa tana murmushi Tace Ehemm....mutumin kirki...maza Kara ci ta sake

ebowa ya karba a bakinsa,Tace Good King...oya again....ya karba,yaji tayi Dadi sosai tana ta bashi Yana ci Yana ganinta dishi dishi.

sai da ya cinye tas ta dakko kankana Itama Haka ta dinga bashi baya ko magana sai da ya Sha da yawa sannan yayi gefe can da Kansa

Nan ta Gane ya koshi,ta Balle ruwa ta tsiyaya a glass cup ta bashi Nan ma a Baki ya shanye ta Kara Masa ya shanye,Tace Inye King din ba,Harara ya Aiko Mata tayi shuru,ta tattara kwanikan ta maida kitchen,shi kuwa Yana Jin karfi a jikinsa wanka yayi sai lokacin Yayi Sallar la'asar ,Magriba da Isha sannan ya kwanta bacci ya sake gaba da shi.

Aamna shugowa tayi taga yayi bacci ga sallaya alamar Sallah yayi,baya kashe light sai ta kashe Masa tare da sake feshe room din da wani Room freshner me Arnen kamshi ta rufe Masa kofa taje itama ta kwanta.

Washe gari da Ihu ya farka Daya tuna kamar jiya Aamna ce ta shigo,Nan ya tunano me tayi,wani ransa ne ya baci shi kadai ya dinga masifa har yayi wanka ya fito cikin wani gajeren wando ruwan toka da Riga brown t-shirt,Lokacin Aamna ta cakare cikin wani wando legins tight,pencil tayi kyau duk na lefe ne, Yar rigarta yellow me siririn Hannu cibiyarta a waje,a kitchen take tana shirya Breakfast kamshi ya cika gidan,ji tayi kamar ya fito da sauri ta fito ta sawa Kofar palon key Yana kallonta yasan cewa zata Yi bazai fita ba sai ya Bata kudi ko wani Abu,dama da fushinta ya tashi yau,yace tun kafin na Miki duka ki Bude kofa ko ki Fadi abinda kike so na Baki,bani da lokacin shirmenki yau,Aamna Tace Breakfast zaka ci sannan ka fita,kullum Ina matarka baza kaci Abinci na ba yau ba inda zaka fita a gidan Nan,sabo da ma baka da lafiya baka Gama murmurewa ba,Ahmad yace shine jiya kika shiga Zaki min fyade? to ta Allah ba Taki ba,nafi karfinki,Wai harda wani cire min Riga ke Uwata ce ko ubana,ke Wai matata ko?Dariya ya bawa Aamna Tace ae naji zauna ka jira Ni,idan naki fa?,kitchen ta shiga da sauri ta Hado komai a tire ta kawo gabansa a Palo ta Ajiye Tace Bismillah kayi ka ci na Bude maka ka tafi,sai da ya dauki lokaci sannan yace badan Ina tsoronki Zan ci ba,Dan Ina da abin Yi ne kawai yau,Aamna Tace a Haka zaka fita da gajeren wando?

Ina ruwanki munafuka Uwar gulma ya Furta,Shuru tayi Tace Enjoy your meal,Bread ya dauka ya gutsira ya kurbi tea sau daya,sai ya dauki chips Guda hudu yaci yace to Bude min na fita,ba musu ta Bude masa,zai fita ya zuba Mata Rankwashi me zafi ya fita abinsa,Ihu ta saki kadan ta zauna ta cinye abincin nasa,shi Kam Machine dinsa ya hau ya fita da shegen kitson calabarsa,Wanda sai dai ayi ta binsa da kallo.

Tunda ya fita Bai dawo ba sai cikin tsakiyar dare,yau anci sa'a Bai Sha komai ba,hannunsa dauke da Ledar take away na abinci,a gajiye ya shigo Amma yaga Aamna zaune tana kallon American film,Sannu da zuwa ta furta,Baki ya tabe ya haura sama abinsa ko kallo Bata Kai matsayinsa ba.

Bayansa ta bi a hankali Yana jinta Bai kulata ba,Yana Shiga bedroom dinsa Wanda ya Sha gyara kamshi ne Kawai ke tashi,kafin ta Shiga ya kulle kofarsa tare da murda key Yana faman Jan Tsaki,Dariya Aamna tayi tana daga jikin Kofar Tace ya jikin naka? Kai ya girgiza yace Uwaki

yake ciki,,ta rasu fa marainiya ce Ni,Yace to tayi ta mutuwa Mana Ina ruwana,Wai ke Baki da zuciya ne? Aamna Tace ae bani da ita My Husband,tana Jin tsakinsa ta juya ta koma dakinta ta kwanta abinta tare da Adduar bacci ta kwanta.

Shi kuwa Abincinsa ya zauna yaci ya shiga toilet yayi wanka tare da brush,cikin kayan baccinsa dogon wando da Riga me dogon Hannu silver color wani yadi Silk sharara,Sallaya ya shimfida ya fara jero sallah ba nutsuwa ba komai da saurin masifa kamar zai tashi sama,idan yayi ruku'u ko Gama dagowa baya Yi zai sabe da sujjada, kafin kace me tuni ya idar tun daga Azahar har Isha,ko Addua babu Ya Mike Yana tunanin ma kamar Sallar Isha raka'a Uku yayi Amma ya fuske tare da furta Ina laifi ma na karasa raka'a dayar a raina Kawai ta cika hudu nayi ya fada saman bed yayi kwanciyar ruf da ciki sai bacci.

Washe gari 9am ya tashi kasancewar baiyi shaye shaye ba,Room din dake cike da kayan Exercise ya shiga Yana ta motsa jikinsa sai da ya Dade sannan ya fito sanye cikin kayan gym dinsa bakake yayi kyau,Yana Fitowa ya Iske Aamna har ta Gama gyara ko Ina na ciki,kamshi yaji a kitchen lekawa yayi ya hangota tana ta soye soye, Shiga yayi fuskar Nan ba Rahma cikin Muryarsa ta Yan kwaya yace bani kasko zanyi girki,Aamna Tace ga wasu Nan ka dauka Mana Kuma ma ai gashi Ina girkin da Kai sai muci wannan,cike da bala'i yace da wannan nake so nayi,gidanki ne ko Ubanki ya Siya min kayan kitchen ne? ai kayan Mijina Kaya nane Kuma wallahi bazan baka ba,baka Isa ba kayi kadan kayi karami da yawa na baka kaskon nan, sabo da Nan gidan Mijina nane Kuma gida na yawwa eheee ....Mari ya dauke ta dashi garin Jin zafin Mari Aamna ta saki ludayi ya Fado saman kafarta gashi yasha Mai na suya me zafi Nan take ya kone Mata wani Dan bangare a kafarta,Ihu ta saki ta durkusa kasa Amma duk da Haka Bai kyaleta ba ya tallafe Mata keya ya dauke kaskon da man Baki Daya da dankalin ciki ya watsa a cikin Sink,har kankon ya Bari cikin Sink,sabon kasko ya dakko ya fara Girkinsa,Aamna ta Mike cikin bacin Rai da Hawaye a fuskarta ta tattaro karfinta ta durma Masa duka a gadon baya ta arce da gudu,shi ko jin zafin dukan ma baiyi ba,ita Tunaninta ta Rama,Zuma ta dakko tare da shafawa a kafarta iya inda ya kone,Palo ya dawo da kwansa soyayye da tea da wani snacks Kamar bread,Aamna Fitowa tayi dama tasan shi Bai zuwa Dining Sam,Yana Palo zaune saman kujera ya wani kishingida a Haka yake cin abinci,Aamna a ranta Tace duk abinda ya shafi Sunnah da dabi'a ta Musulmai baya Yi Sam,abinci a kwance za a ci,a kasan center carpet ta zauna tare da nannade kafafu kamar wacce zatayi karatun Qur'ani ta zuba Masa Ido,Hannu ta zura da sauri ta zari soyayyen kwai fefe Daya,ta fisge snacks ta balli Rabi ta Ajiye Masa,ta Buda tsakiya ta sa kwanta ciki ta rufe,Bai ko kulata ba,tana ta ci yasha tea da yawa saura Rabi ta dauke cup din ta gudu,dama ya koshi shi take uban gudu da tayi zamanta ma shi baida time dinta yanzu.

Mama zaune take a Palo tana gyara wake Baba yayi wanka ya Sha Yar shaddarsa zai tafi kasuwa ya daga Hannu sama yayi wata Hamma tare da Mika yace Alhmdllh Aishatu sakayau nake jina,Kamar wani sabon musuluntа,ji nake Kamar yau aka Yi min wankan tsarkii,sabo da mun Aurar da Yaran Nan mun huta Kuma Alhmdllh Bamu siyar da akuya ta dawo tana goge Mana danga ba,Mama Tace Bari Kai dai Baban Zuhra ai idan na tuna musamman Zuhra tana can tana zamanta lafiya sai naji Ni kamar Ina cikin watan Ramadana Naga Kuma Daren lailatul

qadri,ita kuwa Aamna mun fita ko ba soso ba Sabulu,ta koma bangaren danginta suje can su karata,gashi Dake so suke su Aurawa Dansu Dan Giya har da bani jarin Million Uku cewar Baba shima,Mama Tace yo ai mun gano wayon badan Allah aka Bamu ba,harda wani gida ,Baba yace ai Ina sani na kwantar da Kai na nuna musu mutunci na hada dabara nace su bawa Aamna auren Ahmad zai shiryu.

Hahaha Mama tayi Dariya Tace Dantijara wannan ai bazai taba shiryuwa ba,ita Kuma Aamna nasan kwadinyin tsiyarta shi zai zaunar da ita shi yasa kaji shuru,ko mun Mata waya sai Tace lafiya suke,Munafuka cewar Baba tana can tana Shan wahala,yanzu da zamu je sai Munga ta rame,Kaga yanzu har tayi kusan wata Guda da Aure, kudin Sadakinta data Bamu mun karbe ba ruwanmu sauran Kuma da Tace a siya Mata wake a ajiye a Kauye fa? Baba yac ae gobe fa zamu je gidan Aamna sabo da karta gano cewar Bamu damu da ita ba ko Bamu dauke a matsayin 'ya ba sai mu tafi Mata da kudinta mu Bata muce Kar tayi wannan sana'ar Kawai ta kashe kudinta,Mama Tace ita a dole me Neman kudi Ubanwa zai barta tayi Sana'a, Dan taga kudin sadakin Zuhra mun siya Mata Saniya a Kauye Ana kiwo shine itama tace a siya Mata wake,Mama Tace ai baza mu Bari ta Gane komai daga wajenmu ba,kamar yanda ta taso a Hannunmu ba yabo ba fallasa ita Bata Isa Tace Bamu sonta ba Kuma Bata Isa Tace muna sonta ba to yanzu ma hakane,musamman yanzu da ta auri jinin kudi,a hankali zamu dinga zurarta kudi,so nake Nan gaba ta Bude min katafaren shago na siyar da kayan sawa na Mata cewar Mama,Baba Yana dariya yace ai Ni Kinga na samu jari.

Amma naga Harkar tayi min kadan dole Nan gaba Nima ta Kara min jari,Mama Tace na karbo wasu layu da guru idan munje Zan sa ta Kara daura su so nake sai na mayar da ita Yar bori da wayo sabo da idan Mijin nata ya gani yace malamai take bi kaga bazai taba sonta ba bare ta zauna a daula,lokacin mun yagi rabon mu,idan ya sako ta sai ta dawo ta zauna a shago na Wanda Zan Bude Nan gaba da kudin surukanta ta dinga siyar min da kayan.
Baba Yana dariya har da buga kafa yace kin iya planning,tunda Bata auri talaka ba Allah ya canja lamarinsa Kinga muma harka ta Bude sai mubi a Haka mu yagi rabon mu.

Siyama kwance take saman tsohuwar katifarta sai faman Juyi takeyi tana murmushi ita kadai tare da matse pillow a hankali Tace Kai idan ban ganshi ba yau bazan samu nutsuwa ba,Wasa Wasa a hankali sonsa ya Shiga Rai na daga ganinsa sau biyu sau uku,wata zuciyar ce ta gargade ta tace to Faisal din naki fa,Kuma Wanda kika haukace akan sonsa Mijin babbar kawarki ne, wata zuciyar Tace so so ne Amma son Kai yafi,a fili Tace duk yanda naso kawata ta samu farin ciki ai Bai Kai ga kaina ba,Kuma ma mene tunda Allah Bai haramta ba,abinda ya Dace na San yanda zanyi ya Gane Ina sonsa,kafin kawata ta rigani gwara Ni na rigata,zumbur ta Mike Tace dole na Kori Faisal na daina sonsa,Sam baya birge Ni yanzu,Akan Ahmad Zan iya koyar Shan barasa Nima Indai zai so ni,ta yanda Zan bullo kenan Nima na nuna Masa Ina Sha nasan zanyi Nasara,Mikewa tayi tsaye tare da jawo Wayarta ta danno Number Aamna.

Aamna kuwa daidai wannan lokacin 11am su Mashkoor su Biyar ne Suka zo tare da cike palon suna ta kurbar giya,Ahmad Yana kwance,Aamna ce ta fito sanye da Arabian gown black da Alama fita zata Yi,ta gansu a palo,kallo Suka bita da shi Banda Ahmad da ko kallo Bata ishe

shi ba,Mashkoor ne ya galla Mata Harara ya furta anzo an aure Mana Sarkin mu,kina Bata Masa Rai a banza,Jibson ya ja tsaki,Aamna dai Bata ko kulasu ba,wurin Ahmad ta karasa ta Dan dukar da kanta saitin Fuskarsa Tace zanje kasuwa ba kayan Miya da kayan lambu ka bani kudi da Izni,Tsaki Yaja yace dalla Wai Ni na kawo ki ne,ki tafi ko Ina kika ga dama,Kudi ya jaro dubu Ashirin ya jefa Mata a Fuska yace dauki ki bani waje mayya,Su Jibson Suka kyakyace da dariya ba ji ba gani,Aamna ranta ya baci ta Harare su tayi waje abinta.

Tsaki Ahmad Yaja ya fitar da kudi masu yawa, wani yace bawan Allah ka Adana kudin Nan Kar ka hadu da Yan Iskan gari,Mashkoor Yana gefe yace ai mune da kanmu baka gani bane mune ai Yan iskan da kanmu a Nan,wa ya Isa ya zare Mana ido,aka Yi Shuru matar tana irgawa

Ahmad kudi tana ajiyewa ya galla Mata Harara yace ke ni fa bana son Daudu Yar Daudu idan Baki iya aikinki ba wallahi na Kai kararki a koreki banza,Wai ke ma'aikaciyar Bank harda wani sa glass da Suit ke a dole kina samun salary,Yan Yara daku Kuna rainawa mutane wayo kuka sake kwanan bank Dinku tattalin arzikinsa zai durkushe mu daina Ajiyar kudi,Duk ma'aikatan sun San Ahmad Yana zuwa Yana musu tijara shi yasa Yana zuwa suke sallamarsa ya tafi,suna gamawa Mashkoor yayi wani Bouncing Suka juya Ahmad yace My man oya muje... muje....Yana wani Gadara,Wandonsa Daya sabulo ya danja kadan,Zasu fita kenan sai ga Aamna ta shigo itama zata ajiye kudi a bank,Ahmad ya kalleta Kamar ba matarsa zata wuce su ya riko Hannunta tare da sa damtsenta ya sakalo wuyanta yayi masifar kunyatata a mutane sai ayi Mata kallon karuwa,Fisgewa tayi ya dauke cak tare da Sabata a kafada yace Muje kudin cefanen kika taho ajiyewa bank Zaki tara? sabo da kar mutane suyi Mata kallon karuwa Tace Dan Allah ka ajiyeni Ina matarka Wai kullum sai kaci Zali na,kaje gida your food is ready, Ni ka ajiyeni wallahi,Ana kallo tana wutsil wutsil yayi waje da ita,Wasu suna cewa kanwarsa ce sabo da suna yanayin Kama sosai,wasu Kuma suce da gaske matarsa ce,wasu suce ko karuwarsu ce,Wani yace ai kuwa wannan zata Sha wahalar Zama da wannan bakin kadarar,wanne ubane Yana gani ya bawa wannan auren yarsa oho.

Wajen Machine suka fito,Kamar Yana da hankali shi ya fara Hawa machine din sannan ya Mata Tsawa yace hau,Haka ta hau bayansa Mashkoor ya fige su kamar zai tashi sama,ya dinga kwanto a titi Yana ratsa motoci sai ihu sukeyi Aamna tsoro ya kamata ta kankame Ahmad yace wallahi idan Baki sake Ni ba sai na jefo ki a tsakiyar kwalta,kin sakinsa tayi har suka kaita bakin gate yace sauka,ta sauka yace kina Wasa da Mummy ta kawoki Nan kina wani yawo anyhow,Aamna tayi banza da shi ta shiga gida,Bai Dade ba ya dawo ya Iske ta baje saman Kujera tana bacci,ruwa ya ebo a kitchen ya sheka Mata a Fuska ta tashi a firgice,Harara ta balla Masa ta Mike ta wuce Bedroom dinta tana saka ranar da zata bar gidansa domin ta gaji.

Garin Lagos Unguwar Masu hanu da shuni Mummy tana zaune Tare da Humaira a wani gida na ubansu Wanda idan ka kalli gidan ka kallo gidan Ahmad duk kyansa sai ka ganshi gidan talakawa,Humaira ce ta dauki waya Tace Mummy Bari na Kira Yaya naji,Ahmad ta shiga Kira Yana ganin Sis ya daga da sauri tare da furta sweety,Dariya Humaira tayi Tace Yayana ya kake yace Ina lafiya sis ya school,ai nayi Candy Wai ka manta na fada maka Yaya? congrat...Congrat Sis,Yaya Ina matarka? Zamuyi fada fa Ni nasan wata ne Kawai dai nasan Wacce Mummy ke so karki dameni Zan kashe wayata,Sorry Yaya ke ba Wani Yaya kauyanci ne karki Dora min tsufa da wuri wani Yaya,ki kirani Ahmad Dina sak ko King,Mene wani Yaya,ai girmamawa ne Yaya,bana son wani girmamawar mutane a wajena ke dalla Ware kiit ya kashe wayarsa Yana tsaki,Mummy ta kalli Humaira tace ai halin Ahmad sai shi na rasa inda ya gado halin Nan,Allah ya kyauta.

Faratan Ahmad sun Kara tsayi sosai,Aamna tana zaune a Palo Yana kwance ta juyo ta kalle shi,Fuska ya Murtuke,Kallonsa ta sake Yi tana kasa a zaune ta jingina da kujerar da yake kwance,kanta ya dafe tare da Danna kanta kasa,Kara ta saki ya fisge dankwalin Atamfarta ya zabga Mata duka dashi,layun Dake kanta ya kalla ya saki Dariya yace nasan na fiki daraja a wajen Allah duk Iskanci na,ke shirka kikeyi yarinya duk Sallar da kike Yi ba a karba,munafukar

banza kullum Sallah da karatun Qur'ani Ashe wurin bokaye kike zuwa,shi yasa Allah ya hadaki aure Dani ya daura Miki kaddarar Zama da me cin ubanki,Allah ne yasan irin Barnar da kike yi,Ni duk Iskanci na bana zuwa wajen boka,bana daura guru da Laya,Yan Iska irinku ne masu yiwa Miji Miya da jinjin Haila,fada min ke wanne kikeyi? Aamna Tace Ni wallahi bana zuwa wajen malam,karya kike munafuka,Ni nasan ba Banza Mummy ta auro min ke ba,kin shiga Uku kuwa ke da Jin dadi sai dai ki gani a makwafta,Aamna tayi Mukus ta Mike tare da cire layun gaba Daya ta yaye Hannunta ta Ware gurunta,ta daga rigarta ta zaro na Hips,Baki Ahmad ya bude yace kin Shiga uku,Uku ma sau dubu kika shiga,Ni ba ruwana da tsafinki ki maida abinki kece Zaki ga ba daidai ba a duniya,Zuciyarki ba Allah oh a Haka Shuru Shuru Dake sai daukan carbi da sallah,Ana karatun Qur'ani Ashe duk bana tsoron Allah bane,asubar fari za a jiyo muryarki har makwafta ya makale Murya tare da gwada Muryar Aamna yanda take karatu Wai Allazikhalakhal samawati wal'ard.....Ashe bana tsoron Allah bane wallahi sai Allah ya tambayeki.

Aamna tayi Mukus yace ai dole kiyi Shuru ki kalleni kice me? Watarana sai Allah ya Toni asirinki.

Dariya Aamna take Yi ta fara warware layun a gabansa da gurun,ya kalli takardar me Rubutu yace ga harafin A'lif da Hya'un can Wato Sunana kenan Ahmad gashi can na gani,Aamna ta tattara ta kone komai,yace a banza yarinya Yar bori mutuniyar banza,Harararsa tayi ya Mike ya bita zai daketa tayi daki da gudu Yace ki dake Ni ki hanani kuka ki min asiri in gani da Ido na ki dawo Kuma ki harareni Ni ban harareki ba sai ke,Zaki fito ne.

Washe gari Aamna gajiya tayi ta fito lokacin zai fita tace Yau zaka nemeni ka rasa a gidanka yau Zan tafi gidan ubana,wani farin ciki ya Kama Ahmad yace Dan Allah da gaske kikeyi? Aamna Tace da gaske yau a gidan ubana Zan kwana,wani murmushi ya saki yace gaskiya ban taba sanin kina da kirki ba sai yau,Sabo da Haka yau dole Nima na gwangwaje ki,fada min me kike so? Aamna ta turo Baki ta samu waje,yace ai yau ko me kike so Zan miki,Aamna ta Kama shagwaba Tace koma mene ka bani kyautar Ina so,Ido ya zaro Mata wasu farare tas sai da ta tsorata Yace Gaskiya Zan fada Miki ke Yar Albarka ce babarki ta iya haihuwar Yar halak Haka nake so,yanda kika faranta min yau ace ban Miki kyauta ba nayi asara bani da amfani Kawai na mutu yanzu,Dariya ta Kama Aamna duk akan Tace zata bar Masa gida shine yake wannan murna Haka,wannan kiyayya wacce iri ce,Tunaninta ya katse Mata yace shirya kizo mu tafi na kaiki Shopping ki zabi abinda kike so na ban kwana,Dan Allah Kuma idan kin tafi karki dawo har abada kinji,Aamna Tace to,yace ko Mummy Tace kice a'a ke ba 'yarta bace ta juya Humaira Yarta data haifa Amma ba ke ba,Aamna Tace to,yace Ina jiranki,Da gudu taje sama ta canja wata Arabian gown Dark green me adon black ta Sha kyau ta fito.

Machine dinsa ya gyara ta hau ya fisgeta Suka tafi sai wani katafaren Mall,tare suka shiga yace Ina jiranki zabi duk abinda ya miki,Aamna Bata zabi komai ba ta wuce Bangaren Gold ta zabi wata sarka me kyau da zobenta da Dankunne,yace shike Nan abinda kike so? Tace ae,Kai ya girgiza yace to dauka,Haka ta dauka yaje ya biya kudin Suka tafi,ya maidata gida zai fita Tace to saka min da Hannunka kaga anjima Zan tafi,yace ai yau ba abinda Zaki ce banyi ba tunda Zaki bar rayuwata na huta kawo,Mika Masa tayi ya saka Mata sarkar da kansa da

dankunnen,Yatsanta ta Mika Masa ya sa Mata zoben,yace Nice one, karfe Nawa Zaki tafi? Aamna Tace 6pm yace Good,ya Mike zai fita Yana ta murna yau zai rabu da Kaya ya huta,Aamna Tace Idan ka dawo sai na tafi,yace to ai da wuri kuwa Zan dawo ya fita Yana ta murna Kamar an Masa albishir da Aljanna,Tun kafin 6pm ya dawo gidan ya shigo Yana wakar Bob merly Yana Bappalo Soldier........Ye...yiye....yiye.....Yee...Yee....yiye...

Sharhi fans Dan Allah.

AsmaBaffa
10/26/21, 8:52 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

41-45

FREE PAGE

DUNIYA TA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

NA KUDI NE

GA MASU BUKATAR SHIGA GROUP DARI BIYU 200 NE

ACCOUNT NUMBER
0175487861
ASMAU GARBA MUHAMMAD
GTBANK

MASU TURA KATIN MTN KO VTU GA NUMBER
08033933642

YAN NIGER KU NEMI WANNAN NUMBER
+227 90 79 59 39

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne

ZEE NANDU
KALTUMA ZANNA
SADEEY(QUEEN)
TEEMA'S COLLECTION

.Aamna daga kitchen ta fito tana amsa Masa wakar tasa tana  girgiza Kai ta kwala da karfi Ohhhhh.....yeyi..yiye...your.....bappalo soldier....tsit Ahmad yayi murna ta koma ciki da Alama Bata da Niyyar tafiya,Girar sama data kasa ya hade kamar an Aiko Masa da Mummy ta rasu,Aamna kuwa Bayan ya fita zuciyarta ce tayi sanyi ta huce,kafin ya dawo Allah ya yayyafawa zuciyarta sanyi da Hakuri sai ta fasa,Siyama kuwa tunda ta tafi tana sa ran Aamna zata bar gida take ta murna tana uban Kiran Aamna akan taji ko ta bar gidan Amma karshe ma Sai Aamna data Kira Aamna tana dagawa sai taji tana dariya Tace ke Siyama na fasa tafiya na huce,na tuna ma fa Dan kwaya ne ba a ba'a hankalinsa yake ba nayi Masa Uzuru,ko ba komai ma ai Ibada nakeyi,aure Ibada ne zanci gaba da Masa Addua Allah ya shirye shi,Siyama ta danno Mata ashariya Tace wannan bazai taba shiryuwa ba,Ibadar me aure ne kadai Ibada a duniya,Aamna Tace Sanda Zaki auri Faisal ai masifa kika Kama Yi min akan nace kinyi gaggawa yanzu Kuma Ni da gidan mijina Zaki shigo kina min katsaladan a gidan aure na,kin fa Sanni Siyama ki daina uzura min Ina ta Miki Kara bakya gani,Ya kashe Ni ma Mana Ina ruwanki,Siyama Tace Iyyeee....Mrs Ahmad shike Nan kije ki zauna a wahalar,Tsaki Aamna tayi tare da kashe wayarta.

Yana Zaune sai kunci yake faman yi,Aamna ta kamo Sunna tv taci sa'a kuwa an saka Wa'azin Malam Ahmad Tijjani,Yana magana akan hatsarin shaye shaye,Yace yanzu Duniya Malam ta lalace da shaye shaye,maza,Mata,Yara,manya,Dattijai,abin haushi ma Yara kanana matasa sun Gama kashe kansu da shaye shayen kayan Maye,abin Allah wadai matashi lafiyayye ya jefa Kansa a halaka,ya Zama marar amfani a rayuwar Musulmai,Musulunci bazai Yi

alfahari da su ba,Shan Alkhabis,baza a Sha Aldayyib ba,Mene Alkhabis? Alkhabis shine abinda idan anci ko an Sha bashi da dandano me Dadi a Baki sannan a jiki Yana cutarwa,Aldayyib shine a Baki da Dadi a jiki Kuma Yana da amfani me kyau.

Ko matasa jira kuke sai an lissafa muku a Alqurni ance Giya,taba,Wiwi,har Ana kawo ayar Allah Kuna cewa babu Aya,Ina Iyaye wallahi ku farka,Matasa maza da Mata Kuna da hankali,shaye shaye na kwaya,na hayaki na ruwan barasa da sauransu bashi da amfani ga rayuwarku sai cutarwa,Kun Zama marasa amfani a cikin Musulunci,shaye shaye shi kadai yana barna ba adadi a wajenka matashi,na farko shine Kai da lafiya kunyi bankwana,zai kassara maka lafiyar kayan ciki da dama,sannan babbar Illa zai rabaka da Allah,zai rabaka da addinin Allah,zai hanaka Sallah ko kayi ma kana cikin maye baza a karba ba,Azumi ma Sai ya hanaka domin zaka dauka ka kasa kaiwa sabo da dole sai ka Sha kayan Maye zaka zauna lafiya ya Gama bin jininka,sannan zaka sabawa Iyayenka babbar matsala sabo da dole sai ka kangare,ka bijire musu zaka cutar da su.

Kasan kuwa wa ake cewa iyaye,ya ku matasa wallahi wallahi ku guji fushin iyaye,masifa ne Mahaifiyar ko Mahaifi su zubar da Hawaye a kanka,basai sun maka Addua ba Kai da ganin dai dai a rayuwarka sai in ka tuba sun yafe maka,wani abin haushin ma Iyalinsa zai dinga zalintar matarsa da yaransa,ya mazaje ku San hakkin matanku mataye Kuma wallahi wallahi kuji tsoron Allah duniyar Nawa take,bakwa ganin halin da ake ciki mafi yawan alamomin tashin kiyama sun bayyana,nuni ake mana mu Kara gyara Hali lokaci Yana matsowa,wallahi a Haka Ana da saura da saura Ana ganin kamar da saura a Haka za a wayi gari aga manyan alamomin tashin Alkiyama sun fara Bayyana.....

Ahmad Yana ji ko a gefen rigarsa sabo da yaji Wa'azin Daya fi wannan zafi ma, Canja Chanel yayi yace idan Kinga dama ki gayyato malaman Nigeria kaf su zagayeni ki gani idan zanji na gyara,Aamna Tace ikon Allah a ranta Tace lallai wannan bazai canja ba gwara na nemi mafita,Giyarsa ma taga ya dakko ya Balle Yana korawa, Tsoronsa ya sake shigarta,jiki a sanyaye ta koma dakinta,a palon ya dinga zage zage tana ji,Haka tayi kwana Uku lokacin tuni taje ancire Mata plasta da aka manne Mata ido,sai ganin Idonta yayi tar da Alama ba abinda ya sameshi,Kallo daya ya Mata yace makaryaciyar banza,Shuru tayi sabo da ta gaji da kulashi Yana dukanta,da Yamma kwayarsa ta motsa Aamna taga yanayinsa ba mutunci,taja mutuncinta tana zaune a Palo Siyama ta kwada Sallama,tana shigowa Ahmad ya daka Mata Tsawa yace koma inda kika fito,da sauri ta juya ta fita,Ya zaka koreta?Aamna ta tambaya yace ke wallahi idan Baki daina min magana ba Zan sa wuka na Miki yankan rago,Aamna Jin irin kashen kashen rayuka da akeyi yanzu sai ta tsorata tayi sama da sauri kayan sawarta akwati biyu da duk wani abin bukata shi ta kwasa tayo kasa,Murna wajen Ahmad ba a magana,ko kulashi Bata Yi ba tayi waje,da kanta ta Bude gate sabo da me Gadi baya Nan,Tana fita Napep ta Shiga da kayanta sai gidansu.

Su Mama suna ganinta sun San ma matsalar,Baba yace ya Koro ki ne? Aamna tana Hawaye Tace a'a nice Naga bazan Iya Zama ba Yana min barazana da rayuwata shi yasa na taho Kawai,Mama Kamar gaske Tace Allah sarki kiyi Hakuri komai zai dai daita,dama nasan wannan

ba abin yarda bane,karki koma ko Iyayensa sun zo Kuma ko me za ayi karki koma,Aamna Tace dama bazan koma ba,kin San shagona yanzu sai kici gaba da kular min da shi kawai sai na sallami Yaron ciki,Aamna da murna Tace Kinga na huta da zaman Kawai,Mama Tace ae kina hada hadarki da customers me ya dameki da wani banza,Zauna ki huta sai gobe ki fara zuwa cewar Baba,Allah sarki Aamna sai murna takeyi.

Washe gari kuskuren Aamna da su Baba sun Aamna matar aure da igoyoyi a kanta Bata nemi Izni ba ta shirya ta nufi kantin Mama,Yaron Dake ciki shi ya nunawa Aamna komai yanda abin ke tafiya sannan ya tafi gida shi dadi ma yaji sabo da Mama Bata biyansa Hakkinsa yanda ya kamata sai wahala a banza,Wayar Aamna ce tayi Kara ta duba sai taga Mummy ce,Sai lokacin ta tuna da Aurenta,dagawa tayi Suka gaisa sannan Aamna Bata boye ma Mummy ba ta fada mata komai,Mummy cike da damuwa Tace kinyi kokari Aamna bazan ce ki koma ba,na hakura kiyi zamanki Kawai Ina Jin Ahmad bashi da rabon shiryuwa,Zan ci gaba da Masa Addua,to Mummy Maganar fita fa?ko naje ya bani takardar saki,Mum Dariya tayi Tace karki nemi saki Ni na Baki Izni ki fita duk inda ya Dace Amma ki kula ki Kama kanki ki sani da Aure a kanki,to Inshaallah cewar Aamna sannan Suka Gama waya ,Siyama ta Kira ta Bata labari,Siyama sai murna Tace kinyi dai dai wannan shine magana karki sake ko da Wasa ki koma,ai dama bazan koma ba cewar Aamna kin ganni Ina kula da shagon Mama,Kinyi dai dai kawata Nan suka Sha Hira sannan suka kashe Wayar,Aamna Ana zaune a kujera ga table da kayan aikinta na calculation,Haka ta kwashe kwana Uku tana zuwa Kantin ta Gama Gane komai tana ta ciniki.

Ahmad kuwa Bayan Aamna ta bar gidansa shi Bai ji wani damuwa ba ko a jikinsa,ci gaba yayi da shakatawarsa musamman da ya samu Mummy bai ji ta Masa fada ba,Su Mashkoor suka dawo gidan suka tare kullum sai shaye shaye sukeyi,Ranar da Aamna ta cika sati Daya cif da barin gidan Ahmad ya fito a machine a hankali Yana tafiya a nutse,Aamna ta fito kenan tana aunawa wani yaro barkono karaf suka hada Ido da shi zai wuce,Ido ya tsura Mata itama Haka ya Mata kyau da yawa,Machine dinsa ya karawa wuta ya bar wajen,fasa zuwa yayi inda yayi Niyya ya koma gida abinsa,tunda ya dawo Aamna ce ke Masa gizo a fuskarta,Kawai fuskarta yake tunanowa,Tsaki Yaja ya shige Bedroom dinsa ya kwanta Nan take bacci ya kwashe shi,Mafarkin Aamna ya Shiga Yi suna zuba soyayya tana jikinsa a kwance.

A Matukar zabure ya farka Shuru yayi Yana tunani,yace ah....wannan wanne irin tsafi ne? Gashinsa ya girgiza Kamar Yana korar kuda Haka yake karkade Fuskarsa Yana masifa ki bar Fuska na daina ganinki,a'ahhh.....ki daina fito min a Fuska Ina kallonki,wannan wanne masifa ne Haka?.....Ni.....ya nuna Kansa da yatsa ni Zan zauna Ina tunanin mace,kamata Ni a'ahhhh....chaiiii......mikewa tsaye yayi ya kaiwa Iska Naushi yace Zan fasa Miki Baki fa......shi kadai yake ta abinsa a bedroom kamar sabon kamu,Zama ya sake Yi sai Kawai ya tafi tunanin Aamna...Tsaki Yaja yace again....Wai wannan wacce irin yarinya ce ki fitar min daga ido na daina ganinki....kasa ya sakko ya durkusa ya daga hannaye sama Yana Allah ka gani dai Yarinyar Nan sai Tunaninta nakeyi,Ina ta ganinta a Ido na,bazan Iya ba....nasan ni me laifi ne a gareka,nayiwa mutane da yawa laifi Allah karka Yi Fushi Dani ka jarabce Ni da yarinyar nan,Allah kasa na daina ganinta,Allah na tuba,ya Mike tsaye ya sake juyowa da karfi Yana

tangadi yace Allah nayi Addua Kuma ban daina Tunaninta ba,kirjinsa ya dafe tare da furta wayyooo....my Heart woooo ....Ina ta ganinta fa ya Allah,Ya girgiza Kansa ya shiga zaga dakin Yana safa da marwa Yana Ohh....ohh.....Ni ta fita daga Ido na,ta fitaaaa.....a Haka ya yini Yana sambatu har dare yayi Bayan ya jero sallolinsa na yini Guda yace Bari na kwanta bacci da wuri ko Zan daina ganinta a idona,Yana kwanciya ya kasa bacci sai tunanin Aamna tana Masa gizo,Shi kadai yace kunga yau bazan iya bacci ba sai tunaninta yau an shiga Uku.....mikewa yayi zaune yace kaiii....yau bazan Iya bacci ba sai na ganta....naji idan ban ganta bazan samu nutsuwa ba,...Amma Bari naje na ganta nasan idan na ganta zan daina ganinta a idona...waiiii....ya akayi ne nake so sai na ganta,Kawai so nake Naga Yarinyar Nan yanzu yanzu,Kawai gidansu Zan tafi yafi sauki ai Zan Gane gidansu ko na Kira Mashkoor ya raka Ni gidan sabo da ai sunje daurin Aure zasu Gane gidan,a hankali yace Amma idan na Kira Mashkoor asiri na zai tonu Kuma na Gama kuri da cika Baki a gabansu abin kunya ne a ganni naje wajen mace,macen ma wannan yarinya,Amma fa gaskiya idan ban ganta ba bazan samu nutsuwa ba Dole na tafi,agogon Dake hannunsa ya duba yaga 9pm yace Bari naje ko ta katangar gidan ce na haura na ganta,gashi wani kunyarta nake ji da tsoronta bazan Bari ta ganni ba.

Cikin dare ya dauki pcap ya saka sannan yasa face Mark a Fuskarsa Wai Dan kar a ganshi yaji kunya an ganshi a wajen mace,Musa Wanda jiya ya dawo shi ya bawa key din machine yace Musa zuciyata yau wani Bugawa takeyi bazan Iya tuki ba kaini wata Unguwa,Musa ya karbi key ya hau shima Ahmad ya hau sanye cikin kayan baccinsa wando gajeren da Riga me gajeren Hannu ko a jikinsa Haka Suka tafi,Yana ta nunawa Musa Hanya da kyar ya samu ya gano gidan tunda an taba zuwa dashi sau daya,can nesa da gidan yace Musa ya ajiyeshi,ya sauka yace ka jirani a nan bance ka biyo Ni ba,Musa yace to Oga,Face mark dinsa ya gyara ya bi ta can bayan  gidan,Kamar Biri Haka ya Dane saman katanga Dake Bata da tsayi Haka ya haura gidan su Aamna lokacin Baba ya fito zai rufe gida.

Ahmad ya labe Bai ganshi ba,Baba ya kulle ko Ina ta gidan,Bai San ya rufe kofa da barawo ba,Ahmad yace yanzu Ni ba abin na shigar musu gida ba,Kuma yanzu Taya zata fito na ganta? Ai wallahi idan Zan kwana bazan tafi ba sai na ganta,Yana tsaye har wurin minti goma sai yaga an Bude kofa an fito sai yaga Aamna ce sanye cikin kayan bacci ta fito da bucket,Ahmad ya Kara labewa ya gyara tsaiwa Yana kallonta Yana zuba murmushi yace kalli Hanci Dan Allah me kyau a Nan wajen.....Uhmmm .....Allah yayi baiwa, panties yaga ta Shanya Guda Uku da Bra Guda biyu,Aamna tafi so ta Shanya Rana ta dake su sabo da kashe kwayoyin cututtuka,Bata son Shanya su a inuwa tasan gobe Rana zata dake su.

Ta Gama shanyawa Yana ta kallonta Mama ta fito tace Aamna ki shigo da kujera ciki Tace to,Ahmad yace kaji sunan ma Aam....nah.....my Aamna...no sunan gayu Ahmnaa....Yes...Ahmnna vs Ahmad...A&A kenan a'a wannan Dadi Haka.....kumatunsa ya Mara kadan yace to yanzu Zan Iya tafiya nayi bacci,Zabura yayi yace Kai Nafa haukace,wannan fa hauka ce,Ahmad Ni king Haka Kawai na zauce akan Yar Yarinyar nan,Tsaki Yaja yace Nafa haukace gaskiya....lallabawa yayi ya sake haurawa ya bar gidan,Musa ya hango shi ya taho Yana ta murna Yana murmushi Bai San dalili ba,Machine ya hau Suka koma gida,ranar wani irin

bacci yayi me dadin gaske.

Washe gari Yana farkawa da Aamna ya farka a ransa,Tsaki Yaja yace Wai na ganta ma bazan huta ba...Haba zuciyata me yasa Wai kike min Haka ne,jiya kinsa naje na ganta yanzu ma so kike ki Kara ganinta Baki koshi ba wannan wanne irin tsafi ne Yarinyar Nan tayi min ne,da safe sai na farka da ita Haba which kind juju be that? Ni ba sonta nake ba duk harkar love...love ba ruwana da shi Amma Kuma so nake na sake ganinta Haba nooooo.....ya Furta cikin karaji,Sannan cikin slow Yana yarfe Hannu yace idan na ganta anjima ai shike Nan Kuma sai na huta,ai abin kunya ne kamata Ina son ganin Yar yarinya,zuciyarsa ya dafe yace sai wani tsoronta nake ji zuciyata tana wani bugawa Haka Kawai idan na ganta to daga yau bazan sake zuwa ganinta ba aikin banza,tunani ya shiga Yi yace Naga kamar ma samari na zuwa wajen Baby dinsu da Kaya Decent,to Amma Ni ai ba Baby na bace,Kuma fa sai taji Dadi idan idan ta ganni da kayan hausawa? Murmushi yayi ya koma Gaban Mirror ya duka Yana karewa Kansa kallo ya shafa calabarsa yace gani kyakyawa ai dole ma na birge ta,hannayensa ya Buda a Gaban mirror ya saki murmushi yace chaii....see fine Boy.....oh..oh....baya Yaja sosai Yana kallonsa yace huuuu...Kalar birgewa kaga Kalar birgewa yesss.....Bari nayi wanka, Fuska ya Bata yace to Mene sai wani murna kakeyi zaka ganta aikin banza,Ni wallahi wani banza ne ma akan mace Subhannallahi ya Dan Mari kumatunsa kadan yace Bari na gwada Kalar murmushin da Zan Mata Nan fa ya shiga sakin murmushi kala kala Yana kallon kansa a karshe ya Dan yake kyawawan hakoransa yace ae tsaya dai dai Nan wannan yayi yawwa ae....sai ya wuce toilet.

Tunda ya shiga ciki Yace yau wankan na musamman ne so nake na Kara haske Nan fa ya shiga dirzar fatarsa ba ji ba gani,yace bana wanka da soso yau Zan koma Yi da soso sabo da na fita fes,dubawa yayi bashi da soso,towel ya daura Bayan ya dauraye jikinsa ya fito a Haka daure da towel har wajen me gadi,kudi ya mikawa Musa yace ungo maza ka siyo min soson wanka,karka sake ka dakko min na jarirai me laushi me karfi zaka siyo Wanda Ina wanka Ina Jin radadi,Musa yayi Dariya yace irin namu na talakawa kenan? Karka Bata min time sauri nakeyi Ina da abin yi akan wannan soson wallahi Zan iya sallamarka daga Aiki Matukar baka siyo Wanda zai wanke min fatata sosai ba,Musa ya karba da sauri ya fice,Minti biyar ya dawo da soso me shegen karfi ya bashi.

Wanka ya sake Shiga Yana dirje jikinsa Yana rumtse Ido sabo da zafin soson,Haka ya Gama tas ya fito Yana goge jikinsa yace yawwa Iska tafi shigata Ina Nan Ashe Ina ta cutar kaina da ace da irin wannan nake wanka tun farko ai da nafi Haka haske da Zama Fresh.

Lotion dinsa ya shafa me kamshi ya shiga gyara kitsonsa yace ya kamata nayi sabo wannan kwanansa biyar ya fara tsufa Amma Bari dai naje,sai da ya Gama feshe feshensa sannan ya Bude ma'ajiyar kayansa Yana binsu da kallo yace Suit Zan saka ko me?can ya hango shaddoji da yadika masu tsada da kyau Wanda Mummy ta kawo Masa lokacin da za a daura aurensa kala bakwai,Wata Shadda ya dakko sea Blue Tasha dinki me kyau Hannun dogo me links,Nan ya sa Boxers ya fara kici kicin saka wando Wai Bai iya ba,da kyar da wahala Yana uban Nishi ya saka cif cif shi dinki ya zanu,Singlet ya saka yanda Mummy ta koya Masa sannan ya saka Rigar Shaddar wacce ta Sha guga ga kamshi Shaddar nayi sabo da me tsada ce,calabarsa ya

gyara ya shafe Kansa da man gashi me kamshi Nan take ya dauki sheki,Fuska ya kalla ya matsa baya Yana kallon kansa a mudubi ya hau taje Sajensa da gemusa,fuskar ya goge sosai ya gyara sai gashi ya fito fes da shi,Sarkar azufarsa wata sabuwa ya dakko ya saka,Yana cewa duk da hausawa basa so Amma tana min kyau sai na saka sabo da wannan shine wankan sugar sai da ya Gama ya fesa turaruka masu kamshi,Ya tsaya jikin mirror ya kame a wajen yayi mutuwar tsaye yace ya Ilahi Ashe Haka nake? Dan Allah kalli kyau a wajen Nan ai Dole ma na birge,ya sake kallon kansa yace ah.. ah kalli kyau Dan Allah,irin wannan saurayi ai sai an wanke Hannu daka taba,wani Dan lipgloss na maza ya dauka ya Dan goga a lips dinsa yace yawwa.....Kar Kuma na Zama Dan Daudu Mana ya Isa haka....tsayawa yayi yace to me zance Mata idan naje Kantin nasu? Tunani yayi yace na tuna ma Bari naje,Illar idan na ganta sai naji tsoronta Kuma Haka Zan daure,Fitowa yayi Yana Taku dai dai Yana wani Gadara,yace me kyau sai da takama Nan ya Shiga wata tafiya Yana takama Yana basarwa,Musa Baki ya Bude tunda yake a duniya Bai taba ganin me kyau irin Ogansa ba,Bai taba ganin wankan da yayi ya zuba Uban kyau Haka ba sai yau,Musa yace Oga gaskiya kayi kyau,Murmushi yayi yace Allah Musa?

Musa yace wallahi Oga Kar fa kasa Mata su haukace,Dariya Ahmad yayi ta Jin dadi yace Musa yanzu kana ganin duk wacce ta ganni zan birge ta? Bafa soyayya nake nufi ba Kai Musa Ni kasan ba ruwana da soyayya,Musa ya kalli sama ya nuna sama da yatsa yace Na rantse Oga duk wacce ta ganka sai ta kwana tana tunaninka yau ita da bacci haihata haihata,Machine Ahmad ya hau Wanda Musa ya wanke Masa Shar,a hankali yake tukin sai binsa ake da kallo da gani an San Yafi karfin yawo a Machine ko Ina ya gifta sai an koka.

Aamna kuwa yau wanka tayi ta shirya cikin doguwar rigarta peach color ta lefe ce tayi rolling da mayafi ta dauki hand bag da takalminta me Dan tudu Kalar adon rigar Golden tayi kyau ta dauki bokitin chin chin da takeyi da kanta tana siyarwa a shagon wannan da kundinta takeyi tana samu Yar riba,da kanta ta gyara kantin fes ta shirya komai sannan ta zauna tare da dakko Wayarta tana karanta novel,idan masu siyan Abu sunzo ta Basu ta koma karatunta.

Tana zaune ta dukufa taji machine yayi parking a bakin wajen,kanta ta dago da sauri Jin wani kamshi na daban me Dadi,Ahmad ta gani Wani tafiya yayi da Imaninta ita kanta sai taga kamar yau ta taba ganinsa,zuciyarta ta hau Bugawa da karfi,Kallonsa takeyi ba kyafta Ido tare da Mikewa tsaye,Babu alamun fara a Fuskarsa Yana wani Isa,a cikin ransa Kuma wani kwarjini ta Masa yaji wani tsoronta da shakkarta,duk kwarin gwiwarsa sai ya neme shi ya rasa,jikinsa yayi sanyi a hankali ya taka zuwa gabanta ya tsareta da idanunsa,Itama shi take kallo,can ganin Shirun yayi yawa sai Tace am...me kake so zaka siya Ahmad? Yayi Shuru ya kasa magana,ta kalle shi tayi murmushi Tace wow kayi kyau Wannan shigar tayi maka kyau,Wani sanyi yaji a ransa dama Dan ita yayi Kuma ta yaba,a hankali yana Ina Ina yace shi...shigar...ta...tayi Miki?da sauri ta daga kai Tace sosai wace zata ce ma baka Yi kyau ba,Yaji wani Dadi ya jinjina Kai kawai,sharewa tayi Tace me zaka siya? Kasa magana yayi sai da kyar yace Uhm....uhmm.....Yana ta kallon shagon Yana so yaga me zai iya siya....gumi ya hada Nan take tsabar abinda yake ji a ransa da kwarjinin da ta Masa gashi Bai Iya yiwa mace magana ba tunda ya taso a rayuwarsa wannan ne na farko,Tace Kayi magana Mana me zaka siya? Yace Uhmm....ahhh....ehmmm.....can ya hango chin chin yace Chin chin tare da nunawa da

yatsansa,murmushi tayi Tace na nawa? Yace na....naira dari.....murmushi ta saki ta bude ta zuba Masa Guda uku dari cif a farar Leda ta Mika Masa,karba yayi Yana ta kallonta yace Zan....Zan...Iya Zama a Nan naci? Tace me zai Hana shigo ciki,kujera fara ta jawo Masa a ciki ya zauna Suka jere taci gaba da karatun Novel dinta.

Kallonta Kawai yake ta faman Yi idan yaga zata dago sai yayi sauri ya dauke Kansa,Daya gaji sai ya fara cin Chin Chin din,harga Allah baya son chin chin Amma Haka yake ta ci Yana kallonta,ita Kuma tana ji a jikinta Yana kallonta duk sai ta kasa sakewa da kunya,juyowa tayi karaf suka hada ido,Tace ya kake kallo na? Yace kallo? Kallo Kuma? Ni na kalle ki ai kece ma naga kina ta kallo na tun dazu ya fada Yana dauke Kai,Tace Ni nake kallonka din? Yayi Murmushi yace ae Mana,Kai ta girgiza taci gaba da karatunta,cikin Wayar ya leka yace me kike karantawa? Novel ta bashi amsa, ko kana karanta Novel? Yace No...me zanci da Harkar love ai Ni sai dai dambe, murmushi tayi Kawai.
Yace me yasa Mata kuke son Love ne? Wannan duk Bata lokaci ne,Dariya tayi Tace Kai baka so ta juyo tana murmushi wani kyau ta Masa ya gigice zuciyarsa taci gaba da bugawa,kasa magana yayi ya rike Hannunta wani mugun shock taji ko Ina a jikinta yace Ring din ya Miki kyau,Tace na gode Hannunta ya dauka ya maida Mata saman cinyarta yace kina boye Hannun Nan Kar wani yaga ya Masa kyau da yawa ya yanke Miki shi ya tafi dashi gida,Dariya ta dinga Yi shi kuwa ita Kawai yake kallo,komai nata Dariya a ransa ya furta,Yana sani ya dinga cin Chin Chin din kadan kadan sai da ya Dade lokacin Azahar tayi sannan ya Mike yace Zan tafi Tace ka Gaida gida yace to Zan fada Masa,Dariya ta sake Yi ta rako shi har bakin machine dinsa ya hau ya tafi da mugun gudu,Tun kafin ya karasa gidansa ya tsaya a Hanya ya cire rigar Shaddar tasa sabo da zafi yake ji ta dame shi Bai Saba ba,a kafada ya sakale ta har zuwa gidan.

Da murna ya shiga Yana sauka a machine ya zaro dubu biyu ya damkawa Musa yace je kaci pizza Musa yau Ranar murna ce,Musa yace Allah Oga? Allah kuwa cewar Ahmad ya sake zaro dubu biyu yace kudin lemo ne wannan,Musa ya daka tsalle Yana murna da Ihu har Ahmad ya tafi ya sake dawowa ya zaro dubu Daya yace ungo Musa ka sawa matarka Kati a waya ku kwana kula hirar ku ta Yan karya Kuma karka sake ka Bata duniyar mu Dan Bamu San Inda zamu shiga ba idan ka bata.,,Musa yace Allah Kai sai kayi,Ahmad ya daga hannaye sama yace nine nan yayi ciki Yana wata tafiya ta musamman.

Yana shiga ya cire duka kayan jikinsa ya watsa su a inda yake Tara wanki,saitin zuciyarsa ya dafe tare da furta shu'uma har ta dawo dai dai,Wato har wani bugu kike Yi a hankali da kika ga bana gabanta ai shike Nan kin kyauta,zuciya kin kyauta hakan ya Miki kyau kin Mai Dani wani Wawa Akan yarinya karama Ina ta zubar da aji na ai shike Nan Zaki sani ne.

Washe gari ma wani sabon wankan yayi tare da saka wani yadi Milk color sharara da shi ya Masa kyau matuka an kashe shi da dinki na haduwa,wani takalmin ya zabo me tsada,waje ya fito ya mikawa Musa takalman yace sauri ka kaiwa Shoe maker ya wanke min yanzu Ina jira,Dan Allah Musa kayi sauri ka kawo min su Suna kyalli,Musa ya fita da gudu ya tafi Bai Dade ba ya dawo,Ahmad ya shirya tsaf kyau ba a magana yace yau barkono da citta Zan tayata siyarwa,yau ma Aamna tana zaune ta Gama sallamar wani ya siyo Singlet sai gashi ya Parker

machine,Aamna tayi murmushi Tace Sannu da zuwa,Irin Dan gayun Nan harda wani basarwa Direct ya shige ciki ya zubawa Kansa chin chin yace na Naira Dari biyu yau Zan siya Aamna Tace to,Zama yayi Nan ma Yana kallonta duk kunya ta isheta,Wani magidanci ne yazo yasan Ahmad da irin iya shegensu mamaki ya kamashi ganinsa a Haka da wannan shiga ta Kaya,Bai taba ganinsa da shigar hausawa ba,Kuma Yana Zaune a shago kamarsa me kudi,Shuru yayi yace a bani barkono da citta,Aamna ta Mike zata zuba da sauri Ahmad yace No zauna Bari na tayaki Mana Haba,Tace Kai din? Bai kulata ba yace na nawa? Yace na Hamsim,Aamna tace ga kullin Hamsim can ka saka,ya dauki bakar Leda ya saka Masa ,Citta Kuma Tace gongoni Daya zaka zuba,ya fito ya auna gwangwani Daya ya zuba,mutumin yace babu gyara? Ahmad yace a gindinku kuke so mu kare ne Ina laifi ma duk arahar Nan Baku gani ba,Tsaki Yaja ya dauki citta Daya ya jefa masa a Leda yace gashi Nan anyi gyara,Mutumin ya karba ya tafi shi Kuma ya dawo ya zauna a ciki,Aamna tana ta mamakinsa.

Wata Budurwa ce tazo Tace Aamna nazo siyayyar,Aamna Tace to shugo,Budurwar tayi layin bra da panties ai Ahmad Yana ganin Haka sai ya juya baya tare da rufe Idonsa ruf har sai da matar Nan ta Gama zaba ta biya kudin ta tafi sannan ya Bude Idonsa,Dariya ya bawa Aamna Yana jinta tana ta dariya,yau ya Dade sai Yamma lis ya koma gida,sai mamakin Kansa yakeyi Wai Kamar shi shine zai siyar da citta,Yana kwance a palonsa yace gaskiya na Gama fadowa nayi asara wallahi,Kansa ya dungure yace kayi asara kai Kam Ahmad.

Wasa Wasa kullum Ahmad sai yaje ya Taya Aamna siyar da Abu har wurin sati Daya,gaba Daya su Mashkoor sun daina ganinsa,idan sun Masa waya ma zasu zo gidansa sai yace Kar suzo baya gida ya tafi Unguwa,yafi so ya zauna shi kadai yayi ta tunanin Aamna Yana Jin dadi,Kwaya da giyar da yake Sha duk ya rage ba sosai ba sabo da tunanin Aamna.

Yau kin zuwa yayi gaba Daya Bata ganshi ba har duba Hanya takeyi ko zata hango shi Amma Shuru duk ta kasa sukuni ta shiga wani Hali,gashi Bata da number dinsa Kuma baza ta iya cewa ya Bata ba.

Sai washe gari yau cikin wata maroon suit ya fito kamar a jikinsa aka dinka yayi kyau matuka 3pm yazo wajen,Aamna ta taso da sauri tana murna a ranta a fili Tace me ya hanaka zuwa jiya? Ya rasa me zaice zuciyarsa tsoro yake ji....yace...ahmm...karya yayi yace kaina ke ciwo jiya,Tace Eyya Sannu ya jikin? Da sauki ya furta tare da tsayawa a gabanta Yana so ya fada Mata me yake ji a ransa Amma ya kasa....yace dama Ina so muyi wata magana ne,akwai abinda nake so na fada Miki,Aamna tace Ina jinka tana ta faman kallonsa,kasa fada yayi ta Masa kwarjini sai ya waske yace kina cin kifi tarwada? Dariya ta kamata Tace sosai ma ai Ina sonsa ya,girgiza Kai yayi Murmushi Wanda ya tafi da Imanin Aamna,yace to gobe Zan kawo Miki da yawa ko yau kike son ci? Aamna Tace goben ma yayi,Yana so ya fada Mata shifa zuciyarsa ta kasa sukuni Amma ya kasa sai yace Zaki Zama kawa ta?Aamna ta kalle shi tace me zai hana,murmushi yayi yace to daga yau mun Zama kawaye ko? Tana Dariya ta Mika Masa Hannu sukayi musabiha Tace na Zama kawarka kaima ka Zama aboki na,yace ae dama Ina so na dinga shawarwari Amma Banda kawa,Aamna Tace Ina abokanka fa?Tsaki Yaja kadan yace ai Bama wani haduwa yanzu sosai,taji Dadi a ranta Tace to shugo ka zauna,no tafiya zanyi Ina da wajen zuwa yau,Aamna Bata so hakan ba Amma Tace to shike Nan sai goben,ya hau machine yayi tafiyarsa gidan Mashkoor.

Yana zuwa ya samu Mashkoor shi kadai, Mashkoor yace Kai me Zan gani yau Kaine da wannan shigar lafiya king? Kafadarsa Ahmad ya buga yace ba lafiya ba yanzu ma taimakonka nazo Nema,ku kawo min agajin gaggawa, ka tashi mu tafi gidana akwai magana,Mashkoor yace to,Giyar da Mashkoor yake kurba ita Ahmad ya tiltila a cup ya Sha ya sake Sha yace muje,a machine suka tafi gidan Ahmad.

Aamna tana so ta fada Masa anjima da yamma zata tafi Sokoto ganin Dangin Babanta Amma Bai zauna ba bare ta fada Masa Amma sunyi waya da Mummy ta San da tafiyar.

Shi kuwa Mashkoor Yana palon Ahmad suna zaune Ahmad yace kasan Kai abokina na ne Zan fada maka ne Kawai sabo da yanda muke da Kai,Kai kadai Zan fadawa halin da nake ciki,Mashkoor da muryar Yan kwayarsa yace Ina jinka King,Ahmad ya kwashe kaf abinda yake ji a zuciyarsa game da Aamna ya fadawa Mashkoor,Mashkoor tsoro ya kamashi Yaja da baya Yana tangal tangal a zaune yace Sarkin namu Guda ah'ah,Ahmad cikin rada yace Ina fada maka idan na ganta zuciyata sai naji tana wani kida tana rawa tana wani foli..fafo..lifo...fil...fil....dardariya Mashkoor yake Kamar me,yace ah'ah duk Kai kadai?

Ahmad yace Ina fada maka Dan uwarka Yana dukan kafadar Mashkoor kana ganin Wasa ne bafa Wasa nake ba kana wani Yi min Dariya Dan Iska Kawai wallahi zaka bar gidan Nan, Mashkoor yace na daina Ina jinka,Ahmad yace Ina fada maka ba sai naji Ina tsoronta ba,Ah'ah Mashkoor ya furta da karfi yace wannan Yarinyar da ko Nonon kirki babu? Duka Ahmad dirka Masa a baya yace be careful matata ce ba Budurwa ba, Mashkoor yace dalla ba so bane sha'awarta kakeyi Kawai kaje ka dakko ta ka lallabata kaci abinka ka barta,Wani dukan Ahmad ya kaiwa Mashkoor yace Kai dalla Ni ba wannan nake so ba,baka ganewa Ni Kawai nafi so mu zauna tare da ita idan Dan wannan ne zamu iya shekara Nawa da ita sai Sanda take so zanyi wannan fa ba Maganar Wasa bane,Mashkoor yace cab abin Babba ne asiri tayi maka,Haushinka taji daka koreta ta maka asiri.

Ahmad yayi Shuru,Mashkoor yace Zan taimaka maka akwai wani malamin Baban mu zamuje da Kai Nan take zaiyi maka Rukiyya a cire maka tunaninta ka dawo normal asirin data maka ya karye,Ahmad sai ya tuno layoyin Daya taba gani a Kan Aamna,yace Mashkoor kaima kayi magana tashi mu tafi wajen malamin Nan Yarinyar Nan Yar bori ce muje a gwada, Mashkoor yace yawwa kasan yanzu duniya ta canja Wai Yan Mata Dan masifa da bin malamai suna shirka suna tsafi akan maza,Wai mace taje tayi shirka Dan wani ya aure ta ko taci kudin wani,wata ta mallake Miji etc,kawaye sai su cika Mota suyi Kauye Wai an tafi wajen Malam akan wani ya aure su ko taci kudi,ko ayiwa kishiya da yaranta,shi yasa aure yanzu baya Zama Ana ta Yi Ana Sako Mata barkatai,duk macen data auri Namiji da asiri ta sani wallahi idan ya karye sai saki,yanzu shirka Kawai akeyi an ma daina cewa malamai sai bokan Kan dutse,mutane suna ta maida kansu arna Basu Sani ba.

Tafiya sukayi me uban nisa zuwa wani Dan Kauye,Wani dattijo kazami Ahmad ya gani,Mashkoor bayan sun gaisa ya Gabatar da Ahmad da abinda ya samu Ahmad,tsohon yace ku bada dubu biyar kafin alkalami,Ahmad ya zaro ya bawa Malam,Malam yace saura kudin Aiki dubu goma,Ahmad yace Aiki baiyi ba za a baka kudi? Dattijon yace Kai ka cika son kudin tsiya

ka bada kudi a rabaka da masifa,ciwon so ai masifa ne,Ahmad yace Nifa ba soyayya nakeyi ba,nace maka tunaninta Kawai nakeyi,Ni nayi love Allah kiyaye, gashi nan yarinyar ta Gama kashe maka zuciya cewar malam,Ahmad ya bada dubu goma shi Sam da gani yasan karya ne wannan cin kudi Kawai zaiyi.

Saman Tabarma yasa Ahmad ya zauna,Bayan ya zauna ya Bude Qur'ani ya dinga karatu a Kan Ahmad Yana zaga shi sai da ya Dade sannan yace an Gama Alhmdllh Aiki yayi kyau kuje gida daga yau ka Gama da shafinta, Mashkoor Yana murna ya dinga godiya,Ahmad Baki ya tabe shi baiji canji a ransa ba,Sai dare Suka koma gida,suna dawowa wanka sukayi Suka ci abincin da Suka siyo a hanya,Ahmad ya kalli Mashkoor yace Mashkoor Nifa so nake yanzu Naga Yarinyar Nan,Da mamaki Mashkoor yace ah'ah Kuma dai? Yanzu duk aikin da Malam yayi har kanajin ta a ranka? Ahmad yace tashi ka rakani gidansu Zan haura katanga idan ban ganta bazan iya bacci ba yau dole sai naji muryarta ko na ganta,Mashkoor yace dare fa yayi ka duba lokaci 11pm fa,idan zaka rakani to idan baza kaje zanje Ni Daya,Dan kaga Ina fada maka sirrina zaka wulakanta Ni,Mashkoor yace muje Amma idan munje me zaka ce da su a wannan Daren me zamu ce? Ahmad yace muje Kawai,machine suka hau a daren Suka tafi Kamar mayu.

A bakin gate Suka tsaya tare da kwankwasa gidan,Baba ne ya fito Jin bugu yaki karewa Yana budewa tsoro ya kamashi ganin su Ahmad ya tabbatar giya suka Sha shi yasa Suka zo da wannan Daren yasan basa hayyacinsu,lafiya? Baba ya tambaya,soshe soshe Suka Kama Yi, Mashkoor yafi Baki shi yace dama...dama..munzo duba Aamna ne sabo da munji labarin Bata da lafiya,Baba yace sabo da kwaya ta gaya muku karya sai kuzo min gida a wannan daren? Kun firgita mu Ni da matata,to Aamna Bata Nan ta tafi Sokoto tun yamma dazu tace ta sauka tana can Dangin Babanta sai Nan da kwana hudu zata dawo,Kirjin Ahmad ya buga Kamar zaiyi kuka yau bazai iya bacci ba Matukar Bai ji muryarta ba,Baba zai juya yace sai da safe da Sauri Ahmad ya kalli Mashkoor ya Masa rada kace ya Bamu number dinta,Da sauri Mashkoor yace Dan Allah  Dan Bamu number dinta Muna so muyi Mata ya jiki,Baba yace Wai uban waye yace muku Bata da lafiya fatan ba takura Mata zakuyi ba,da sauri Ahmad yace a'a Kawai Sannu zamuyi Mata,Baba ya Harare su sabo da Bai so Haka ba Amma sabo da kwarjinin Ahmad yace bani waya na sa maka,da sauri Mashkoor ya Mika wayarsa Baba ya sa Masa number a ciki Yace kuje garam ya rufe gidan,Ahmad ko a jikinsa sai murna Suka hau Machine suka koma gidan Ahmad.

A Palo Ahmad yace Kira ta awaryarka muji, Mashkoor ya kalle shi da mamaki yace da wannan tsohon Daren? Ahmad yace Dan Allah ka kirata naji muryarta Ni bazan iya Mata magana ba zuciyata bugawa takeyi,kayi magana da ita kasa a handsfree idan naji muryarta shike Nan Zan samu nayi bacci yau,Amma Matukar banji muryarta ba yau bani ba zaman lafiya, Mashkoor yace abin har ya Kai Haka mun shiga uku?Tsaki Ahmad ya ja, lokacin Aamna ta kwanta ta fara bacci taji Wayarta tana ta Kara,dubawa tayi taga bakuwar Number

AsmaBaffa
10/26/21, 8:53 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

46-50

FREE PAGE

DUNIYATA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

NA KUDI NE

MASU SHIGA GROUP DARI BIYU 200 NE

ACCOUNT NUMBER
0175487861
ASMAU GARBA MUHAMMAD GTBANK

MASU TURA KATIN MTN KO VTU GA NUMBER
08033933642

YAN NIGER KU NEMI WANNAN NUMBER
+227 90 79 59 39

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne

RUKEY MUAZ
LEEMAT
~-
MINERH

KHADIJA DANDAWAKI
HUMAIRA MUHAMMAD
AMINA ADAMU USMAN

Tsaki taja tace waye wannan da wannan daren? Kin dagawa tayi har ta katse, Mashkoor ya kalli Ahmad yace King Bata daga ba a kyaleta tayi bacci,da masifa yace ka Kara kiranta Mana,to tana bukatar tayi bacci fa cewar Mashkoor,Bata bacci da wuri na sani ka sake Kira Wai me yasa kake min Haka Zan sa ma poison a lemo ka Sha ka mutu ka kirata again, Mashkoor yace Nifa baza ka Jani cikin haukarka ba,Kawai ka shigar Ni ciki mun haukace yau gaba Daya bansha ko kwalaba Daya ba mun Kare akan kwaila,wata Harara Ahmad ya aika Masa Nan take Mashkoor ya sake Kiranta lokacin wata Budurwa Yar Uwar Aamna Minal ta kwanta a gefen Aamna Tace Wai waye yake ta Kira ne Haka? Aamna Tace ban sani ba,Bari na daga naji cewar minal ta dauki Wayar tare da dagawa, Mashkoor yace an daga....an daga...Ahmad yace ehem Yi magana Mana.

Mashkoor yace hello Aunty Balaraba Mashkoor ne? Minal tace ba ita bace Yar uwarta ce Minal ce,Aamna tana ji ance Mashkoor ta Mike zaune,Mashkoor yace ehem Dan Allah Bata kusa me Wayar? Minal Tace gata ma Bari na Bata, Wayar Aamna ta karba,Lokacin Ahmad ya gyara Zama tare da furta ehem a hankali, Mashkoor yace Aunty Balaraba Barka da dare,yawwa Mashkoor ya gida? Lfy Alhmdllh,dama...dama...Ni da King munje gidanku ance bakya Nan kinyi tafiya,Aamna Tace Yana Ina King din,Tsoro ya Kama Ahmad shi Taya zai iya magana me zai ce Mata, Mashkoor yace Bari na Baki shi ya mikowa Ahmad Wayar.

Yana karba sai da yayi minti Daya Aamna tana ta faman hello hello sannan yace hello cikin Muryarsa da ya saita me Dadi ta nutsuwa....uhm...ahm...ahhh....munje gidanku dazu ance bakya Nan? Aamna Tace eyya sorry Friend Ina ta so na fada maka Bamu hadu ba Amma jibi Zan dawo Inshaallah,Ahmad yace okay...Allah ya kaimu, Mashkoor da rada yake cewa matarka ce fa ka daina wannan abin taya zaka barta tana tafiya inda taga dama Haka? Ahmad Bai kulashi ba yace Friend sai da safe Bai San me zai ce ba,Tace okay bye ta kashe Wayarta,Ahmad yace Nifa ba Maganar Mata nake maka ba ya za ayi Naga na birgeta shine magana Kawai,Dariya Mashkoor ya dinga yi yanda Ahmad duk yake ta murna akan yaji muryar Aamna,yace to yanzu Zan iya bacci,Mashkoor yace ka haukace Nima ka sani na Zama

mahaukaci,Bari naje nayi bacci,Ahmad yace ungo wannan banzar akwakwar Wayar taka tunda nadauki number dinta,Ae ai dole ka zagi Wayar tunda ta Gama biya maka bukatarka.

Washe gari da sassafe Ahmad ya farka ya dawo Palo inda Mashkoor yake bacci ya dinga dukan Mashkoor a gadon baya,da kyar Mashkoor ya farka Yana masifa Wai Dan Allah mene Haka jiya ka hanani nayi bacci yanzu ma Haka Mene ne? Baka tashi da wuri mene yanzu abin tashi again,Ahmad yace Yarinyar Nan nake so ka kirata ku gaisa sai ka sa min Wayar a Handsfree naji muryarta,Tsaki Mashkoor Yaja da muryar Yan kwaya yace wai a'ahhh....wannan wanne bala'i ne Haka? Okay kace min kawarka ce Kai ba sonta kakeyi ba wa yace maka Ana Kiran kawa Haka a waya,so kake Yarinyar Nan ta tsaneka sabo da yawan takura Haba su Mata basa son takura,kana nutsuwa fa King,Shuru Ahmad yayi yace okay Bari to bazan kirata ba sai ta neme ni Zan daure,Ehemmmm...Abeg jeka kitchen ka Mana girki King kasan ka iya girki cewar Mashkoor.

Ba karamin dauriya Ahmad yayi ba yaki Neman Aamna a waya,Aamna taga Shuru Bai nemeta ba ranar da ta dawo Kaduna yau Ahmad Yana kitchen shi da Mashkoor suna magana Yana girki sai ga Kiran Aamna ya shigo wayarsa,Wata nutsuwa Ahmad yayi tare da cewa yeee...ta Kira ni...daga Wayar yayi yace Hello.....Kawata,Aamna Dariya takeyi Wai Dan rainin hankali ma ba matarsa bace kawarsa ce ma,a Wayar Tace dama fada maka zanyi na dawo dazu,Wata Uwar Zabura Ahmad yayi sai da Mashkoor ya firgita,Ahmad yace Kin dawo lafiya Kamar Yana gabanta har wani zufa yake Yi,Tace Ify Alhmdllh,yace Zan zo gobe,okay Aamna ta furta ta so ace yanzu zai zo Amma Wai wani gobe, Wayar ya kashe ya saki Dan Ihu yace she done come back Yana dukan kafadar Mashkoor, Mashkoor kallon mamaki yake Masa Kawai ganin king dinsu ya haukace.

Wanka sukayi Mashkoor ya dauke shi Suka tafi Shopping Wai Ahmad shaddoji zai siyo da yadika masu tsada za Masa dinki sabo da ya birge Aamna.
Ko da Suka shiga inda ake siyar da shaddoji da yadikan maza Ahmad ya kalli me kayan ya zaro Masa Ido yace Guy Kalar birgewa muke bukata masu tsada,Me Shadda yace gasu Nan ku zaba,Ahmad ya dinga zaba Mashkoor ya koma gefe Yana ta kallon ikon Allah har ya Gama sannan Suka wuce wurin tela,Ahmad yace Kai tela fa Wanda yasan me yakeyi yawwa idan kasan tela bana kirki bane karka kaini, Mashkoor Yana ta Dariya yace Wai Ni Kam ko Lilamin Masallaci za'a nada ka ne? Ko kula Mashkoor Ahmad baiyi ba,wani Shagon dinki Suka shiga,Ahmad yace Bari na gwada basirarsa Kai tela nawa zaka min Dinki na karshen tsada? Tela yace dubu bakwai, dubu biyar dubu goma sama da Haka,Ahmad yace wannan dinkin da gani bana arziki bane baka iya komai ba baka San me kakeyi ba Malam ja can dalla, mu bar Nan, Mashkoor ya sake daukansa Suka tafi Wani wajen na masu tsadar dinki Amma da kyau,Ahmad Yana ji an zuga Masa tsada yace yes.. .yanzu nasan Kai telan kirki ne Nan ya bashi kayan,yace auna Ni ko Ina dai dai Ni, wallahi ka min hauka sai na sa an kone shagon dinkinka da kayan ciki sabo da Haka don't Mess up,tela yace zaka ga Aiki ai bana Wasa,sai da suka Gama komai Suka je ya siyo takalma Designers da agoguna etc.

Sai dare Suka Gama sannan Mashkoor yace Zan tafi gida,da masifa Ahmad yace akan me ai

wallahi ba inda zaka je Sai an Gama tsare tsare da Kai, Mashkoor yace Nifa na gaji Haba ka rike Ni na kwana na yini Yar giyar ma ban Sha ba tun jiya Ni bazan iya ba, baza ka saka Ni a wannan haukar ba,Fuska Ahmad ya Bata tare da furta Kai meke damunka ina magana kana magana are you mad?

Shuru Mashkoor yayi yace to kayi Hakuri na zauna Amma a kawo min ruwa da kayan aiki,Nan Ahmad ya koma bedroom dinsa ya kwaso kayan shaye shaye ya ajiye musu Suka dinga Kora abinsu,Ahmad Yana murmushi yace yawwa na tuno nasan dole tana yin Facebook babu Wanda baya Facebook a duniya,Nan take ya fara latsa wayarsa Yana duba Facebook Yana Searching sai dai Bai San sunan Baban Aamna ba,Amma sai ya gwada Aamna Hussain,Nan take sunan Aamna ya bayyana da hotonta,Yana murmushi yace Yes....see fine Beb,see Beb....naaa..wow...see her lips...oh.....My God...a'a...kaga kyau Haka,...fuskar Wayar ya shiga nunawa da yatsa Yana shafa gemunsa Yana murmushi yace abinda kike min baya dacewa,bakya kyauta min Sam,ki daina...ki daina Tam.....Mashkoor ya saki Baki Yana kallon ikon Allah, Pictures dinta ya shiga dubawa kala kala can ya hango Aamna da wani saurayinta a pic Wato Affan,Glass din wayarsa ya shiga Rankwashi da karfi a saitin Affan Yana ka...ga...shege...Dan... Iska,me yasa zaka tsaya kusa da ita....mugu....Tsaki Yaja ya fita daga Facebook din gaba daya Yana Fushi yace Taya zai tsaya a kusa da ita aikin banza,Cikin Maye Mashkoor yace Wai...Wai...ba kace kawarka bace?Yeah Ahmad ya furta,yace to Mene na damuwa Haka? Maganar gaskiya King ka fa haukace.

Ahmad Yana Zaune yayi Shuru Mashkoor yace ya akayi ne? Yarinyar Nan nake so na gani yau da Daren Nan Amma bana son ta ganni kuma bana so ta San na ganta Kawai na ganta a boye ba tare da ta ganni ba,kaga yanzu 10pm muje ka kaini sai na tsallaka gidan, yau ko bacci takeyi har dakinta sai na ganta,Mashkoor tsoron Ahmad ya shige shi Kamar zaiyi kuka yace Wai Mene yake damunka kafa haukace King,Kaga Idan zaka kaini Malam ka kaini Zan zuba ma guba a abinci ka mutu Tam, Mashkoor yayi Dariya irin ta yan kwaya yace muje,a daren Suka hau machine suka tafi,a nesa da gidan Mashkoor ya sauke Ahmad,Ahmad yace karka tafi Ina ganinta Zan fito mu wuce,ta Kofar gidan Ahmad yabi ganin a bude Basu rufe ba,kamar barawo Haka yake Sanda yace bana so ta San Zan kalle ta,da sauri yabi ta bayan gidan wajen Flowers,Baba ne ya fito Yana masifa Dan Iskanci sai a bar gida a bude tun yaushe nacewa shedaniyar Yarinyar Nan ta rufe gidan Nan Amma dake Aamna ba Yar Albarka bace ta bar gidan Abude,Ahmad Yana ji Baba ya zagi Aamna sai ya kasa jurewa Yana bayan ginin gidan yace karya ne kaina Mara Albarka.....tsorata Baba yayi ya rasa a Ina yaji an ramawa Aamna ya shiga waige waige ko zai ga mutum baiga kowa ba,Tsoro ya kamashi ko aljanun Aamna ne suke tare Mata fada,da sauri ya rufe gidan ya kulle ko Ina ya koma ciki da saurin gaske.

Ahmad ta Kofar kitchen yabi Dake kitchen akwai kofa ta waje ta ciki sai yabi ta Nan ya shiga Palo Yana shiga Baba ya shigo da sauri ya fada bayan kujera ya buya,Baba Yana masifa ya kulle Palo ma ya sa key, yace aikin banza kitchen dinma a Bude aka barshi Bari na rufe,kafin ya karaso Ahmad da rarrafe ya koma Bayan Daya kujerar,Baba ya kulle kitchen Yana cewa beraye sun fara addabata a Palo naji Kamar sun shiga cikin kujeru Bari gobe da wuri Zan samo mage tayi maganinsu.

Ahmad Yana ji a hankali yanda Baba bazai ji ba yace Baba nine ba bera ba,Baba dai dakin matarsa ya shige,Sai ga Aamna ta fito sanye da wata guntuwar rigar bacci fara silk me siririn Hannu,Ahmad ya baza Ido Yana kallo Nan ma a hankali yanda baza taji ba yace Kai bakya kyautawa Baba fa idan Yana ganin irin wannan abin sai Shedan ya shiga zuciyarsa,wallahi sai ya Ayyana wani Abu gaskiya ki gyara,ba kishi nake ba Amma ki gyara,Aamna Bata San Yana yi ba taje kitchen ta fara dafa Indomie,cikin karfin halin Ahmad ya fito fili ya tsaya a Bayanta tare da Harde hannayensa a kirji Yana Shan kallo,a hankali ya Mika hannayensa biyu tare da wara su yace in Dan tallafooooo......hips Ido ya lumshe,Aamna Bata sani ba harda wakarta tana me so na....me so na....Ahmad Yana amsawa a hankali Yana Nuna Kansa Yana gani...gani....Aamna ji tayi kamar ana magana a Bayanta Matsawa tayi da Niyyar juyowa tuni Ahmad ya koma Bayan jikin bango daga Palo ya labe taga ba kowa,ci gaba tayi da aikinta ya dawo shima Yana ta kallonta har ta Gama ta dauka a plate sai ta tsaya dakko ruwa a fridge ta ebo pure water biyu tare da furta Allah sarki a gidan Mijina kuwa Ruwan Roba nake sha,kafin ta Gama gyara kitchen ta fito Ahmad yayi sauri ya shige Bedroom dinta Wanda yaga ta fito daga ciki.

Bayan labule ya buya abinsa Aamna ta shigo tare da dannawa kofarta key tana Waka Tace yawwa Bari na kwashi harka ta zauna a gefen bed tana ci tana latsa waya tana Dariya,shiko Ahmad ta bayan labule yace kalli murmushi Malam Kamar wata flower Haba ai wallahi Babu Wanda ya Isa ya ja da Allah,wata baiwar Allah duk duniya kowa da kamarsa daban da Computer ce ke kera halitta ai da tuni tayi photocopy na Aamna ta yafi mutum dubu,Amma Kuwa Allah kowa hancinsa daban,bakinsa daban,Dariyarsa daban,kukansa daban,girarsa daban,kafa,Hannu,Kai,komai daban Allah kenan.

Aamna Bata San da mutum ba Tace zafi Bari na sake wanka ba tunanin komai ta tube rigarta ta jefar,Ahmad ya zaro Ido yace tab gaskiya ban kyauta ba Zan kalle mata tsaraici ba Izni,Idonsa Daya ya leko ta labule yace tab Ni idan kika dawo gida na karya ne ki Haifi wani yaro,Ni da yarona zamu Yi takara kenan akan Abu daya Ni da shi ai karya ne,Yarana kuyi Hakuri Uwarku ta ja muku baza kuzo duniya ba akan wannan yaki zanyi da ku,Juyawa tayi yace lahaula fiii......see Ass uhmm....Ganin ta juya baya sai ya juro hannunsa Daya ta labile yace na taba suuu......da sauri ya janye hannunsa Kamar walkiya ganin zata juyo ta kamashi,Towel ta dauka ta shige toilet,sai da yaji karar ruwa sannan ya fito daga inda ya boye,Indomie ta rage yace Bari naci ragowar ta ko na samu karama da tabarakinta ya dauke ya cinye,ruwan data rage ya shanye tas harda tsotse bakin Ledar pure water Wai ya tsotse bakin Aamna,kafin ta fito ta Bude kofa Ahmad ya dauki Wayarta ya turata bakin kofa sannan ya Bude Kofar ya fice da sauri,ta kitchen yabi ya fita tare da haure katanga,ko Ina ya bar kofofin a bude sabo da dabara ya hada.

Aamna da sauri ta fito daga toilet Jin karar key an Bude Mata kofa,mamaki ya kamata taga Wayarta a bakin kofa ita data barta a saman bed,abincinta data rage taga an cinye,da sauri ta fito tana duba gidan sai taga an Bude Kofar kitchen ko Ina,ga handkerchief an jefar,Ihu Aamna ta saki tana Baba barayi,barayin waya Baba,Baba ya fito da Aamna ta nuna musu kitchen,Baba

yace abinda nake gudu kenan munafuka ai ke kika jawo kece ba Kya rufe gidan,Baba yace Bari na duba Naga me aka sace min,startime wacce ake Kamo tashar kallo Baba yaga wayam an sace,Hannu ya Dora a Kai ya kurma Ihu yace dubu goma Sha biyar dita,Radio dinsa da yake Jin labarai itama a Palo ya barta yaga an sace ta itama,Baba Takaici yace me yasa Dan Ubanki ba a sace wayarki ba Aamna? Aamna Tace ai Nima an cinye min ragowar abinci na da ruwa,wayata ma Allah ne ya kiyaye barayin suna bude kofa na fito daga Bayi da gudu shi yasa suka jefar da wayata garin gudu Basu sace ba,Baba yace ai tsafi sukeyi da tsafi suke Shiga gidan mutum ko ka kulle da key a banza,Mama Tace matsiyata Allah ya takaita Suka koma tare da kulle ko Ina.

Mashkoor Yana Kan machine Yana ta jiran Ahmad har 12am ya fara gyangyadi ma Sai ga Ahmad ya fito ta baya da sauri Hannunsa dauke da Radion Baba da Startime din su Aamna wayo ya hada sabo da a tabbatar barayi ne.

Mashkoor ya gano plan din abokinsa ya dinga sheka dariya yace sata har gidan surukai wannan wanne irin Dan Iskan suruki ne? Dariya Ahmad yayi yace yau nayi farin gani,tunda nake a duniya sai yau na kalli Abu mafi kyau a duniya,Duk kasar wajen da kaje? Cewar Mashkoor,Ahmad yace ai wannan duk ba kallo bane,Basu da komai me kyau,ai Country me kyau Yana jikin Aamna,Kansa ya dafe yace kaina Juyawa yake kaini gida Kar na Fadi na sume,Rawar sanyi nake ji da mun sani mun dakko Jibson ko banza ya dafe Ni juwa nake ji, Mashkoor yace me ka gani ne Haka? Cikin muryarsu ta Yan kwaya Yace New worldddd....my man,jiri nake ji....yau idona ya samu Karin karfi gani tarrr nake ganin komai,idona ya washe yau,Yau ko me Shan Carrot juice Bai Kai idona kwari da washewa ba,Fess nake gani,Mashkoor Yana ta Dariya yace barawon Suruki,yace ai dole idan ba Haka ba sai su fara Bincike suna sa Ido Watarana su kamani.

Baba da safe cikin Fushi ya tashi an sace Masa startime da Radio yace wallahi kullum nayi Sallah sai na buga Tabbatyada duk Wanda yayi min satar Nan Allah ya bayyana shi,Dubu goma da motsi ai ba Nan take ba Kuma duk sakakinku ne ya nuna Mama yace Mene amfanin mace wacce Bata tattala kayan mijinta Bata kula da dukiyar mijinta komai naki Baki San adani da tattali ba ke Kam Baki Dace da matar aure ba da tsohuwar bazawara kika Yi Kama wacce mijinta ya Dade da rasuwa,Mama ta bude Baki Tace Wai ni na sace maka ne wannan wacce masifa ce akan Dan abinda Bai Kai ya kawo ba,Idan kinji haushi yau ki biyani cewar Baba,Mama Tace Zan biya ka Amma kaje Nima Allah ya isa,Baba yace ae ki biya naji Allah ya Isan.

A ranar Mama ta aika aka siyo Mata sabuwar Radio da Startime,Baba yace kin taimakawa kanki.

Aamna cikin wata doguwar rigar lace ta shirya sea green and milk ,takalminta,Mayafi da jaka duk milk tayiwa Mama sallama Mama Tace Yau ki dawo karfe biyu sabo da Zaki Mana wanki,to ta furta tare da ficewa zuwa Kantin,tunda taje take jiran Ahmad Amma Bai zo ba har 2pm lokacin ta rufe shagon ta wuce gida,20mnt da tafiyarta lokacin Ahmad ya Sha wanka cikin wata sabuwar Jallabiya me tsada ruwan zuma Kamar yanda ya Saba ta tsangale Masa,Takalminsa ma ruwan zuma yayi kyau tare da daura agogonsa me tsada,Sabuwar kitson calabarsa ya

gyara tare da Kama ta yasa Black band ya daure ta a tsakiyar kansa,wani uban kyau ya sake tsulawa, Mashkoor Yana ta zugashi yace ai dole ma ta rude,Kaga Handsome,shi Kuma a Gaban mirror ya tsaya Yana kallon kansa sai da ya Gama yace yau ba sauki bazan kalleta ba karta ce Wani sonta nakeyi, Mashkoor yace Good ka ja ajinka ba yanzu ba kwaila Kar ta Raina mu,da Masifa Ahmad ya furta wace Kwailar dan Uwarka? Ya bi Mashkoor zai ci ubansa Mashkoor ya gudu daga room din Yana dariya.

Kwafa ya ja ya fito tare da hayewa machine dinsa ya fita sai shagon Aamna Amma sai ya ganshi a rufe,Wanda ke siyar da takalma a kusa ya tambaya yace Ina me shagon Nan? Yace yanzu ta rufe tafi gida naji tana cewa zata Yi Aiki ne,Okay Kawai Ahmad ya Furta ya hau machine dinsa zuwa gidan su Aamna,har cikin gidan ya shigo da Machine dinsa,Aamna ya hango a jikin tap da tarin uban wanki a gabanta na Mama Dana Baba,Sanye take da Vest fara da Skert din atamfa wata maroon,gashinta har gadon baya Bata daura dankwali ba tana ta fama,Mama zaune take tana hutawa Kawai abinta tana ganin Ahmad ta Bata Fuska,ya manta ko Sallama baiyi ba ya karaso da Izzarsa yace Mama Barka da Rana,Baki Mama ta tabe Bata amsa ba Tace sai ka koyi Sallama sai na amsa maka gaisuwar taka,Baki ya tabe tare da yin Sallama ciki ciki ya kumbura Baki Kamar me shagwaba,Mama ta amsa tana hararsa sabo da bakin ciki,Juyowa Aamna tayi tana ta Kallonsa yanda yayi kyau,Murmushi tayi Tace Kawana Sannu da zuwa,Ahmad yace kawa ya Hanya,Lokacin Baba ya fito yace yau me Zan gani bayan auren da kuke da shi kun sake komawa sababbin kawaye Kuma? Mama Tace tayani jin sabon salon bariki, Ahmad Bai kulasu ba tunda wacce yazo wajenta tana Nan Ina ruwansa.

Mikewa tayi tsaye suna facing juna juciyarsa sai bugawa takeyi duk sai ya nemi kwarin gwiwarsa ya rasa,a hankali yace wanki kike Yi me uban yawa duk ke kadai,Aamna Tace ae ya na Iya,Kallonta yayi da azababbun Idonsa masu narkar Mata da zuciya yace Bari na tayaki,Aamna tayi Dariya Tace Kaine ka Iya wani wanki kalle ka fa ko Sabulu ai baka iya wankewa ba,komai fa Yi maka akeyi,Nifa super Man ne Ina da karfi da kike gani na har noma Zan iya zuwa gona nayi,Zan Iya nome Miki gonar data fi girman gidana lokaci Daya,karfa ka Sha wahala,ya nuna Kansa yace Wasa kike Dani,Aamna ta Mika Masa kujera ya kalli kujerar yace ba Aiki kike so ba sai kace wata mace na zauna a kujera Allah kiyaye a tsaye Zan tayaki kawo bucket ki gani,Baba da Mama Suka saki Baki suna kallo suna Jin haushi su Kuma gashi Basu Isa su iya ko Masa Maganar banza ba.

Bucket Aamna ta kawo Masa har biyu ya nannade Hannun jallabiyarsa dake me dogon Hannu ce,agogonsa ya cire ya ajiye gefe,Yace Ina kayanki a nan? Aamna ta Tace ka gansu a nan,yace Miko ta kansu Zan fara,ai kuwa ta kwaso ta bashi a gabansa kala hudu sai su Hijab da Vest yace idan an Gama sai kije ki cire na jikinki suma a wanke su yau baza ki kwana da Kaya masu dirty a gidan Nan ba,Baba Yana gefe yace Uhmmm.....Sun kasa magana suna tsoro Dan kwaya ne sai ya birkice musu yanzu.

Ahmad wanki ya fara baya wanki Yana wanke kala Daya Hannunsa ya fara Dan fashewa Amma ya maze yaci gaba da abinsa,Kugunsa ne ya fara ciwo sabo da sunkuyo amma idan ya Kalli Aamna sai ya fasa mikewa ya huta sabo Kar ya Gaza,Haka ya wanke kayan Aamna fes ya

kwashe kayan Baba da Mama Yana tayata suna wankewa ya kusa wanke na Baba,Mama ganin banza ta Fadi sai tace ke Aamna tashi ki barshi ya karasa wankin ki Shiga kitchen ki Mana girki,Ahmad yace ya Zaki ce ta tafi? Mama Tace Kai kace Super Man ne ai sai ka karasa ita ta Mana girki, to Aamna ta furta ta tafi ta bar Ahmad,tana tafiya ya Mike tare da dauraye hannunsa ya kwashe Takalminsa a Hannu da agogonsa da wayarsa,Mama Tace ya zaka daina aikin,dama yayi masifar gajiya,da masifa yace Ni na gaji bazan iya ba dama na gaji yayi tafiyarsa da sauri,Mama tana Kai...Kai....Amma ko juyowa baiyi ba ya hau machine dinsa ya bar gidan.

Mama da masifa ta shiga wurin Aamna Tace to ya gudu sai ki Koma ki karasa yace ya gaji shi,Dariya abin ya ba Aamna dama tasan karfin Hali ne Kawai Haka ta fito ta karasa Mama tana ta masifa taje taci gaba da aikin girkinta.

Ahmad kuwa a gajiye ya shiga gida Yana dafe Kugunsa ya Iske Mashkoor Yana kallo,Yana yatsina Fuska ya zare rigarsa daga shi sai Singlet da gajeren wando ya fada saman kujera Yana bawa Mashkoor labari yace yau wanki na tayata wash...bayana...taimaka ka siyo min pain killer a chemist kazo kayi min gashi da ruwan zafi wayyooo bayana My waist Yana magana da kyar yace yatsuna sun fashe ....Ni..Ni...nine nace Super man ne Ni, Mashkoor ya dinga dariya yaje ya siyo Masa ya dawo tare da hado ruwan zafi ya dinga gasa jikin Ahmad,shi Kama sai Kara da wayyo,Kwana Uku Ahmad Yana jinyar jikinsa kafin ya warke ya dawo normal lokacin Aamna Bata ganshi ba.

Yau Juma'a cikin sababbin dinkunansa yasa wata farar Shadda kamar ka sace shi yanda ya zuba kyau,calabarsa ya daure ya shirya Yana kamshi, Mashkoor ya kalle shi yace ban taba tunanin zaka ja Ni cikin Harkar Nan taka ba,kwana Uku ko Kofar gida ban leka ba wannan wacce masifa ce Wai,Gemunsa yake tajewa Yana shafe shi da wani turare Mai kamshi yace Ni fa na fara gajiya da Harkar wani Kawa da Abokin Nan ya kamata ta San me nakeji a Raina,Mashkoor yace ka bani dama Ni naje na fada Mata kana sonta,Baka da hankali an ce maka sonta nakeyi Kuma ko sonta nakeyi wani ne zai fada Mata Ina sonta ba Ni ba,ai Ni abinda nakeji a Raina game da ita Zan fada Mata ba Wani love ba.

Mashkoor yace to yanzu fada Mata zaka Yi? yace ae direct Zan sameta gaba da gaba na fada duk irin abinda zuciyata takeyi idan na ganta yau yau din nan,Allah ya bada sa'a cewar Mashkoor,Fita yayi abinsa Musa me Gadi Yana a dawo lafiya ranka ya Dade,Ameen ya Furta yiyiwa Machine dinsa key ya fita zuwa Shagon Aamna,tana tsaye tana sallamar wata ta siyi kayan kamshi ta hango shi yayi parking,Murmushi tayi Tace Sannu da zuwa,Kasa magana yayi sai kallonta yake Yi har ya karaso inda take ya tsaya a gabanta daf da ita Kamar zai shige cikinta Kuma ya Bata Rai zuciyarsa ce Kawai take bugawa,kasa fada Mata yayi yace ya gida fuskar Nan a daure,Lfy Alhamdulillah ta furta tare da cewa shigo ka zauna Rana,shiga yayi Yana ta Fushi,Tace fushin me kakeyi yau Haka? Kadan ya kalleta Bayan ya zauna a farar kujera yace da zuciyata nake Fushi ita take nunawa bacin Raina,Dariya ce ta Kama Aamna Yana ta kallonta a ransa yace kin cuceni zuciyata bazan yafe Miki ba Kuma yau Bari na koma gida sai kinci ubanki,Me ta maka zuciyar Aamna ta tambaya yace Ni kadai na San irin wulakancin da take mini Amma ba komai Yaja kwafa,Aamna ta sake kecewa da dariya Tace kana da abun Dariya wlh,Kawai sai ran Ahmad ya baci shi ga abinda ya dame shi ya fada ya kasa fada duk

akan Aamna Dan rainin hankali ta sashi a gaba tana ta dariya,a ransa yace na koma ma abin Dariya na koma Comedian ba komai yayi Shuru.

Har ta Gama dariyar ta dakko Gyada soyayya Tace ga Gyada muci,ganin tasa hannnu a Ledar ta Eba tana ci sai shima zai Eba Aamna Tace tsaya na bare maka,bare Masa tayi Guda biyar ta zuba Masa a tafin Hannu Tace to ci,kallonta yayi sannan ya zuba a bakinsa Yana daga zaune Yaja baya yayi wani tangal tangal Kamar zai Fado Aamna ta rike kafadarsa da sauri tana tambaya lafiya???yace Dadi ne ya kwashe Ni sabo da hannunki da ya shafi jikin gyadar nan,Dariya Aamna tayi Tace Kai Ni nayi zaton ma wani Abu ne,wani English novel ta dakko na love tana karantawa Tace ka San littafin Nan? Na Mene ya tambaya? Love Novel ne Baki ya tabe yace sai ku wannan ai,Mayafinta ne ya Dan zame kadan gashin Gaban goshinta ya bayyana wani yala yala,Hannu ya sa tare da jawo mayafin ya gyara Mata Aamna dai mamaki yake Bata kamar ba shi ba,duk irin kiyayyar Daya nuna Mata tana ina ne? A ranta Tace Anya ba Yana da manufa a kaina ba kuwa? Gaskiya Zan nemi shawarar Siyama.

Kiran Sallah aka kwala Sallar Juma'a,Aamna ta kalle shi tace yanzu za'a fara khuduba sai muje Sallah ko? Da sauri ya girgiza Kai yace a gida zanyi anjima,Jam'i Yana da Lada fa? Yace na fiki sani ai, kin San kuwa Islamiyya Nawa nayi a duniya? Kin San saukata Nawa? Aamna Tace Dan Allah muje tare,a ransa yace Yarinyar Nan fa zata fara juyani karka sake wannan Yar tatsitsiyar ta juyaka a banza,ai ba sonta kakeyi ba da har zata juyaka,wata zuciyar tace Amma idan kaje Sallar zata ji Dadi zata samu farin ciki,Kumatunsa ya Mara a hankali yace Kar ka Bari ta juyaka ka dawo hankalinka,mikewa yayi yace Zan tafi,Tace Nima tafiya zanyi zanje gidan Zuhra,yace kin fiye yawo to na fasa tafiyar Zama ya koma yayi Dole ta zauna,Lokacin Sallah yayi Yana kallo tayi Alwala tayi Sallah a Nan shagon,tana idarwa yace Sannu da kokari,Fuska ta Bata tace Dan Allah kayi Sallah Kar lokacinta ya wuce,Shuru yayi Kuma yaki tashi sai yaga tayi Fushi ta zauna,Fuskarta ya leka kadan a ransa yace akan Haka har tayi fushi,Bari to na Yi Amma badan fushinta ba,Mikewa yayi tana kallo yayi Alwala ya Tada Sallah murna tayi ta saki ranta ta juya tana kallonsa a nutse yayi sallarsa kasancewar Bai Sha komai ba,Yana idarwa ya Mike ya fice tare da tafiya ko Sallama bai Mata ba.

Mashkoor kuwa Yana can a gidan Ahmad tare da su Jibson gaba Daya Yana ta Basu labari yanda Sarkinsu ya lalace,duk sukayi tagumi suna jimami,Jibson yace ai kuwa sai munje har inda yake tayata siyar da citta mun kure shi,yanzu King ne ya lalace Haka abin haushin Akan wannan Yar Yarinyar Aunty Balaraba cewar Bash,Mashkoor yace yanzu idan kaga shigarsa Daya canja kamar Limamin masallaci,Salati suka saki Tawaga yace duk akan Yarinyar nan lallai sai munci ubanta kuwa tunda ta mayar Mana da King Haka, Mashkoor yace Uhm Baku gani ba har wani sharemu yake Yi ba Amma muyi Masa Uzuri ai King ne sai abinda yace,Allah sarki masu shaye shaye da hankalinsu sun San Amana da abokantaka duk abinda dayansu ke so suna so,sannan basa mantawa da Alkhairi da zaman tare,shi yasa sun Shaku da juna sosai.

Ko da Ahmad ya shigo ya Iske su tafawa sukayi ya haura sama,Yana shiga wayarsa ya dauka tare da Kiran Sis dinsa Humaira,Humaira Tace Yaya na? Ya kake? Ba lafiya sis Dan Uwanki ya fada cikin bala'i,Humaira ta tsorata sabo da Bata taba Jin yayanta Haka ba,Kamar

zata Yi kuka Tace Yaya mene ya sameka? Sis wata ce Nan idan na Ganda zuciyata kamar zata fito ta fado,sai ta dinga Yi min kida me zaki,Humaira Tace Kamar ya? Yace idan fa ban ganta ba bana iya bacci,sai na ganta nake samun nutsuwa,Haka idan naji muryarta sai naji Kamar wani kidan goge sabo da Dadi,gashi tsoronta nakeyi sai naji na kasa fada Mata me nake ji,Yanzu ya zanyi? Humaira tayi zaton zaice Aamna ce Amma yace Mata wata,Amma duk da Haka tayi murna yayanta ya fada soyayya,Tace Yaya kaje ka sameta karka ji tsoro Kawai ka fada Mata me kake ji,ka daure Haba Yaya kamarka wace zata ce baka Mata,Sis Nifa ba sonta nake Yi ba Kawai dai Ni na fada Miki abinda nake ji,Humaira tayi Dariya tare da furta ka fada Mata karka ji wani shayinta kaji,yace to sis Zan gwada ya kashe wayar,lokacin da yayi wanka su Jibson sun tafi sai Mashkoor sai shi.

Ahmad dakin Aamna ya Shiga Wanda ta bari,cikin kayanta data Bari ya zabo wani Mayafi Baki ya fito Palo wajen Mashkoor tare da jefa mayafin a jikin Mashkoor yace Man tashi ka yafa mayafin Nan za mu gwada practical akan yanda Zan furtawa Aamna me nake ji game da ita,yanzu ka yafa mayafin Nan Kaine a matsayin Aamna Ni Kuma Zan zo na gwada ya zan bullo Mata idan naje, Mashkoor ya dinga dariya harda buga kafa,ya Mike yayi Rolling da mayafin Aamna ya taho Yana yanga tare da wani shanye Hannu,a Gaban Ahmad ya tsaya tare da Yi Masa fari da Ido ya wani tsotsi lips yace Hey.....harda rike hips da Hannu Daya yanda Mata ke Yi,Ahmad Dariya ta kamashi shima ya kalli Mashkoor yace to ai Ni gemunka ne idan na kalla Taya Zan maka magana Ina ganin gemu dalla jiba Muscle dinka damatsa na maza,jiki Kamar katako, Mashkoor ya sake makale Murya Yana fari da Ido yace Dan Allah kayi mu gwada ai Kawai Kamar shooting Film ne Oya fara Mana nine Aamna gani.

Ahmad Yana daga zaune ya fara magana Kamar zaiyi kuka,Baby Idan na ganki zuciyata wani Dancing take min,Idan kika min murmushi kuwa har wani Rawar galala zuciyata take min,Sannan Ni sai naji Ina shakkar Yi Miki magan....da sauri Mashkoor ya dakatar da shi yace dalla Haka zaka Yi lallai zata Raina ka Haka maza ke magana wani gadangatsai Taya zaka burgeta oya canja salo Action.....Ahmad yayi Gyaran Murya tare da gyarawa ya kalli Mashkoor zai fara magana sai ya sheke da dariya yace wallahi idan na kalli Damatsanka hankalina Bai kwanciya bana kallonka a Aamna ga gemu da saje haba,Kayi sauri Dan Allah wannan fa Kamar Film ne gwada Ina jiranka Mashkoor ya furta Yana wani Fari da Ido Yana karairaya Kamar Dan Daudu,Ahmad mikewa yayi tsaye yace Ni bazan iya ba kallonka nakeyi wani Gardin banza dalla bani ya fisge mayafin daga jikin Mashkoor tare da ajiyewa a gefensa, Mashkoor yace kaga matarka ce fa ka daina wannan abin ka fadawa Mummy ta fadawa Aamna ta dawo gidanka kaga shike Nan.

Ahmad yace baka da hankali Nifa ba Wai wani mu zauna tare ko wani Sex ba,ya za ayi na birgeta,ya za ayi tasan me nakeji a Raina game da ita shine Kawai dawowarta gidana ba shine mafita ba,Ni ba wannan nake so ba,Dan dawowarta ai ba matsala bane Kawai Ni ka Gane nufi na,idan ta San halin da nake ciki Nan gaba Sanda taga tana so sai ta dawo gidana Ni wannan ba shine damuwa ta, Mashkoor yace Amma sai kayi ta wahalar da kanka kana tsallaka musu gida,Kai banza ne bana so ajina ya zube ta Gane Ina son na kalleta ko wani Abu,ai abin sai da dabara cewar Ahmad.

Da dare 9pm Ahmad suka Isa gidan su Aamna Mashkoor Yana jiransa a can bayan gidan,Wai shi lallai Bai so Aamna ta Gane Yana son ganinta sai dai ya kalle ta a boye.

Sharhi

AsmaBaffa
10/26/21, 8:53 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

51-55

KARSHEN FREE PAGE

DUNIYATA AAMNA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

NA KUDI NE

MASU SHIGA GROUP DARI BIYU 200 NE

ACCOUNT NUMBER
0175487861
ASMAU GARBA MUHAMMAD
GTBANK

MASU TURA KATIN MTN KO VTU GA NUMBER
08033933642

YAN NIGER KU NEMI WANNAN NUMBER
+227 90 79 59 39

Official

By
AsmaBaffa

Kinfi karfin page
NAFEE
Allah ya bar kauna

Page naku ne

MAMU GALADIMA
AYUSHEE
MOM PAPI AND ALAMEEN
OUM ABULKHAIR
HAUWANCY COOL LIFE
S.Y.SAGAGI
RA'AYYS
I HAFSAT
UMMY MANGA
MAMAN ARFAT
MAMAN YASIR
M DEWU
HAUWA A CHINDO
HALIMA

GODIYA TA MUSAMMAN

DIYAR KATIBI
UMMIN HIBBAH
UMMA KHURSUM
ASMAU YUSUF
UMMIN DEEJAT
BESTYNBEELAT

Yau Baba Bai dawo da wuri ba,Aamna Kuma dawowarta kenan daga gidan Zuhra Mama Tace tazo ta tayata dafawa Baba abinci,ko hutawa Bata Yi ba ta shiga wajen Mama a kitchen suna girki,ta Kofar gate Ahmad ya shigo gidan,ta windown kitchen ya leko dai dai lokacin Mama ta dago kanta sama Kawai Harshen Ahmad ta gani ya Mata gwalo ya bace.

Amma Bata San shi bane Tace Kinga kamar Harshen mutum ta window ya min gwalo ya bace

Aamna,Aamna ta sheke da dariya Tace wallahi Mama yanar Ido ta Kamaki sai munje asibiti an duba idonki,Mama ta dage ita fa sosai taga Harshen mutum,Aamna ce ta maida abin Dariya shi yasa Mama ta hakura Kawai, shi kuwa ya gansu a kitchen ai ta Kofar Palo ya shigo a hankali ya shige Dakin Aamna,bed din Aamna wani me kyau ne na karfe irin na kasar waje Dan madaidaici Amma kasan bed din Yana da tsayi mutum zai iya Shiga kasan Bed din ya buya gashi ta gyara bed din ta saki bedsheet har Yana taba kasa ma'ana ko mene a kasan Bed din baza a iya gani ba,lekawa Ahmad yayi ya kuwa shige ciki ya kwanta abinsa,Bai Dade ba Aamna ta shigo dakin tare da dannawa kofarta key,Abincinta ta Ajiye a plate da ruwa harda lemo mirinda,ganin ba kowa a dakin ta kulle ko Ina sai ta hau tube kaya,dama dabiarta ce idan ta kulle Kofa ta dinga tubewa daga ita sai pant ba komai a jikinta,Ahmad yace yau ma idona zai samu Karin karfin gani Ni da ciwon Ido haihata haihata ya Dan leko ta kasa,Baki ya bude ganin Aamna da pad a jikinta da Alama period takeyi,Yana kallo ta dakko wata pad din da bakar Leda ta shige toilet sabo da Gadarar ba kowa ga towel a Hannunta Amma Taki daurawa ta tafi da shi a hannu.

Fitowa Ahmad yayi ya Bude plate din yaga rice and stew da Naman rago yanka Uku sai salat a gefe,yace da a gidana ne sai kinci nama kin koshi duk Loma Daya sai kin hada da yankan nama,Sorry My world ya rufe Mata tare da komawa kasan bed,ta Dade tana wanka kafin ta fito tana goge jikinta ta fara shafa lotion ta cire guntun Towel din tana ta shafe jikinta,Ahmad Idonsa Yana waje ya leko yace sunanki me Tinjim daga yau,sai data Gama sannan ta saka Riga da wando na bacci masu laushi ta zauna ta tare da fara cin abincinta  da mamaki yaga ta cinye tas ta shanye lemo da ruwa,a hankali yace Allah yasa Ina da kudi Zan iya ci dake Amma da talaka kika aura ai ke Kam shikenan sai dai Gomnati ta kawo dauki, Popcorn yaga ta dakko a wani katon Bowl ta Ajiye a gefen bed ta kwanta tana latsa Wayarta tana ci a hankali,idan ta eba ta cire Hannunta tana can tana Danna waya sai ya zuro Hannu ya eba ya cinye a kasan Bed, suna Haka taga wayam Wai har ya Kare,Aamna ta dinga mamakin kanta Wai har ta cinye popcorn din,ta kashe Wayarta tare da kashe light ta kwanta tana adduoi kafin ta Gama Adduar bacci ya kwashe ta.

Sai da ya tabbatar baccinta yayi nauyi sannan ya fito a hankali da Dan hasken wayarsa yayi amfani tare da Kare Mata kallo,Aamna ta baje a saman Bed,cinyoyinta Suka tafi da hankalinsa Hannu yasa tare da shafa su a hankali yanda baza ta tashi ba,motsi tayi kadan tare da sake wangale su,Ido ya Kura musu yasa Hannun ya janye rigarta sama sosai ya kallesu son ransa, ganin kamar zata farka sai ya daina, Kansa ya duka a saitin kirjinta tare da kwantar da Kansa a Kirjinta yaji wani laushi sai ya lumshe Ido Nan take yaji ya fara Jin bacci,da sauri ya tashi Jin ta hada zufa sosai sabo da Rashin wuta bare a kunna fanka,Mifici ya gani a can gefen bed din nata,Dauka yayi a hankali ya shiga yiwa Aamna fifita ba ji ba gani Kamar me jinya a gadon asibiti,Aamna cikin bacci taji Iska me Dadi tana Ratsata ta sake gyara kwanciya tare da Jan numfashi me Dadi,Murmushi yayi yaci gaba da Mata fifita sai da Hannunsa ya gaji sannan yaga Kamar zata farka sai ya ajiye mificin ya lallaba ya bude Kofar a hankali ya fita Allah yasa Bata farka ba Kuma Bai hadu da kowa ba har ya bar gidan, Mashkoor Yana ta uban jira ya hauro ya fito Suka tafi gida.

Hannu Dayan Wanda ya shafa Cinyar Aamna sai Ahmad ya daga shi sama kada ya daina amfani da shi Kamar Wanda aka yiwa lallen Sallah,Mashkoor yace lafiya Wai me ya samu Hannun rauni kaji ne?yace ai wannan Hannu yau ya Zama special bazan na aiki da shi ba,Kai ko Gaisawa da maza bazai Yi ba sabo da jikin Aamna Yana makale a jikin hannun Nan, Mashkoor yace ka shiga Uku wallahi king.

Bayan Kwana uku Siyama ce ta Kira  Aamna lokacin Aamna tana shago Tace gani Nan zanzo Miki Ziyara,da murna Aamna Tace to sai kinzo,15mnt da yin wayarsu Ahmad yazo sanye cikin 3qutr da t-shirt hannunsa dauke da wata katuwar leda baka,Murmushi Aamna ta saki tare da Furta Sannu da zuwa,jajayen lips dinsa ya turo gaba da shagwaba,Ledar ya kawo gabanta tare da ajiyewa ta Bude yaga kifi tarwada da yawan gaske,murmushi ta saki tare da Kallonsa Tace yanzu baka manta ba Ashe Kuma ma ai Rannan ka Aiko Mashkoor ya kawo min kifin harda kaji da yawa fa,Ba kince kina sonsa ba? Ae ta furta yace to ai shine na kawo Miki,Kuma kaji ai Naga a gidan Baba bakya cin nama kina koshi shi yasa duk sai ramewa kike Yi,Dariya Aamna tayi Tace Ni bana son sharri duk kibar Dana yi,Kallonta ya tsaya Yana Yi har ta Gama dariyar,ke komai naki Dariya Wai Ina rashin kunyarki tayi ne da surutunki? a baya masifa kike min da Shishigi me yasa yanzu kika daina? Aamna kanta ta danga sama tayi fari da Ido Ahmad a ransa yace Mashaallah ko iya wannan aka barni da shi ya isheni farin ciki na sati Guda idan na tuna shi.

Mikewa tayi tsaye tana Masa Murmushi Tace Kaine ka gyara min halaye na,kaci ubana da yawa sai lokacin na Gane Allah Daya,a hankali yanda baza taji ba yace ai Nima yanzu uban Nawa kike ci na Zama wani banza,Bakinsa taga Yana motsi Tace me kace? Cewa nayi Ni ba abinda na Miki kece kike min shishigi,Siyama ce tayi Sallama gabanta ya Fadi ganin Ahmad da Aamna a tsaye daf da juna kamar zasu Rungume juna,Fuska ta Bata tana Hararar Ahmad sabo da kishinsa,ita ba hassada takewa Aamna ba Kawai son Ahmad ne yayi tasiri a ranta taji dama ita ce.

Laaa Siyama kinzo cewar Aamna,Ahmad juyowa yayi Amma ko kallo Bata samu daga gare shi ba ya maida hankalinsa cikin Shagon,Nan Siyama ta shige ciki ta zauna tana satar kallon Ahmad,Ledar dake gaban Aamna take ta faman kallo taga kamar Abu na motsi ciki,Ahmad ganin tana ta kallon Ledar ya tabbatar Aamna sai tabawa Siyama kifin Nan itama ko su raba tare sai ya leka Daya shagon ya Kira wani yaro Wanda Ahmad yasan Yaron kusa da gidan su Aamna yake ganinsa shima gidansu makwafta ne,Yaron Yana zuwa Ahmad harda shafa Kansa yace Dan magyatso kasan gidan su Aamna? Yaron da Ahmad ya Masa suna da Dan Magyatso yayi dariyar sunan sabo Yaron Kalar yunwa ne,jikinsa tsilili cikinsa Dan kato sabo da Almajirin gidan Wasu ne a kusa da gidan su Aamna,yace ae nasan gidan Ina shiga ma idan an aikeni,Ahmad yace ka iya machine? Yaron yace sosai ma ai Ni nake yo cefane a machine din gidan Uwar dakina,Good cewar Ahmad yace ungo key din machine Dina jeka gidan su Aamna ka kaiwa Mama sakon Nan kace gashi inji Aamna,Yaron yace to ya karba ya hau machine din Ahmad ya tafi,Siyama ta so ace ta karbi kifin ko Quarter ne itama taje gida sun Sha farfesu Amma tana kallo Ahmad ya dauke Dan mugunta.

Tunda Siyama ta Shiga shi ya fito ya tsaya a waje,Aamna Tace ka shigo Mana yace a'a Machine Dina nake jira tafiya zanyi,Siyama ta kalla tace ina zuwa kawata ta fito Wajensa suka tsaya,tana ta Kallonsa a ranta tana ayyana irin kyansa,Shi kuwa ganin tana kallonsa harda Kara gyarawa Kamar za a dauke shi hoto,idan ta kalla ta kalla sai ya sake canja style din tsaiwarsa Haka yake ta Mata ya tafi da hankalinta sai daga baya ta lura da abinda Ahmad ke Yi Yana ta canja style din tsaiwa,Dariya ce ta Kama Aamna ta danne kadan tayi Murmushi Kansa ya shafa tare da mazewa kamar ba shine yayi ba,Hannunsa Aamna ta rike ya Janye hannunsa da sauri,Aamna tace lafiya? Kitsonsa ya Sosa yace ba komai Kawai Ni ba a taba min jiki kin sani ko kin manta ne?

Baki Aamna ta tabe Tace daga an Dan rike maka Hannu sai kace Dan gwal? Yace ai nafi gwal Ni,Harararsa tayi a ranta tace Dan ma na Dan nuna Masa caring shi illarsa Bai San arziki ba,Ganin ta harareshi yace Jaraba tare da miko Hannun yace ungo cinye shi ki huta,Bige Hannun tayi tana Dariya Tace bana so,Suna Haka Yaron ya dawo da Machine din Ahmad ya karba tare da bawa Yaron dubu biyu,ya dinga Murna yana godiya,Ina Handbag dinki? Ahmad ya tambayi Aamna.

Tana ciki yace dakko min ita,me zakayi da ita Fuska ya Bata yace ki dakko Mana Ni ba Mudubi ko powder dinki Zan gani ba nasan ku ba Uwar komai a jaka sai Kuna boyeta,Dakkowa tayi tare da Mika Masa yace Bude abarki ki rufe idonki Kuma,Aamna ta zuge jaka ta rufe ido,ganin Haka Siyama ta leko tana kallo Ahmad ya zaro kudi masu yawa Yan dubu dubu ya zubawa Aamna a jaka yace to Bude,Bude Idonta tayi taga kudi dama Bata da kudi tayi broke Bata da ko sisi gashi tana son siyen abinda ba a rasa ba na bukatar rayuwa,taji Dadi sabo da ya Bata lokacin da take bukata Tace Na gode Allah ya Kara budi Amma sunyi yawa kamar,Kansa ya dauke yace na tafi Mummyta ta aikeni tun dazu wani waje zanje na Mata Abu,Aamna Tace Kai dai kana son Mummy kullum Mummy,ai Mummy ta daban ce,Mummy na tafi Mummyn kowa cewar Ahmad,Aamna Tace Nima tawa tafi ta kowa,Murmushi yayi yace kin nemi Number Abbanki kuwa? Aamna Tace me Zan Masa tunda ya manta da ya auri Uwata ya Kuma haife Ni idan na karba me Zan Masa?

You are not Serious Haka aka ce Miki Iyaye suna laifi?Shuru Aamna tayi Watarana tana mamakin Hankalin su Ahmad,gasu dai suna tafka abin tsiya sai Suna Abu Kuma na basira da hankali, a fili tace Suma Yan Uwan nasa Dana je Sokoto nace su bani number dinsa Suka ce wallahi wurin shekara Uku kenan duk sun kasa Samunsa sai dai suna Kiran Yan Uwa na can kasar sunce yana Nan lafiya Kawai dai yanzu yayi retire a aiki Bai da aikin Yi ga Yara da Mata sun Masa yawa wahala ta kamashi,Ahmad ya girgiza Kai yace tab nasan yanzu ya sake kanjamewa Allah Sarki Abbinki,Aamna Dariya ya Bata ta bigeshi a kafada kadan Tace Wai Mene Haka ka dameshi Akan ramarsa, Murmushi yayi yace Bai yuwa ya rasa waya sai kace a Nigeria ai can ba a wannan talaucin, Ni Zan nemo Miki number dinsa,Aamna Tace Okay thanks, Machine dinsa yayiwa key tare da tafiya abinsa.

Siyama tana zaune ta kumbura tayi fam kamar ta fashe tace ke dai Aamna kinyi asara,wallahi Baki da hankali to wannan abinda yake nuna Miki ba so bane,Kar ma ki yaudari

kanki Ahmad bazai taba shiryuwa ba ko jiya naje wajen Jibson a club Suka kwana suna shaye shaye suna rawa,Aamna Tace karya kikeyi Siyama wallahi Ahmad baya rawa,Yana Jin kida Yana bin Waka Amma in Banda ya Dan kada Kansa ba abinda ya taba Yi na rawa,Da kike cewa bazai shiryu ba kece Allah,Ina ruwana da Club dinsa,Siyama Tace Iyye to Bari kiji idan Baki sani ba Neman Mata suka koma Yi yanzu,kije ki tambaya Ahmad lallabaki yakeyi ki saki jiki da shi ya samu biyan bukata,Aamna Tace karfa ki manta Mijina ne,ko ma me yayi Hakkinsa ne ko ciki ya min akwai me zagina a duniya? Wai me yasa kika tsani Ahmad Haka ne Siyama? Siyama Tace sabo da Ina sonki kawata Ina kaunarki bana so ki fada wani Hali,Aamna tayi shuru....Tace to yanzu me kike so nayi? Karki bashi dama Kawai Kuma karki yarda da shi karki Bari Zuciyarki ta fada sonsa cutarki zaiyi,ki kiyaye Aamna bana so na ganki cikin wani Hali,plan suka hada Miki,Ahmad tun Yana yaro kangararre ne a Haka ya girma a tunaninki dare daya zai shiryu sabo da ke? Kiyi tunani fa,wanne duka da wulakanci ne Baki Sha ba a Wajensa? Ai Ni nake tsokanarsa Aamna ko a lokacin Ni ke shiga harkarsa da ban kulashi ba babu abinda zai min,Siyama tayi Dariya Tace kina Abu kamar yarinya 25yrs Sam Baki da wayo Baki da hankali Ni Naga wani Tsoronsa kike ji ma kina wani biye Masa,Dan giya irin wannan Dan kwaya abin kyama cikin Al'umma mutanen da Basu San darajar kansu ba bare ta wani Nan fa Siyama ta dage ta dinga zuga Aamna tana fada Mata karya,har ta Gama sannan Aamna Tace Ni fa bazan iya wulakanta shi ba,Kuma bazan iya masa komai da zai Bata Masa Rai ba,Kawai dai nasan bazan Bari na fada sonsa ba,ko cewa yayi Yana so na Zan Amince Amma badan so ba Zan Amince Dan nayi kokari na canja shi ya dawo mutum Kamar kowa ya daina wannan shaye shayen shine Kawai abinda Zan iya Dan na taimaki Iyayensa,Siyama tace ya dai fiye Miki Ina Baki shawara karki fada sonsa.

Bayan wasu satikai Ahmad Haka yake ta wahala da zuciyarsa ya kasa fadawa Aamna idan yaje da Niyyar fada sai ya kasa babu irin plan din da Basu hada ba da su Mashkoor Amma idan Ahmad yaje Gaban Aamna sai ya kasa furtawa,Yau Suna zaune da Mashkoor suna shaye shayensu Mashkoor yace yau shine Plan na karshe King idan baka iya fada Mata ba wallahi gidan Nan Zan Bari kaje ka karata,Ahmad ya daki Center table yace yau Dole ne na fada ma Dole babu fashi mene plan na gaba?wayarsa ce tayi Kara Yana dubawa yaga Bash ne abokinsu dagawa yayi yace ya akayi ne guy? King ku fito Umman Jibson ce ta rasu a asibiti ciwon Sugar dinta ne ya tashi Ana kaita Hospital ta fece wallahi,Ba ko Salati Ahmad yace yanzu Ummati ta ware itama? Yace kwarai kuwa Kun manta yau Kuma ake Sadakar Arba'in din Baban Tawaga da ya Dier shima ya kamata ku fito fa Jibson Yana wani Hali, Mashkoor ya kashe waya tare da kallon Mashkoor tashi mu tafi Ummati ta arce itama shikenan mijinta yayi asarar matarsa Allah sarki Shan maganin Mata ya Kare Abbin Jibson Kuma karya ta Kare Dadi ya kare Masa ya Gama Shan rabonsa, Mashkoor yace Kai tsohuwar Nan ai ta godewa Allah ai su Kam sunci duniyarsu me zasu ce da Allah mu ware kawai.

Machine suka figa Suka tafi Ahmad ya kalli Musa yace Kai Musa ka taho ta'aziyyar Ummatin Jibson kaga ku na kirki ne wala'allan adduarku tafi Shiga,Dariya abin ya Bawa Musa ya danne ya nuna jimaminsa yace gani Nan kuwa Bari na kulle gida,Ahmad yace biki ya same mu sabo da yanzu mutuwa ta koma biki Yan iskan mutane su taru ayi ta kwasar girki, Mashkoor yace Ana kaita kabari muje a agazawa su Jibson da tallafin kayan abinci kasan babansu ba harka

Yana Shan wahala,Haka ne fa Guy cewar Ahmad,ai kafin kace me Yan shaye shaye ta ko Ina abokan su Jibson suna ta sauka wasu a mota wasu a machina, da su aka yiwa Ummatin Jibson Sallah aka kaita,Tabarmar su daban a Kofar gida sunyi jungum jungum Ana zaman makoki,Jibson ya dunkule waje daya a tsakiyarsu tare da sunkuyar da Kai kasa Yana Dan Hawaye motsi kadan sai Yace Uhmmmmm........Uhmmmm.....su Kuma abokan suna Sorry...sorry....Guy,Baban Jibson Yana kusa dasu Yana jinsu da mutanensa shima Ana karbar gaisuwa,duk Wanda yazo yiwa Jibson gaisuwa yace Ashe Ummati ta rasu? Jibson sai yace da Uwata ta mutu gwara Ubana ya mutu wallahi,Kowa yazo sai Jibson ya fada Masa da Uwata ta mutu gwara Ubana ya mutu Abbin Jibson Yana ji Yana ta Jan kwafa,wasu kuwa dariyarsu Kawai suke dannewa.

Tawaga ne yazo ya kotse machine tare da bulbule mutanen wajen da hayaki ya sakko wajen su Ahmad ya Bude hannaye da sauri Yana takowa Yana an Kuma...an Kuma Yan Uwa an Kuma jama'a...suka ce cikin jimami an Kuma Guyu......ciki yazo ya zauna yace Yau akayi Sadakar Arba'in ta Abbana Ni fa yanzu gaba daya na koma Wani shege....shegeee ne Ni Kawai bani da uba...kaf mutanen wajen babu Wanda Bai Basu Dariya ba Amma wasu Haka suka danne sabo da wajen Mutuwa ne,wani Wanda ake cewa Gayu yace ai Nima Ina cikin Shegun mu mun Zama 'yayan shege to ba uba ai Kawai ka Zama Dan shege....wani Ana kiransa Jagu Dan wiwi a cikinsu yace wannan abin idan na tuna ba karamin kuka yake sani ba ya fashe da kuka shima Yana cewa Nima Ina cikin 'yayan Shegu,Wai su Kawai idan baka da uba ya mutu to ka koma Dan Shege,idan Kuma Uwa ce to ka Zama cikakken Maraya komai girmanka.

Ahmad ya dafa Jibson yace ai gwara na Zama Shege akan na Zama Maraya Jibson,Mummy ta Mutu ai Kawai ku kaini kabari da Raina Nima ku binne,Mashkoor yace mu Kuma mu zauna da wa idan mun binneka shike Nan muma Bamu da kai? Ai bazai yuwu ayi biyu babu ko daya ba,Ana ta kallonsu Dariya ta cika mutane Amma an kasa Yi sabo da mutuwa kowa sai ya bar wajen yake Dariya,Wani Dan Majalisa yazo Ta'aziyya,Baban Jibson ya Kira shi yace ga babban Dana can,Jibson ya karaso wajen,Dan Majalisa yace Sannu da Hakuri Allah yaji kanta yaro kayi Rashi,Jibson yace Babban Rashi yau na tabbata Maraya Dan Allah ku bani mukami a Gomnati na shugaban Marayu na Nigeria da Uwata ta mutu wallahi gwara Ubana ya wuce sau dubu dubu,Danmajalisa shima abin Dariya ya bashi gashi da yanda suke Maganar abin Dariya ta Yan maye.

Kudi ya zaro dubu Ashirin ya mikawa Jibson yace gashi ko ruwa a siyawa Mutane Jibson yace Allah kiyaye na karbi bakin kudi,wannan bakin kudi ne tunda baka bani ba sai da Uwata ta mutu zaka bani wanne amfani zasu min,Baban Jibson ya daka Masa Tsawa Amma Jibson yace wallahi bazan karba ba,da karfi ya daga Murya Dan wulakanci sai da aka ga Uwata ta mutu Za'a taimakeni duk an wani cika Mana Kofar gida Ana cinye Mana Dan abincin Daya rage Mana,Dame zamu ji da cinye abinci ko da jimamin,kowa Yana ci Yana wani jimami,Mata Yan Uwa suna kuka suna ta girki Ana Dora tunkunya Ana saukewa wallahi baza mu lamunci wannan ba,Ahmad ya mike shima yace a barmu da abinda ya dame mu na rashin Ummati mun gaji tun safe muke bi layi layi na mutane Muna rabon ruwan Sha da Abinci,Tawaga yace aikin banza Muma Haka Dan kudin Sadakar da aka Tara Mana da abincinmu cikin sati Daya aka

cinye shi tas ga tarin Yara an mutu an bar min,Baba ya dinga aure aure ya Tara Yara Ashe duk Haihuwar da akeyi Ni ake haifawa ban sani ba, wallahi da nasan hakane da kaina Zan dauki matan Baba na kaisu asibiti Dan ubansu duk a daure bakin Haifarsu,yanzu ga Yara can sunfi ashirin Ni kadai ne Babba Kuma ba Wani Abu ya mutu ya Bari ba gona ce Kawai a Kauye Guda biyu.

Ina Shiga gida Yara suna zare Ido Yan kanana turagutsa ba Wanda zai iya aikin karfi to wallahi a Nan ma tunda Ummati ta rasu Baba baza ka Kara aure ba wallahi ko wace zata aure ka sai mun farke Mata ciki,Ahmad yace bazai yuwu Iyaye ku dinga aure aure Kuna mutuwa Kuna bar Mana masifa ba,ga yanda kasa take ciki yanzu a mutu a bar maka Yara Kai kanka da kyar kake iya rike cikinka, daga yau mun Zama masu yaki da Aure auren Iyayenmu maza,duk tsohon Daya matsu zai Kara aure to ya Nemo juya wacce Bata Haihuwa ko Kuma aje a cire Mata mahaifa.

Jibson yace Iya Ummati Abbi ya aura Amma Haihuwar ta Sha Uku Haba jama'a sai kace macen Zomo, Guda Daya ne ya rasu Sha biyu suna Nan cas da me zanji gasu duk mata,ko wacce na shiga Yaya kudin makaranta,Yaya kudin kitso,Ya..ya..ya...masu auren ma yau Fa'iza mijinta ya hanata abinci ta dawo gida an auno Mata shinkafa ta tafi da ita,gobe Safiya mijinta ya mareta ta kawo Kara,jibi Zakiyya mijinta ya korota  to a gaskiya bazai yuwu ba,daga yau kunci abincin karshe gobe ko koko ba me Fitowa da shi wallahi.

Mutane suna ji Ana ta kallo wasu suna zanzarewa Baba shima yasan Yaran sunyi gaskiya tsoro yake ji Kar a cinye Dan abincin nasu su fada wani Hali Amma sun tozarta shi ya zaiyi dole ya kyalesu tunda su suke siyo komai abokan,Ahmad kadai mota guda ya sauke musu ta kayan abinci da safe,Haka duk abokan kowa iya karfinsa sun kawo tallafi daban daban,Kuma ko ba mutuwa sune suke taimakonsu basa kukan rashi.

Ranar da akayi Sadakar Uku suka Kori kowa Suka ce Sunna sak ba zaman makoki ya Kare,Ranar Bash ya tafi gida ya Iske Mamansa tana Aiki yace Mama Yaran naki Mu bakwai kika Haifa Dan Allah Mama karki sake Haihuwa Haka,Mama ta kalle shi tayi murmushi Tace baka da kunya Bashir Ni kake gayawa Haka? Wato ka Sha ta maka yawa zaka zo ka min hauka ko? Bash yace Mama Naga darasi Yaran Nan Ni fa kuke haifawa kina ganin Yayana ba lafiyayye bane yanzu nine kamar Babba gashi Mama da kuruciyarki,Dake ita Maman Bash sai ka rantse ba ita ta haife su ba,Allah ya Bata kyan jiki karamin jiki gareta sai ka rantse Yayarsu ko kanwarsu,Bash yace Mama gobe Monday ki shirya zamu je asibiti ki duba abokina,Mama Tace Allah ya kaimu Bashir.

Washe gari da Sassafe Bash ya dauki Mama zuwa Asibiti,wajen Likita Mama taga sun shiga,Bash yace Likita gata na kawo maka ita akan Maganar da mukayi,yace matarka ce ko me? Kawai Bashir yace Matata ce, Maman Bash Dake akwai saukin Hali ba ruwanta yaranta Kamar abokanta tana kallo Bash yace a Mata Allurar Family planning Haihuwar ta Isa Haka,Likita yayiwa Mama tambayoyin da Suka Dace itama dama ta gaji da Haihuwar,Test aka Mata Bata da ciki Nan Likita yayiwa Maman Bash Allurar wata biyu,yace idan time ya cika ku

dawo Karku tsallake,Bash yace an gama,ya figi Mamansa a Machine suka dawo gida,Kuma Mama Bata fadawa mijinta ba sabo da Bash yace karki fada Masa kin San Baba Dan gargajiya ne sai dai yaga Shuru kin daina Haihuwa,daga yau Haihuwa ta Kare a gidan Nan sun Isa Haka, Mama tana ta dariyar su Bash.

Bayan Mutuwa ta lafa anyi Sadakar Bakwai Aamna yau kwana bakwai Bata ga Ahmad ba,duk ta Shiga damuwa ta Kira wayarsa Bata shiga,Bata San mutuwa aka musu ba,Shi kuwa Ahmad da dare Bayan sun Gama shaye shayensu da safe 7am ya koma gida, Mummy ya Kira a waya, yace Mummy Ina cikin wani Hali,danki ya fada soyayya jiya jiya na gano cewar Soyayya na fada,Farin ciki ya Kama Mummy Tace wannan wacce me sa'ar ce? Bata kawo Aamna bace tunda yace wata ce tasan da Aamna ce zai ce Aamna ce,ta so ace Aamna ce,Mummy Tace to itama tasan kana sonta ko me? Ahmad yace Mummy kwarjini take min na kasa fada Mata,zuciyata idan na ganta bugawa takeyi,Mummy Tace karka damu Son ka cire tsoro Kai fa Namiji ne ko wace kaje Ni na baka dama ka fada Mata duk irin son da kake mata,Ni Mummy Umarni na baka ka furta Mata karka ji tsoro,ta dinga zuga Ahmad tana dorashi a Kan hanya,suna Gama Wayar yaji wani kwarin gwiwar da Bai taba ji, yace Mummy ce ta bani Umarni,wannan Umarnin Mummy ne naje na fada Mata.

Ai zumbur Ahmad ya mike sanye da 3qutr blue da Riga Armless wata white and sky,ba Wani shiri ko wani wanka da canja Kaya na Kamala,lokacin zuciyarsa ta Gama tunzura, Kansa Kuma ba Wani saiti tunda jiya an cake da yawa,7am da sassaffe ya tsaya a Kofar gidan su Aamna ya Shiga dukan gidan Baji ba gani kamar zai balla musu gate,gaba dayansu a tsorace Suka yo waje Baba,Mama , Aamna tare da Siyama sabo da ranar Siyama a gidan su Aamna ta kwana,Baba Ne ya bude kofa,ko kulashi Ahmad Baiyi ba ya fada gidan a fusace da Masifa hankali a tashe Yana Bala'i ya tsaya a Gaban Aamna Dake tsaye sanye da kayan bacci ya nunata da yatsa da karfi a gigice ba nutsuwa Yana haki yace

Kin hanani sukuni...tun Sanda na ganki Bayan kin bar gidana kina shago...zu..zuciyata...ta kasa sukuni...Dora Hannu yayi aka ya sake nuna ta da yatsa da sauri da sauri yake magana ba kakkautawa Yana zaga compound din gidan Yana Wallahi na rantse.....ko idona na rufe bana bacci fuskarki nake gani kina min gizo....kullum idan na ganki zuciyata bugawa takeyi...Ina Jin tsoronki......ko yaushe bani da sukuni....burina kullum na ganki....ko naji muryarki.....bana...Bana Iya motsi sai da tunaninki......komai nakeyi kece a Raina....kece.... kike min gizo....sunanki idan aka ambata sai zuciyata ta buga.....Haka nake tsallakowa gidanku cikin dare in labe inyi ta kallonki.....Rannan ma Dan karku kamani nayi muku basaja na sace muku startime da Radio....Baba ya kurma Ihu tare da nuna Ahmad yace Kaine??......Ahmad Bai kulashi ba yaci gaba da bayani....yace kusan kullum da dare sai na shigo gidan Nan na ganki baki sani ba....har dakinki nake buya na Sha kallonki tsirara kin shiga wanka......da Ni kike rufe kofa a room Dinki duk abinda kike Yi Ina kallo....kunya ta lullube Aamna ta sunkuyar da Kai kasa.

Ci gaba yayi da bayani yace duk abinda nake Miki Dan kiji Dadi nakeyi.... komai Danke nakeyi....har zuwa shago Dan na ganki naji Dadi ne.....Yan....yanzu ma....zuciyata bugawa takeyi wallahi Ina sonki....sonki nake Yi...da ban Gane sonki nakeyi ba sai yanzu.....Murya ya

canja Kamar me kuka ya hada zufa Yana haki yace Yan....yanzu....ma tunda nazo gabanki zuciyata Bugawa takeyi.....idan Baki yarda ba taba kurjina kiji ya cafko Hannun Aamna ya daura a kirjinsa saitin zuciyarsa yace kinji?...kinji?....Aamna Tace ae naji ta zame Hannunta.....Siyama,Mama,da Baba suna ta tabe Masa Baki sabo da basa son abin,shi kuwa Bata su yake ba ci gaba yayi da cewa Wallahi Allah Sonki nakeyi......idan Baki yarda ba Kira number ta kiga sunan Dana saka Miki a Kan number dinki,Aamna ba musu ta latsa Wayarta ta Kira wayarsa sai ga Sunan Daya sa Mata ya Bayyana MY WORLD.

Bai tsaya ba yaci gaba da bayani Yana tonawa Kansa asiri Wai duk cikin bayyana soyayyarsa a gareta ne.

KARSHEN FREE PAGE

ASMABAFFA.
10/26/21, 8:53 AM - A Maryam: P🌵🌵 DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

NA KUDI NE

DAN ALLAH KARKI FITAR DA NOVEL DIN NAN BADAN NI BA DAN GIRMAN ALLAH, IDAN BAKI BIYA BA KARKI KARANTA DAN DARAJAR ALLAH.

DUNIYA TA AAMNA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

55-60

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne mutanena Yan Albarka

UMMI DEEJAT
ALHUSNA

Yace nine....Nine.....Ni ....ya rasa me zai ce ma karshe yace Ni...dai Dan Allah Ina sonki kinji....kinji....ya kafe ta da Ido Kamar zaiyi kuka,Mama ce tace ai taji ka kaje kawai....kallon Aamna yayi yace na tafi kawai? Ae jeka cewar Baba,yace Kawai? Suka ce ae jeka zata baka amsa daga baya,shi Kam tuni yaji zuciyarsa wasai tunda ya amayar da abinda ya dame shi sai Kawai ya juya ya tafi abinsa zuciyarsa Kuma na tsoron amsar Aamna da zata bashi Nan gaba,Haka ya koma hankalinsa ya kwanta ko Bata ce tana sonsa ba ya fada Mata sakon zuciyarsa.

Gaba Daya ya samu su Mashkoor a gidan su Bash,yace to yau dai anyi ta Ta Kare yau na bayyana Mata,Ihu Suka saki na murna tare da tambayar me Tace? Yace Wai zata bani amsa daga baya,Tagumi Suka Yi Suka ce zaman makoki Bai Kare ba,Yarinyar Nan da raini take kamarka kace kana sonta Tace wani sai Nan gaba ma zata bada amsa,Gaskiya Aunty Balaraba Bata Yi ba sam,Nima Ina tsoron lamarin Nan cewar Mashkoor yarinya tsigigiya duk ta gigita Mana Kai,Ahmad yace wallahi Ni kaina zagin kaina da kaina nakeyi,kullum sai na shiga daki na tsinewa kaina sannan na fito,wannan abin tsinuwa ne Man cewar Tawaga.

Aamna kuwa Bayan ya tafi Mama Tace masifa wannan wanne irin tsagera ne Haka ba ko kunya bare Kara,Baba yace Yaran karshen tashin alkiyama ne in Banda tambadewa kai mtswww Baba Yaja Tsaki,Siyama kuwa ranta yau idan yayi dubu ya baci,kallon Aamna tayi Tace Kar dai ki Kai kanki hallaka wallahi,Mama Tace Idan taje ya kasheta ai ita ta huta da Duniya Dan wannan zai iya yiwa mutum yankan rago,Aamna ce ta kalle su Tace ba Wanda zai fada min abinda ya kamata nayi,Ni matar aure ce Kuma matarsa,sannan Ni na San dai dai sabo da Haka ba sonsa zanyi ba taimakonsa zanyi na taimaki Iyayensa idan ya shiryu shike Nan sai na barshi,Zuhra ce tayi Sallama ta shigo ta Iske zancen, Siyama tana tabe Baki tana bada labari,Zuhra tayi murmushi Tace mashaallah Alhmdllh,Ke Aamna wallahi idan Zaki so abinki ki so shi tsakanin da Allah,ba'a Wasa da zuciyar mutum musamman Daya zurfafa Haka wallahi idan kika yarda bayan kin San ba sonsa kike Yi ba wallahi Kinga yanda yake zai iya komai,mijinki ne ki so abinki ki koma ki zauna lafiya,ke da Allah ya taimakeki ma iya shaye shaye ya tsaya baya Neman Mata da sauransu,karki Raina Masa hankali baza kiji da Dadi ba na Nan gaba,kiyi amfani da ilimin.....ke dalla rufe Mana Baki banza Shashasha cewar Baba,so kike ya kashe ta,ai Ni abinda nake so yanzu ta Amince Masa Kamar gaske sai mu samu mu

dinga zarar kudi a jikinsa inda ya makance a kanki Haka nasan har aikin hajji sai ya kaimu,Zuhra Tace haba Baba haba Bai kamata ba,zuwa Makkah Dole ne?, Kuna cikin rufin asiri Iyayensa sun Gama muku komai a rayuwa,Baku da Muhalli Suka Baku Muhalli,Muna cikin talauci Suka fitar damu daga wannan gashi Kuna cikin rufin asiri,ci,Sha,sutura duk kunfi karfinsu Amma Baku godewa Allah ba.

Hannunta ya rike tare da janta kitchen,Suna Shiga ya dauke ta tare da daura ta a sama kusa da Sink,hannayensa bisa cinyoyinta yace Zan fara girkin kina kallo kinji,Kallonsa takeyi ba ji ba gani Wani Farin ciki takeji,Jikinta ne taji Yana wani yam..yam,Yana magana Amma shi take kallo,a hankali ta matso da fuskarta saitin tasa da Niyyar Masa kiss har ya wani lumshe Ido da sauri ta dawo hayyacinta sai ta fara wayancewa tana dariya,Sharewa yayi shima ya fara girkin,ita Kuma tana ta faman kallonsa,Sai da Yamma ta ebi abincin a flask ta tafi da shi gida Wai yayi Dadi.

Shi kuwa Karamar jaka ya dauka tare da shirya kayansa, Mashkoor ne ya kaishi Airport,sanye yake cikin wata Gezna Sea blue,Fadin kyan da yayi Bata Baki ne,kitsonsa dai Yana nan,Da Yamma 5pm Mummy tana zaune a katafaren palonta tare da Humaira sai gashi ya buga Sallama,Mummy da tsananin mamaki Tace Ahmad nake gani ko wa? Dariya ya saki ya tsaya a Gaban Mummy ya wani juya ya juyo tare da yin safa da Marwa a Gaban Mummy yace ya kika ce Mummy,Mummy Tace Wai Kaine da gaske? Shekara Nawa Muna fama da Kai kazo ma gida kaki sai yau Katsam,Yace dama surprise na muku shi yasa naki fada muku,Mummy Tace uhm Kaine kake magana Haka a nutse Kuma cikin shigar hausawa wow,Humaira sabo da murna harda tsalle ta Rungume shi tana Sannu da zuwa Yaya,Yace sis kin Kara girma fa,Mummy ya Rungume tare da aniye jakarsa a gefe,Mummy Tace Humaira sauri ki Kira Daddy kice yazo ga Ahmad yazo yaga abin mamaki,Zama Ahmad yayi kusa da Mummy.

Daddy ne ya fito tare da tambaya me Zan gani Ahmad Yau Kaine a Lagos? Abin mamaki kaine,Dariya Ahmad yayi tare da mikewa ya wani sarawa Daddy Kamar Yana Gaban babban

soja yace Daddy nine Mana,Sabo da farin ciki Daddy Rungume shi yayi yace Dole yau muyi Celebration yau King Guda a Nan gidan,Daddy gwada yanda suke magana ta Niggogi yayi yace Fresh Boy,the King of Guys Ahmad yace yes ooooo na me,Daddy Yace aje a shirya girki yau Ranar murna ce,a Kira Saddeeq da Mufeeda su zo,Haka aka shirya girki iri iri suka zauna a Dining Saddeeq,Mufeeda,Ahmad, Mummy,Daddy da Humaira Ana ci Ana Hira Ahmad ya fara Basu labarin Aamna,Mummy Tace dama Aamna ce? Gaskiya nayi murna.

Ahmad Yana cin abinci yace Ina Baku labari da kuke gani na Haka harfa masallaci nake zuwa Sallah, Saddeeq cikin murna yace Inyeee, Mashaallah cewar Daddy,Ahmad yace Kuma shaye shayen da nake Yi duk na rage saura kadan shima Zan daina Nan gaba,Mummy Tace Alhmdllh,Ya daki kafadar Sadeeq yace ae naji Dole na fada gaskiya Daddy Yarinyar Nan Ina sonta duk ta canja Ni abinda nakeyi duk na rage Ina ta Zama mutumin kirki kullum,Humaira harda tafin Jin dadi,Daddy yace duk itace tayi aikin Nan Wanda munyi shekara da shekaru mun kasa,Ahmad yace sosai itace Kai Daddy Haka idan time din Sallah yayi zata kirani a waya,Muryarsa ya makale Wai irin muryar Aamna zai gwada musu Tace Kaje kayi Sallah a Jam'i Babyna,Ni Kuma idan banje ba sai naga Kamar ma ba sonta nakeyi ba sai na tafi,ai Sanda Sonta ya kamani Daddy na Sha fama,lokacin Baku ga danku ba,susucewa fa nayi,Dariya suka saki,Mummy tace gaskiya tayi Aiki,yace Bari na Kira muku ita kuyi Mata godiya,Nan take ya Kira Aamna ta daga yace kunji zakin muryarta ya saka Wayar a Handsfree kowa na ji Aamna Tace Babyna kaje lafiya,Mummy ya kalla yace a hankali kunji kunji ko yanda take ji dani, Saddeeq ya kalla yace ji Murya dan Allah,Dariya Saddeeq yayi yace to anji,Mummy ce ta karbi Wayar Suka gaisa da Aamna ta dinga zuba Mata godiya da Addua,Daddy ma yace bani ita nima,Haka su Humaira da Mufida tare da Saddeeq duk sun Mata godiya.

Ahmad Wayar ya kashe yace Kuma k
Ullum dare muke rabawa Muna waya,Babu kalmar Dake tsaya min a Rai irin idan zamuyi bacci Tace Sweet Dreams Baby har dodon kunne na sai yayi rawa Karrrrr....Dariya suke ta Sha Yana ta Basu labarin komai dama ba kunya yake ji ba,karshe yace gaskiya Maganar Serious Yarinyar Nan kuyi Mata gagarumar kyauta sannan kuje har gida ku gode Mata.

Daddy Yana dariya yace zamu je ne sai Nan gaba,yanzu tunda ka gyara halinka kuje da Saddeeq wurin siyan mota ka zabi motoci ko Nawa kake so sababbi Zan siya maka,wancen Dana kwace sun tsufa latest zaka zaba,yace thanks Daddy.

Tunda Ahmad yaje suke Shan labarin Aamna kullum,har kwanakin Daya kwasa Suka cika,Mota Daya tal ya zaba wata muguwar jibgegiya me tsada baka,kowa yaga motar yasan ka hau mota,kafin ya dawo an kawo motar Kd an hadata an Mata duk abinda yake bukata,Su Jibson sai murna suke Yi.

Ranar da ya dawo Kd Bai je wajen Aamna ba sai washe gari ya dau uban wanka cikin wani black trouser pencil da rigarsa me dogon Hannu,Irin kyan Daya zuba ba a magana,Sabo da Iya shege su Baba suna tsakar gida sai gani sukayi Ahmad ya shigo ya Bude gate da Kansa ya koma ya shigo da wata azababbiyar mota,Dukkansu tsaye suka Mike har Aamna Dake Shanya wanki,Mama tana gefe,Idonsa ya rufe ya manta Yana Fitowa daga motar ya Rungume Aamna,itama Haka ta kankame shi suka ki sakin juna,sai da Baba yayi Gyaran Murya,Sannan

Ahmad da borin kunya yace na manta ban kula ba Sannan ya rusuna ya gaisar da su,Mamaki ya Kama su Mama bayan gaisuwa harda rusunawa  mutumin da ko kallo Basu ishe ba,Baki Mama ta tabe,Aamna ta kalli motar Tace wannan fa? Yace au mota? Yace dama Ina da su da yawa ma Baba ne ya kwace Dana ki shiryuwa,Murmushi Aamna tayi Tace tayi kyau,ko kina sonta ya tambaya,Tace a'a ai kayanka Kamar Nawa,idan kina so ki fada min sai na bar Miki ita,Aamna Tace na gode Baba ya galla Mata Harara Yaja kwafa ta musu asarar mota,je ki shirya muje yawo,Aamna da sauri Tace to tana murna taje ta cakare ta fito cikin Atamfa taji dinki cif ita,Da Kansa ya Bude Mata mota ta Shiga sannan ya rufe suka tafi,Wuraren hutawa sukaje suka dinga holewa Suma idan ka gansu abin sha'awa.

Tunda ya dawo kusan kullum sai ya Kai Aamna Wuraren hutawa,Haka Siyayyar kayan birgewa ko yaushe Yana dawainiya da ita.

Bangaren su Jibson kuwa bayan sun bar wajen Sameera sai bayan sati Daya Sameera ta Basu damar komawa,Wannan time din harda kaisu wani palon Baki,Bash ya kalli Jibson suka Yi Signa, Sameera ta dau wanka Kai sai ka rantse Bata taba aure ba,Lemo ta kawo musu da ruwa ta zauna,Jibson yace me Hannun karfe da Alama na jefa na cafke,Dariya Sameera tayi tace ae,Jibson yace to ya Maganar Dattijon naki? Sameera Tace na daga Masa red card,Jibson yace kin birge ni ai tsoho sai tsohuwa,Bash yace sai na dinga hango ku a High table Ana wedding Dinner,Cikin rashin sa'a sai ga Baban Brown yazo zance shima ya Sha shaddarsa tare da wani Dattijo abokinsa,Baban Sameera dake abokansa ne Direct palon ya shigar da su sabo da Bai San da Baki ba,ai suna shiga Suka yi Ido hudu da su Jibson suna ta Hira da Nishadi,Baban Sameera yace ai ban San da Baki ba Nan ya janye su Baban Brown suka koma dakinsa,Jibson ya kalli Bash suka kyafta ido,sai Suka Mike suka Mata Sallama suka tafi da sauri,Shima Baban Brown cike da bacin Rai ya tafi gida tare da Kiran Mubaraq yace lallai su zo tare da su Jibson,Babu Bata lokaci Brown,Jibson da Bash Suka Amsa kiransa,suna zuwa ya dinga bala'i yace Dan wulakanci Baku San bazawara ta bace? Jibson yace yo Baba Allura cikin ruwa me Rabo ka dauka,tunda Nema kakeyi muma shi Muka je.
Mene zaka damu?

Brown yace Baba Kamar takara ne Kuma cikinku duk Wanda ya same ta murna zanyi sabo da idan Kaine zanji Dadi tunda Baba nane,idan su ne Kuma abokai nane, ai takarace ku gwabza Kawai Wanda ya lashe zabe muje muyi Masa Allah Sanya Alkhairi,Dattijon yace okay Wato na gano ku shi yasa Yarinyar ta juya min baya,idan naje Bata saurarata Ashe kune kuke hure Mata kunne,Bash yace au Baba ta fara juya Maka baya? Baba bai San murna zasuyi ba yace ae Mana,ta daina kulani ko naje sai Harara,Ihu Bash yayi yau akwai Party za Sha Zanku dance,mun lashe zabe,Baba yace zanyi maganinku nasan me zanyi ku tafi ku bani waje mutanen banza lalatattu masu takara da ubansu,Kai kuma Mubaraq Wato abokai sunfi uba ko zaka zo ka sameni,tafiya Suka Yi suna ta dariya an Juyawa Abba baya.

Ahmad kuwa yau Saturday Shiryawa yayi ya jibgowa Aamna siyayyar kayan makulashe zai je,Lokacin 5pm Zuhra ta zo da Siyama ga Mama a zaune suna Hira,Ahmad yazo Kofar palon hannunsa dauke da ledar take away,zai shiga kenan sai ya tsaya cak Jin an Kira sunansa Siyama Tace Aamna baza ki hakura da Auren mutumin Nan ba,tunda kin Gama chanjashi ki

kyale shi Haka,Aamna Tace ai Bai Gama shiryuwa ba,jira nake sai na Gama canja shi gaba Daya sai na zare jiki na,Siyama Tace yanzu shine ya kamata ki zare jikinki,Zuhra Tace Aamna Baki da hankali wallahi dabba ce ke wallahi Baki San me kike Yi ba Kuma duk da kin girmeni, Ae naji Ni dama Dan na canja shi ya shiryu na Amince da soyayyarsa Kuma ai na taimaki Iyayensa,Ahmad ya Gama ji tsaf,Nan take zuciyarsa ta hau Bugawa da karfi,hankalinsa ya tashi,Idonsa ne yayi ja sosai,jijiyoyinsa Suka firfito,kasa hakura yayi gwara ta San yaji,Palon ya banko kofa da karfin ya shigo ciki, duk suka juya a tsorace suna Kallonsa.

Wani haki yakeyi da huci Kamar zai mutu duk sai da suka tsorata,Aamna wacce tuni ta fara kuka sabo da ta tabbatar yaji me suke tattaunawa,Bata taba nadama irin wannan ba a rayuwa,Kallonta yayi Idonsa ya ciko da kwalla Yana Ina Ina duk ya rude yace ki fada min abinda naji kina fada yanzu karya ne,cikin karaji yace kice mafarki nakeyi,kice karya ne abinda naji....Aamna tana Rusa Kuka Tace tsaya tsaya Zan maka bayani,cikin tsantsan tashin hankali yace bayanin banza,me Zaki fada min,me Zaki fada min,Kansa ya nuna yace Ni...Ni.....Wai Ni kika yiwa Haka....kin San karya ne kika ce kina so na?...sai da kika dagani sama sannan kika sake Ni na Fado....me na Miki Haka?....Wai duk abinda nake Yi a kanki ?...kujera ya daka da karfi yace Bari kiji Ina mugun kaunar Mummy na fiye da komai a duniya Amma duk abinda Tace nayi bana Yi,Amma ke duk abinda kika ce sai nayi,sanadinki yanzu Sallah Bata wuce Ni,Shaye shaye sabo da na faranta Miki na daina.....Amma....Amma....rasa me zaice yayi Idonsa ya zubo da Hawaye yace tunda na San kaina ban taba zubar da Hawaye ba sai yau kika sani Yana magana cikin karaji duk ya girgiza su ya haukace musu gaba Daya,Mikewa Aamna tayi tana kuka Tace wall....

Cikin tsawa yace bana bukatar bayaninki Ledar Dake hannunsa ya watsa saman kujera,Laptop sabuwa me tsada ta fado daga cikin Ledar Ashe ita ya siyo Mata da kayan tande tande,Bude kofa yayi ya fice a fusace, Aamna tana kuka ta bishi da gudu tana kiransa,Siyama ta riketa Tace ki kyaleshi ke gaba ta kaiki sai ki zare kanki cikin sauki,Aamna ta fisge Hannunta Tace Ni wallahi Ina sonsa da gaske wayyo Allah na Ni na shiga Uku ta zauna ta shiga Rusa uban kuka ba ji ba gani,Zuhra Tace kinwa kanki sai ki samu Wanda ya fishi mu gani,Aikin banza tayi tafiyarta gida itama,Siyama kuwa sai murna a ranta Haka ta tafi gida abinta cike da nishadi.
Mama ita kanta yau tausayin Ahmad ya kamata matuka Ashe yayi nisa a shiryuwa Aamna Bata sani ba ma,wajen Aamna Mama taje tana lallashinta,Aamna tana kuka Tace wallahi Mama Ina sonsa wallahi Allah Siyama ce kullum take zugani zuciyata ta kasa tsaiwa waje Daya,na shiga Uku na lalace Mama,Mama Tace kiyi Hakuri Inshaallah zai dawo ne.

Bangaren Ahmad kuwa dama Mashkoor ne ya ajiyeshi a motar ya tafi yawo zaizo ya dauke shi,Kawai a kafa ya dinga tafiya ba tare ma da yasan Ina ya nufe ba,sai da yayi tafiya me nisa sannan ya shiga Napep direct Gidan Mashkoor aka ajiye shi,shiga yayi Yana Jan kafarsa da kyar jikinsa a sake,duk sai da suka tsorata ganinsa haka,Kansa a kasa ya nemi waje ya zauna ba tare da ya kalli kowa ba yayi Shuru,Kallon kallo su Jibson suka shiga Yi,kwalabar giya Tawaga ya Mika masa,ba musu ya karba ya kwankwada Yana goge Dan hawayen idonsa,Suna ta Kallonsa Yana Hawaye,Tawaga yace Wai me ya faru ko Mummy ce ta rasu? Shuru ya musu, Mashkoor yace bamu taba ganinka cikin wannan yanayi ba me ya faru ne King? Bama son

kukanka King cewar Bash,King a hankali yace Kun san dai yanda nake son Yarinyar Nan ko? Suka ce ae,Yace Kuma kunga yanda ta nuna min kauna,Suka ce ae Mun sani,yace to Kuma dai Kun ganni kalata ba kowa ke samun Irina ba ko? Suka ce ae,yace Kuma nine King,Suka yes Mana,yace kunga irin yanda nake fama da ita ta dawo gidana Taki Amma na hakura na barta sabo da Ina jira ta Gama abinda zata Yi sai ta dawo,to Wai duk Ashe Tace ba Sona takeyi ba Kawai ta karbi soyayyata Dan ta canja Ni na shiryu na daina shaye shaye,Ihu Suka saki,Bash yace that girl?,Yace yeah,yanzu Ni kudi ne da zata canja Ni? Suka ce a'a,yace to Tace canja Ni Kawai zata Yi na dawo mutumin kirki,Tawaga yace Yarinyar da Bata da ko nonon kirki ga Yan Mata Nan suna rubibinka Amma Aunty Balaraba zata maka Haka?

Jibson yace Ni dama Sam ban yarda da ita ba,Kawai ka bamu Dama mu tozartata a garin Nan, Mashkoor yace sai Dana fada maka kayi hankali da Mata yanzu ka bamu Dama muci ubanta,Ahmad yace Kuna ji na? Suka ce ae,yace ku bar min case din Ni zanyi Handling dinsa sabo da matatace baza ku Shiga zancen ba ku barni da ita,Shuru sukayi suna jimami kawai suna Kora shaye shayensu.

Aamna kuwa kwana tayi tana Rusa Kuka ko gajiya Bata yi,Baba ma da yaji labarin yafi Jin tausayin Ahmad akan Aamna,lallashin duniya Aamna Taki hakura Sai Kiran Wayar Ahmad takeyi yaki dagawa,a daren ta kirashi yafi Sau dari,Daya gaji ma kashe wayar yayi gaba Daya.

Sharhi sharhi fans.

AsmaBaffa

10/26/21, 8:53 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

NA KUDI NE

DAN GIRMAN ALLAH KARKI FITAR DA NOVEL DIN NAN.

DUNIYATA AAMNA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

66-70

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne

MAMU GALADIMA
BESTYNBEELAT
AISHA
MAMAN SAMHA
HAFSEE

Ranar Bai iya ko gyangyadi ba bare wani bacci Yana ta tunani,saman bed dinsa Kawai ya dawo ya kwanta shi kadai yasan irin radadin da yake ji a ransa,Aamna ma tana rike da waya Haka bata Yi bacci ba Haka gari ya waye,washe gari da safe ba yanda Mama batayi da ita ba akan taci abinci Amma Taki ci ko wanka Bata Yi ba sai kuka Kawai,Hijab ta zura ta tafi gidan Zuhra,tana Shiga gidan Zuhra tana mopping Aamna ta fada jikinta tare da fashewa da sabon kuka,Zuhra taji tausayinta Tace Aamna kiyi Hakuri Kar wani ciwon ya shigeki,Aamna tana kuka Tace Ni ya dawo, Taya Zan huce ya yafe min ya dawo?, Zuhra ta kalleta yanda dare daya ta firgice,Zama sukayi a saman kujera Zuhra ta Shiga lallashin Aamna da kyar ta samu ta daina kukan Amma duk da Haka idan ta Lula tunani sai sabon kuka.

Bangaren Ahmad kuwa Shaye shayen ma idan yayi baya Jin dadinsa ko kadan Haka ya hakura sannan Sallah Bai fasa zuwa masallacin ba,abokansa kuwa gaba Daya Suma sun tsaya cik sabo da halin da abokinsu ke ciki,suna ta tayashi bacin rai,barinsa suka Yi shi kadai sabo da kadaicin yake bukata,kwance yake shi kadai Yana tunanin mafita sai ga Jibson ya shigo tare da Siyama wacce taci shegen gayu,a saman kujera Suka Iske Ahmad Yana kwance Yana tunani duk ya fita a hayyacinsa,Jibson ya kalli abokinsa da tausayawa yace King gata fa Kawai ka so

wannan tunda Aunty Balaraba ta ki ka,Ahmad fuskar Nan ba Rahma ya kalli Siyama yace Jibson Haka za ayi,Jibson ya fita abinsa ya rage daga Siyama sai Ahmad,tana ta faman karairaya tana fari da Ido,ta durkusa a gabansa Tace Ina sonka Ahmad,na Dade Ina kaunarka Matukar zaka so ni ba abinda bazan maka ba,har kaina Zan Iya mallaka maka,Ahmad kwata kwata hankalinsa baya jikinsa Haka Yace ba damuwa Ina sonki kinyi tashi ki tafi, gobe Jibi 10am kizo,Siyama farin ciki ya kamata harda godiya,Tsaki Yaja yace Jeki sai jibi,tashi tayi tana murna ta tafi.

Kamar Yanda yace Jibi sai ga Siyama 10am ta wani dau wanka duk ta matse jikinta ta zo,Ahmad ya fito sanye da Jallabiyya Suka fita a motarsa har bakin shagon Aamna lokacin Mama sun gaji da kukan Aamna gwara ma tazo shagon ko ta rage tunani,Aamna tana bakin shagon tare da Zuhra suna magana kawai taga motar Ahmad tayi parking a Bakin wajen,Fitowa yayi sai taga Siyama ta fito tare da rike Hannun Ahmad,har Gaban Aamna suka karaso ransa a bace ya kalli Aamna Yace kalli ya kika gani Yarinyar da tasa kika wulakantani kalle ta yanzu har gida take bina tana rokata akan na so ta,har gida take zuwa lokacin kina gidana take Neman na so ta,akanta kika min Haka to gashi roko na takeyi na sota,Siyama murna ta koma ciki Bata Yi zaton tona mata asiri zaiyi ba,Tace Honey ya Haka zaka Tona min asiri,Zuhra da Aamna Suka saki Baki galalala,Tsawa Ahmad ya dakawa Siyama yace ke dalla rufe Mana Baki,Baki da hankali amfani nayi da ke sabo da tana gadara kekawarta ce ta gari,kece me Bata shawara,kallon Aamna yayi yace Dan kince Baki so na cikin minti Daya zanyi mata kala kala Wanda zasu so ni,idan nayi Niyyar saurarar Mata cikin mintuna Kamar Riga Haka Zan na canja su,ke tunaninki har mace ce,Siyama ranta ya baci ta juya cike da borin kunya ta bar wajen sum sum.

Wata dalleliyar motar ce ta tsaya a jikin ta Ahmad,budurwa ce fara Yar gayu ta ko Ina tayi karshe ta karaso tare da tsayawa a Gaban Ahmad Tace Sweetheart kazo mu tafi motarka Zan Shiga kasa Musa ya maida min tawa ita a gidanka,Ahmad ya kalli Aamna yace kin gani idan kin kini cikin lokaci kankani Zan samu Wanda suka fiki komai,ya nuna Budurwar yace wannan idan Ilimi kike takama PhD ne da ita sannan me kudi ce ke gidanku ko Tyre ta mota Kuna da ita? Me kukeyi in Banda Siyar da citta,Ahmad Kamar Bai San Aamna ba Haka ya tsaya ya ci Mata mutunci tas sannan ya samu zuciyarsa tayi sanyi,Budurwar Yar gayu ita ce ta rike Hannun Ahmad suka tafi,Aamna tana tsaye sunyi mutuwar tsaye da Zuhra sai Hawaye da ya wankewa Aamna fuska,Kuka ta barke da shi me karfi lokacin da taga Ahmad sunja mota sun tafi,Zuhra Tace ya Miki kyau Aamna Kinga abinda nake fada Miki,Baki ji me yace  Miki ba in a minute zai iya canja Wanda suka fiki kala kala,Mata rubibin irinsa sukeyi Kuma gaskiya ne,yanzu kalli dalleliyar Budurwar data ke like Masa,kalli kawar taki Siyama da kike takama da ita,itace ta Kai kanta tana rokonsa ya so ta,amma a gabanki me Tace? Aamna cikin kuka Tace Bazan yafewa Siyama ba,Kina gani Zuhra ya tafi gidansa da wannan kyakyawar Budurwar gidansa shike Nan kwana zasuyi tare,Zuhra Tace mene damuwarki tunda kince ba sonsa kike ba canja shi zakiyi,Aamna ta sake fashewa da sabon kuka Tace wallahi.....Zuhra....Ina sonsa......Ina....sonsa...I love him....I love him....Siyama ce take nuna min Illar auren me shaye shaye shi yasa zuciyata ta kasa tsayawa,to ai gashi ita yanzu ta nuna Miki iyakarki,tunda Dan shaye shaye ne shashasha Mene Zaki damu? Aamna da Matukar bala'i Tace Ahmad Dina ba

shashasha bane ta ja tsaki tayi cikin Shagon tana ta uban kuka,Zuhra tana ta dariya ta bita ciki Tace to kiyi Hakuri Yana sonki har yanzu Bai daina ba ai kinfi ma wacce yazo da ita kyau,kin fita komai,Aamna Ido yayi jajir Tace gashi Nan ya tafi da ita gidansa,Ni wallahi komawa zanyi gidan Mijina duk Ni na cuci kaina,Zuhra tana ta dariya Tace wallahi karki koma yanzu yanda yake Fushi da ke kika je zai iya Miki Illa gwara ki Bari ya huce,Aamna Tace da abinda yake min ba gwara kullum ya dinga min Bulala Hamsim ba,Zuhra tana Dariya Tace au yanzu dukansa ma sonsa kikeyi?Aamna Tace ae dadinsa zanji Indai ya hakura to yayi ta duka na kullum har durkusawa zanyi na gode Masa.

Suna zaune wata tazo siyan Citta Aamna tana ta tunanin Ahmad sai ta zuba Mata barkono,sai da ta karba Tace citta fa nace,Aamna Tace au na manta sai ta juye ta zuba mata kanunfari,Matar Tace Citta fa tunanin me kikeyi Haka ne,Sai Zuhra ce tazo ta karba ta zuba Mata,wani yazo ya siyo Wani Boxers sai Aamna ta karbi kudin dari biyar ne Kuma dari biyar din ya Bata Amma sai ta irgo dari takwas ta bashi tace ga canjinka lokacin Zuhra ta tafi shi kuwa mutumin ya sani Amma ya karbe abinsa yayi gaba.

Kusan kwana Uku Aamna duk ribar Mama ta tafi Aamna tana ta yin aringizon kudi.

Yau ma da safe zata hada tea a kitchen sai ta dakko gishiri ta saka a madadin sugar sai da ta kurba ta feso da shayin waje sai taga gashiri ne,gaba Daya Bata cikin hayyacinta.

Ahmad Kam abokansa suna zuwa suna ebe Masa kewa,Jibson ne ya shigo ya same su tun kafin ya zauna yace ku fara Yi min jaje, Mashkoor yace na me? yace ku tausaya min suka ce Mene? Jibson yace Jiya kafin na kwanta bacci 9:30pm, Allah yaji Kan Sameera me Hannun kwano badan ta mutu ba sai Kawai na dinga ganin fatalwarta a kaina,tsorata nayi na Kira Wayarta a daren tunanina ta rasu ne an binneta tayi min fatalwa.

Sai kuwa ta daga tace ita kalau take Nan na gano mayya ce zata kamani nayi Mata fata fata nace Kar ta sake na sake ganinta a Ido na,Dariya suka dinga Yi,Jibson yace Kasurgumar mayya ce ban sani ba,na Kai kaina babu dama na Dan kebe Ni kadai sai ta dinga min fatalwa, Jibson yace yanzu ma Haka Ina ganinta a idona,Bash yace ko dai so ne? Jibson yace Bazawarar Allah kiyaye,Idonsa ya Shiga murzawa yace gata tazo... tazo bazan lamunci wannan ba idan na gaji Kara Zan shigar kotu Mayya ta kamani,Tawaga yace Wai da gaske kake?yace ae Mana, Mashkoor yace kirata a waya muji,Jibson ya dakko waya tare da Kiran Sameera,bugu Daya ta daga.

Yace ke Kwano Mene Haka bana son wasan da kike min,gaskiya na daina ganinki Maganar gaskiya Ina daga Miki kafa Zan kaiki Kara akan me Zan dinga ganinki,ko bacci nayi sai kizo min Mene Haka Dan Allah Ni bana so Gaskiya,Dariya Sameera tayi ya dameta da zargi Wai ita mayya ce Bayan ita Bata San komai ba,tsokanarsa tayi Tace Yau Danwake kaci ko? Tsoro ya Kama Jibson sabo da Tabbas yau Danwake kannensa suka Yi a gidan Kuma sai da yaci ya fito,da sauri ya kashe wayarsa su Tawaga Suka dinga dariya Jibson yace ba abin Dariya bane wannan wallahi Danwake naci na fito idan ba mayya ba Taya tasan naci Danwake? Gaskiya a Nemo min maganin mayu wallahi,Bari Brown yazo Dan Uwarsa ya sa munje wajen Mayya,Suna ta dariya Bash yace Ashe duk wankan da muke dauka a banza tana kallon Hanjin mu me muka

ci,Jibson da sauri yace Kuma ranar tuwo naci kaga zata kalle Ni a banza Ina cin tuwo,da ace nasan Haka ne ai Kwai da nama zamu ci idan munje ta ganmu Yan gayu,yanzu ta ganmu cikinmu duk tuwo,Bash yace kyaleta anjima zamu je kaza zamu siyo muci muje Suka ce Haka za ayi su Ahmad suna jinsu suna ta dariya,Amma Ahmad duk da Haka hankalinsa Yana wani wajen.

Da Yamma su Jibson kazar kuwa Suka siyo Suka ci harda Shan Yogourt,Bash yace Bari na Kara da Biscuits sabo da ta ganmu muma ba baya bane,Jibson yace Apple zanci Ni Haka Suka dinga Ciye ciye su Tawaga suna ta dariya,yau da Sameera ta shigar da su Palon Baki kallonsu tayi Tace Bari na kawo muku lemo ko da yake nasan kunyi ciye ciye da yawa,Bash da sauri ya kalli Jibson,Jibson tsoro ya kamashi yace Wai ke Kwano Taki da ita aka haife ki ko kuwa siyanta kika Yi? Sameera ta Gama Gane shi Amma sai Tace me fa? Kasa fada yayi Dan kar ya ci Mata Fuska sai yayi Shuru kawai,Sameera ta fita a ranta tana ta dariya Bash ne yace ai ance ta bangaren Uwa tafi karfi Wala Allah ita a nono ta Sha,Abban Brown ne yazo zance yau ma yaga su Jibson Ashe Basu daina zuwa ba,Takaici yasa ya shiga palon shima ya nemi wuri ya zauna sabo da shima Abban Dan rigima ne baya tsoron abin kunya gashi ya makance Akan son Sameera,Su Jibson Suma suka ki tashi mirsisi sukayi,Abban Yana ta harararsu Suka share abinsu,Sameera ta fito tare da ajiyewa su Jibson lemo ta zauna tare da maida hankalinta wajen su Jibson,Abba ko Kallonsa Bata Yi ba,kwafa ya ja ya Mike ya fice Kamar zaiyi duka.
Su kuwa sai magrib sannan Suka tafi.

Bayan Kwana biyu duka abokan Ahmad na kusa Mashkoor, Jibson,Bash,Tawaga da Brown wajen Ahmad Suka zo,Brown yace Ahmad ka shirya muje daurin auren Cousin Dina a Kano gobe,Ahmad yace a halin da nake ciki bazan iya binku ba ga motar Nan ku dauka kuje da ita koma Ina ne ai komai Nawa naku ne,Suka ce to ba damuwa,washe gari da Sassafe Suka shirya tare da tafiya Kano,Ahmad da Rana Yana kwance Yana ta tunani iri iri akan abinda Aamna ta Masa sai ga kiran Wayar Mashkoor sabo da shine Kawai Suka Yi waya yanzu yanzu,Yana dagawa akace masu wannan motar sunyi hatsari ayi sauri azo Kan gawarsu gaba Daya sun mutu na Daya motar ne babu Wanda ya mutu suna asibiti,Zumbur Ahmad ya mike tuni ya rasa inda zai sa Kansa,yanzu abokan nasa ne suka Suka mutu? Kayan dakinsa ya shiga watsi dasu.

Kuka Kawai ya fara ya rude Kawai Iyayensu ya Kira ya sanarwa kowa hankalinsa ya tashi ko wanne danginsa Suka tafi can inda akace anyi hatsarin,Shi kuwa Ahmad a rude ya Kira Mummy ya fada mata,Yana kashe wayarsa ya fita shima ya bazama,tare da Baban Jibson Suka tafi can hanyar Kano,Suna zuwa Suka hango Yan Sanda da mutane da yawa a wajen Ana ta zaro gawarwaki,motar Ahmad gaba Daya tayi fata fata,da gani yawan gawarwakin Ahmad ya Fadi ya sume yin duniya Bai farfado ba,da shi aka hada aka tafi Asibitin da Wanda Basu mutu ba,Daya motar ita bata wani lalace sosai ba da gani kasan a motar Ahmad sune Wanda Suka mutu Kawai.

Duka Emergency aka wuce da su,Mummy ce ta Kira Aamna tare da sanar Mata Tace kiyi sauri idan sun dawo ki je wajen Ahmad kar ki Bari ya koma shaye shaye,Ahmad Yana son abokansa wannan abin zai taba shi,kece kadai Zaki iya kwantar Masa da hankali,Aamna tana

kuka Tace to Mummy.

Ahmad da kuka ya farka Yana Kiran sunayen abokansa Muryar Mashkoor yaji yace Kai dalla mace ne ka ganmu Bamu mutu ba wallahi raunuka Muka ji na Daya motar ne Suka mutu,Zumbur Ahmad ya mike Yana bin dakin Emergency da kallo yaga dukkan abokansa suna numfashi Brown dake Jan motar ya Dan fisu Shan wahala,Farin ciki ya Kama Ahmad yace ya akayi Baku mutu ba yanda motar Nan ta dagargaje Haka? Mashkoor yace ikon Allah wallahi,ai Watarana mutuwa ba a Nan take ba sai kaga motar da Bata wani ki jiki ba an mutu wacce tayi raga raga Kuma ba a mutu ba,Jibson yaji wuya duk jikinsu raunuka yace na daina shaye shaye daga yau na jiyo kamshin mutuwa,Tawaga cikin wahala yace yan kannena marayu da tuni an musu sakiyar da ba ruwa,Ba Baba ba Ni sun Shiga Uku wayyo Allah na tuba,Ahmad yace Ni yau wacce irin godiya Zan yiwa Allah,Bash yace  kaje kayi ta Sallah,Iyayen su Jibson kowa kuka ya Kare sai murna da godiya ga Allah,Ahmad ya fadawa Mummy Basu mutu ba,Itama Mummy cike da murna ta sanarwa Aamna Tace Idan an dawo dasu asibitin Kaduna taje can lallai ta kula da Ahmad.

Haka kuwa Ahmad shi ya biya kudin Hospital,har Wanda Suka mutu ya Bawa Iyayensu tallafi,Transfer aka musu zuwa Kaduna private hospital Ahmad ya dau nauyin komai Dukkansu ba Wani rauni me wahalar warkewa Suka ji ba,Sameera a guje tazo Asibitin tana ta kuka a gefen bed din Jibson ita dai tana son Jibson a rayuwa,Jibson kallonta yayi kadan yanda ta tashi hankalinta a hankali ya daura hannnunsa saman nata Hannun dake saman cikinsa,Idonta da Hawaye tace ya jikin? Murmushi yayi yace da sauki Me Hannun kwano yau cuta tasa bani da kitse,namana ba maiko zaiyi ba yanzu ki tausaya karki lashi kadan,Dariya Sameera ta dinga yi,Ahmad Yana kallonsu yayi Dariya tare da zuwa gefen Jibson ya zauna yace Malam me zaka iya ci? Kannen Jibson ne Suka shigo da Abinci iri iri,Ahmad suka gaisar tare da Sameera duk da Basu San wace ba.

Jibson yace kaima kasan bazan wuce farfesun hanta ba Malam,Maye Ahmad ya Furta suna Dariya yace Sameera ki taimaka a bashi,Sameera ta zuba a plate Ahmad ya tallafa Jibson ya jingina da jikin pillow,Kanwarsa Fa'iza Tace wannan Surukar mu ce ne?Ahmad yace ae Kawai,sai murna sukeyi suna kallon Sameera,Sameera harda kunya,Jibson yace me Hannun Kwano a bani Mana yunwa,Sameera kuwa Fa'iza ta mikawa Wai ta bashi ya ci,Fa'iza Tace ai mu fita zamuyi ma kiyi aikinki suka fice tare da komawa Room din Mashkoor.

Sameera ta fara bashi a baki Yana ci suna kallon junansu.
Mashkoor Wanda duk ya fisu Jin sauki,Ahmad ya koma Room dinsa tare da kannen Jibson gefe Kuma ga yayar Mashkoor tana zaune,wata Nurse ce Yar kyakyawa fara Amma ba can ba ta Sha fararen uniform dinta Idonta dauke da farin Glass da Alama Hutu ya ratsata kana gani kasan ba talaka bace,baza ta wuce 22yrs ba,tana kamshi ta shigo ta kalli Mashkoor Tace ranka ya Dade maganinka fa? Fuska ya Bata yace Baku da Aiki sai durawa mutum kwaya,Ahmad ya dura Masa ashar yace Amma ai kasha marar amfani Malam ka karba,ya kalli Budurwar yace idan Zaki bani a Baki da kanki Zan Sha,Dariya ya Bata tace Indai zaka Sha me zai Hana,Ahmad Baki ya tabe tare da kwadawa Mashkoor waya a Kansa kadan,Kara yayi

kadan,Nurse wacce ake Kira da Nafeesat ita ce ta bashi maganin da kanta sannan ya Sha,dama Ahmad ya Dade Yana kallon Mashkoor kullum Nurse din idan ta zo sai ya wani nutsu magana ma baya Wasa ko kadan idan a gabanta ne,Kallon Nurse din yayi a nutse yace na gode ya wani gyara t-shirt dinsa,Tace juya na wanke maka raunin Dake bayanka Zan Masa dressing, Mashkoor ya cire Rigarsa tare da juya Mata baya,Nafeesat jikinsa take karewa kallo wani luwai luwai da Alama Ana kula da jikin Nan sosai dama gasu duk Yan gayu ne,Shi kuwa Mashkoor Ido ya wani lumshe da Hannunta ya sauka a gadon bayansa,Sai da abin ya bawa Ahmad Dariya ya Harare shi sannan ya fita.

Room din Bash kuwa Ana gyara Masa inda kashinsa ya goce sai Ihu yake Yi,Yan Uwansa suna ta Masa dariya,Mamansa tana rike da shi..

Tawaga shima sosai yaji sauki Yan kannensa marayu sun yanyame shi wajen su goma Sha babu masaka tsinke sabo da shine jigon rayuwarsu Basu da matsala idan Yana Nan,Harda Yan Yara wasu duk sun Dane jikinsa suna ta wasa Yana ta dariya Umma tana musu fada Amma Ina,ai ko gida ya dawo da gudu zaka ga suna Fitowa ta kudu ta arewa suna Masa Oyoyo shi Kuma Yana daukansu Daya bayan Daya,Ummansa Tace Allah ya taimakemu da ace ka mutu da mun shiga uku,Dariya yayi yace ai Allah Yana Nan,Ahmad Daya shigo dakin sai da suka bashi tausayi matuka har da hawayensa ya goge kadan,Yaran suna ganinsa shima Suka dinga gudu Wajensa Suka yanyame shi suna Yaya Ahmad Ina wuni,Daukansu ya Shiga Yi Daya bayan Daya yanda suka Saba Yi musu,gaba Daya Suka taso har manyan maza da mata,Ahmad ya kalli Umman yace Umma yanzu kuka zo? Tayi murmushi Tace wallahi Kuwa Allah dai ya saka,ya muku Albarka,Allah ya baku lafiya da tsawon rai,Allah ya albarkaci rayuwarku, Inshaallah baza ku tabe ba,Ahmad yace Ameen Umma,Kanin Tawaga Yaja gefe Yace ya gidan namu akwai abinci ko? Yaron yace akwai komai wallahi,to ba Mai matsala? Yace babu komai,Yan makaranta fa? babu matsala Suma,Ahmad yace Good to yanzu ja Yaran Nan ku koma gida da Umma sai ku bar Sageer tunda shi Yana da girma Kuma Namiji ne,yace to,Umma ta ja Yaran Suka fita har Ahmad a Napep biyu ya biya kudin sannan ya bawa Umma 10k yace tayi cefane Suka tafi suna ta godiya.

Brown dama suna da Dan Hali su Basu da matsala Kuma Ahmad ya biya kudin Hospital,Allah sarki shima danginsa suna tafe,Bash ma Basu da matsala komai normal.
Ahmad kuwa kullum acan yake yini acan yake kwana wanka ne Kawai ke maida shi gida,Yana musu komai da kudinsa da lafiyarsa,Me Hannun kwano ma da ita ake jinya tana tafe da Abinci kullum,ko wanne room mutum Daya ne a ciki,Kuma suna ta samun lafiya kullum.

Aamna Shiryawa tayi itama zata je dubiya,Mummy ce ta fada Mata Hospital din da suke,Sabo da tana sa Rai zata ga Ahmad wani Arnen wanka ta dauka cikin dankareren farin lace me tsada na lefe Wanda Bata taba sawa ba,dinkin Riga da skert komai fari ta sa har takalmi da jaka lady in white tayi ta tafi,Da Nafeesat nurse ta fara haduwa ta tambayeta,ai Kuwa duk ta nuna mata,Dakin da Tawaga ke kwance ta fara shiga Yan Yara kanana su Uku ta hango da Dan shekara bakwai,takwas,sai me biyar suna Wasa a jikin Ahmad dukansu mata,Ahmad Kuma Yana Zaune a gefen Tawaga suna ta Hira suna dariya yace ai Kai sunanka Me Marayu Allah zai

dafa maka da wuri Tawaga yanda kake kula da Marayun Nan haka,Aamna tsayawa tayi tana kallonsu sun Matukar birgeta,kawarta ta tuna Siyama yanda taci amanarta ta rabata da masoyinta abin kaunarta,kafin ta Gama tunanin taga Yan Uwan Tawaga suna ta sintiri Yara da manya suna ta zuwa ana tafiya da su gaskiya suna ji da shi,Yan Yaran Dake Wasa wata Yar Budurwa ta kwashe su kaf ta bawa kannenta suka tafi da su gida,Ita Kuma ta dawo ciki,Budurwar baza ta wuce 19Yrs ba kyakyawar gaske suna Kama da Tawaga sai dai ta Dan fishi haske kadan dake mace ce,Shima Wala"Allah Dan Yana shaye shaye ne.

Budurwar me suna Hafsat ta kalli Aamna wacce Taki shigowa tun dazu Tace baiwar Allah kin Dade a tsaye ba dubiya kika zo ba ne? sai lokacin Ahmad ya juyo Sabo da sun juya baya,Aamna ya gani sai da zuciyarsa ta buga,yaji wani sabon sonta ya sake shigarsa,Wutar sonta tana ruruwa a zuciyarsa,Itama Haka Aamna ji take Kamar ta kurma Ihu sabo da sonsa da Kuma yanda zuciyarta ke bugawa ba kakkautawa,Tawaga ne yace Aunty Balaraba karaso Mana,Hafsat tashi tayi Tace zauna a Nan ita Kuma ta zauna kusa da Ahmad Tace Yaya Ahmad na siyo Mana Whot kullum zamuna Yi da marasa lafiya sabo da su samu nishadi,Dariya Ahmad yayi yace kin kyauta Hafsat,Aamna ji take Kamar ta mutu sabo da murmushin da yayi ba karamin kyau yayi ba,,Hafsat Tace Yaya Ahmad give me Five ta Mika Masa Hannu zasu tafa caraf Aamna ta rike Hannunta cike da kishi Tace ba muharraminki bane Yan Mata,Tawaga yayi Dariya ya kyaftawa Hafsat Ido tace na gode da tunatarwa Aunty.

Tawaga ta gaisar ta Masa ya jiki ya amsa da fara'a,Ahmad take ta faman kallo,zuciyarsa ce ta kasa Jurewa ya tashi tsam ya bar room din a fusace ya koma Room din Mashkoor Wanda daga shi sai Mashkoor,Aamna tana gamawa Tace Bari naje na duba sauran ta musu Sallama,Bayan Aamna ta fita Tawaga yace Hafsat matarsa ce fa? Dariya Hafsat tayi Tace lallai Dole ta ji haushi na,Amma fada Suka Yi? Ae Kawai Tawaga yace,Tace me ya hada su? Tawaga yace bana son gulma fa Ina ruwanki so kike naci Amanar abokina na fada Miki sirrinsa,Sorry Yaya ta furta,yace kinyi Assignment din naki? Ae ta furta yace Good so nake Yi kema ki Zama Nurse ki dinga tsira Mana tsinken bature,Dariya Hafsat tayi.

Aamna dakin Mashkoor ta shiga Bata Yi zaton Ahmad Yana ciki ba, Mashkoor yace Aunty kece? Murmushi tayi tace nice ta gaisar da shi tana ya jikin? Yace da sauki,Ahmad ya Bata Rai Kamar zaiyi duka, Aamna jikinta ya sake sanyi,Aamna da kyar take danne zuciyarta Kar tayi kuka tace Mashkoor Allah ya kiyaye gab.....Hawaye ne ya zubo Mata ba tare data shirya ba,Ahmad ganin kukanta hankalinsa ya Kai Matukar tashi Amma Daya tuna kalamanta na ba sonsa nake Yi ba na karbi soyayyarsa ne sabo da na canja shi,sabo da na taimaki Iyayensa sai ransa ya sake baci,zuciyarsa tayi bakikirin, Mashkoor Kuwa tausayin Aamna ne ya kamashi da gani tana son Abokin nasu matuka Amma tuna abinda tayiwa abokinsa Tace ba sonsa takeyi ba Kawai sai ya share,yace kiyi Hakuri Aunty komai zai dawo normal,Maganar Mashkoor yasa ta danji sanyi tana shesheka Tace da gaske kake Yi? Yace Inshaallah very soon,Murmushi Aamna tayi,ganin Haka Ahmad ya fice daga dakin a fusace.

Haka ta duba duka Brown,bash da Jibson ta fito zata tafi ta hango Ahmad a wajen Nafeesat Nurse suna magana tana rubutawa da Alama magunguna za a siyo,tafiya Aamna tayi abinta.

Bayan Kwana biyar Aamna da Yamma Shiryawa tayi ta tafi gidan Ahmad lokacin ya shirya zai tafi hospital ya ganta ta shigo tana tafiya Sadaf Sadaf,da sauri ya koma palonsa sabo da Bai so ya ci Mata mutunci a Gaban me Gadinsa Bai Dace ba tana matarsa, palon ta shiga da masifa yace me ya kawo ki gida na? bana bukatar sake ganinki a rayuwata ki fita harkata,Aamna gwiwoyinta ta zube a kasa tare da hade Hannayenta biyu tana zubar da Hawaye tana Rusa Kuka Tace Dan Allah,Dan girman Allah ka yafe min,kayi Hakuri da abinda nayi maka wallahi Allah shine sheda Ina sonka....Ina sonka Ahmad....wallahi Kaine rayuwata,Ina sonka wallahi abinda na fada ba Haka ne a Raina ba na rantse da Allah ta karasa da kuka,Cikin hasala da karaji yace da kunne na naji, idan da wani ne ya fada min bazan yarda ba zaki Raina min hankali Get out bana kaunar sake ganinki,mayaudariya makaryaciya fitar min a gida,idan kika sake shugo min gida sai Kinga abinda Zan miki,tashi ki bar min gida,Tana durkushe tana kuka Tace Ahmad ka saurare Ni Dan Allah......Tsaki Yaja a Matukar hasale ya yo kanta ba shiri ta Mike ta fice da sauri tana ta kuka,Musa Yana kallo ta bashi tausayi,yace kayi Hakuri Oga Yarinyar ce akwai naci,Ahmad ya daka Masa Tsawa yace kai matar tawa zaka ce Mata me naci wallahi Zan sallameka a aiki,Shuru Musa yayi Ahmad ya fita Yana ta Fushi Yana Jin haushin Musa yace Aamna ce me naci,ya ja tsaki. Aamna kuwa tun kafin ta koma gida zazzabi me zafi ya lullube ta.

Kwana biyu tsakani aka sallami Mashkoor da Tawaga sabo da su sun warke, Cuta ce ta Kama Aamna sabo da Bata cin abinci Kuma ga kuka kullum da take sharba,Anyi anyi taci abinci Taki ci,Zuhra ko yaushe tana Hanya tana fama da Aamna Amma Taki ci,an Bata magunguna Taki sha Tace ita gwara ta mutu ta huta da duniya,Mummy Aamna ta Kira a waya tana ta kuka Tace wallahi Mummy ina sonsa Dan Allah ki Masa magana,idan ba shi mutuwa zanyi Aamna ta sake barkewa da kuka,Mummy Tace kiyi Hakuri Aamna nasan Yana sonki zai dawo ne,Aamna tana shesheka Tace har yanzu baya ko daga wayata ko text na Masa baya Replying Ni mutuwa zanyiii.....Baba Yana Zaune tausayin Aamna ya lullube shi,yace kiyi Hakuri Aamna zai dawo Inshaallah,Mama tayi tagumi abin Nan ya isheta Allah yasa Ahmad ya dawo.

Bayan Kwana biyu jikin Aamna yayi zafi sosai lokacin Kuma Brown ne kadai ya rage a Hospital Amma duk an sallami su Jibson sun warware,Shima Brown saura kadan a sallame shi.

Mama ce ta shirya da kanta ta tafi gidan Ahmad,me Gadi ya Bude Mata ta shiga,Ahmad Yana garden a zaune yayi tagumi shi kadai,Jin Ana ta Sallama ya taso tare da lekowa,Mama ya gani yayi mamaki,Palo ya kaita yace shigo Mama,Zama tayi sannan ya gaishe ta harda kawo Mata lemo, Mama Tace Bazan Sha ba,Ahmad Ni ba ruwanka nazo Sha ba,Aamna tana can Bata da lafiya Kamar zata mutu akan ka,to wallahi idan Muka rasata sai munyi Sharia da Kai, Ahmad yaji wani dum a ransa Jin Aamna Bata da lafiya,a ransa yace yaushe su Baba suka fara kaunar Aamna ko da yake riko ba Wasa ba su Suka raineta akwai shakuwa Dole,a fili yace ku kaita asibiti Mana ko ku Bata magani da Abinci Ni Mene Nawa a ciki,da masifa Mama Tace Taki cin abinci Kuma maganin ma taki Sha babu yanda Bamu Yi ba,mikewa Mama tayi Tace Ina Jan kunnenka Yar mu ta mutu sai kaje kotu wallahi,Ahmad yace ku Bata magani zata tashi Ni ba abinda zanyi,Mama ta fice a fusace shi kuwa ya koma bedroom abinsa.

A ranar aka sallami Brown shima,komai Normal,Iyayensu har gida Suka dinga zuwa suna

yiwa Ahmad godiya.

Yau Tawaga a Machine dinsa ya dauki kannensa Wanda baza su iya Kai kansu school ba yaje ya ajiye su,ya juyo zai tafi kenan Ya hango wata Matashiyar Budurwa Yar kyakyawa fara Amma Bata fiye Hanci ba,Idonta kanana idan ka ganta ka rantse ta hada jini da Yan China Amma ita doguwa ce siririya, zata Kai 18yrs, a jikin gate din makaranta ta labe Kawai take ta aikowa da Tawaga zagi da Hannunta,tana Masa dakuwa,Shi abin ma mamaki ya bashi Bai santa ba Haka Kawai,kwafa yaja a ransa yace zanzo daukan kanne na ne Bari a tashi a school yau har karkashin gadon Uwarki sai na shiga na ballaki.

Kwance Aamna take a palon saman kujera ta lulluba da bargo tana ta Rawar sanyi,Kanta a saman cinyar Zuhra,Baba da Mama suna tsaye a kanta jikinta ya dau zafi ga magunguna Likita ya rubuta anyi anyi taci abinci ta Sha magani taki,Mama tace Aamna so kike ki kashe kanki,an Baki abinci kici kinki magani ma kinki Sha,gashi shi da bakar zuciya yaki hakura,kema ga taurin Kai Haba Aamna,Aamna tana kuka Tace Ni bazan ci ba gwara na mutu na huta tunda baya so na yanzu,Baba Ina sonsa Dan Allah Baba kaje Wajensa ka dawo min da shi idan ba Haka ba bazan ci komai ba.

Muryar Ahmad Suka tsinta a jikin kofa daga waje yace idan Ni na Baki abincin Zaki ci? Ai Zumbur Aamna ta Mike Kamar ba ita ke kwance ranga ranga ba,bargon ta jefar sanye Take da wata Yar guntuwar rigar bacci red,Gashinta yayi buzu buzu,kofa ta Bude da sauri taga Ahmad a tsaye yaci Uwar gayu cikin wani farin yard sai sheki yake zubawa,ga wani sabon kitson calabar anyi Wato har yanzu da saura ba a Gama canjawa ba,Hannunsa dauke da ledojin take away, Murmushi ya sakar Mata ai Aamna ganin Haka tasan ya huce tuni ba ruwanta da wasu su Baba da Suka fito Suma ta fada jikin Ahmad ta Rungume shi tana ta kuka tana cewa kayi Hakuri,wallahi karya nakeyi Ina sonka bazan sake ba tana shesheka,Kankameta ya sake Yi a jikinsa Yana Jin wani farin ciki,Baba da su Zuhra kunya ta kamasu yanda idonsu ya rufe,Baba Kansa ya sadda kasa yace Ashsha....Ashsha.

Ina ta godiya masu sharhi

AsmaBaffa

10/26/21, 8:53 AM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

NA KUDI NE

DUNIYATA AAMNA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

71-75

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne

BK
Sweety Bella
Umman Muhammad
Asmau Yusuf
Sa'adatu Tijjani
Teema's collection

Muje ciki Aamna ta furta tare da rike Hannunsa Suka Shiga Palo,Zama sukayi a saman kujera Aamna harda gyara Masa rigarsa,Su Baba da sa Ido duk sun ki tafiya suna ta faman kallonsu,Ahmad ya kalle ta yanda ta rame tausayi ta bashi ya Bude Ledar take away din ya fito da ita tare da dakko Shawarma me zafi sabo da yasan tana sonta,a kafadarsa ta kwantar da kanta tana kallon su Baba ba kunya,Mama Tace muje ciki Zuhra,Shawarmar ya shiga Bata a Baki tana ci,Mama tana mamaki yanda aka dinga yaki da Aamna taci abinci Taki ci Amma yanzu gashi tana ci,Shi Kuwa Baba tunaninsa yanda Aamna tayi ranga ranga Kamar zata mutu Wai yanzu itace ta watsake Haka lallai,Ahmad yace to ci Nan wurin yafi Nama ya Bata taci,yace

da Dadi? Ya tambaya,Aamna ta daga kanta Sama sannan ta sake kwantar da kanta a kafadarsa tana murmushi,Baba yace u'uhum yace ku mu tafi Mana,sannan Suka tafi aka bawa su Aamna waje,Sai da ta cinye Shawarma ta cinye wani meat pie,ta cinye chips da wani gasashen kifi sannan ya Bata Fruits ta Sha ta Dade rabon da taci abinci Haka tunda Suka Yi fada,sai dai ta Sha tea sama sama.

Sai da ta Gama yace saura wanka,ba musu ta Mike tare da cewa to tana ta wani girmamashi,Hannunsa ta rike Tace muje ciki,Kallonta yayi Yana murmushi me kayatarwa ya furta kije kiyi wanka Ina jiranki,Kuka ta saki cike da shagwaba Tace baka hakura ba kenan? Mikewa yayi yace muje,Bedroom dinta Suka Shiga ya kwanta saman bed dinta ita Kuma ta shiga wanka ta Dade kafin ta fito lokacin yayi bacci ma tuni sabo da Rashin baccin da yake samu duk dalilin Aamna,Fuskarsa ta leka tana ta wani farin ciki tana murmushi,jikinta ta goge cikin Nutsuwa ta Gama shafe shafenta ta shirya cikin wani dakakken lace Brown and dark green shima na lefe ne sabo gadagal,Yar kwalliyarta ta tsara tare da kashe dauri na zamani tana zuba kamshi ka rantse wani party zata je,Kamshinta ne ya jawo farkawarsa.

Kallo ya bita da shi ji yake kamar ya hadiyeta,Hannu ya Mika Mata tare da furta taso mu wuce tafiya zanyi,Fuska ta shagwabe tare da furta Wai saurin me kake Yi Haka? Ina da abinda zanyi ne su Mummy nan da 3days zasu zo, Alright ta furta tare da Furta muje to,mikewa yayi Suka tafi tana  gaba ta bude kofa kenan ya sa Hannu ya maida Kofar ya rufe ya jawo Hannunta da sauri ta juyo suna facing juna hannayensa yasa tare da riko Hips dinta ya mannata gaba Daya a jikinsa,Kirjinta Yana saman nasa,Hannayenta ta sakalo ta wuyansa suna kallon juna suna aikawa juna murmushin so da kauna,goshinta ya shiga yiwa kiss double a jere ya dire a saman labbanta.

Tuni Aamna ta lumshe ido tana Jin wani taratsatsin wuta a cikin jininta,Shima bangaren Ahmad abinda yake ji ya zarta ya iya control,Aamna taji Abar tasa ta Mike sosai,kunya ce ta kamata sabo da tana jinta a jikinta,lulawa tayi tunaninta lokacin data fisge Masa towel a farkon aurensu lokacin tana gidansa suna fada,a ranta Tace wacce fa na gani a baya itace yanzu tana ta tunawa,Ahmad Kuwa yama rigata tunano Sanda yake ta Shan kallonta ba Kaya zata je wanka,Aamna Martani take maida Masa suna ta tsotse bakunansu kamar Kare ya samu kashi,a ransa Yana tuna maitar Aamna a fili kuru kuru tana bukatar Namiji Yana cin zalinta baya Mata komai sabo da kar Tace jikinta yake so ba ita ba,shima yau yanda yake ji yafi karfin zuciyarsa,jikinsa har rawa yakeyi sabo da yanda Aamna ke Masa kiss wani me zafi duk ta makalkale shi.

Jikin Kofar da suke ya Kai Hannu a hankali tare da Murda key sabo da tsaro,Cike da kunya Aamna tace Allah yasa su Baba Basu ji karar key ba,Daukanta yayi cak suna karewa kansu kallo yace basa Nan ma sun fita Unguwa,Aamna tace Amma Iya Romance zamuyi ko? Abinda kike so,Tace ai Bamu koma Hospital ba an duba anga ko na warke ba,Dariya yayi shi sai yanzu ma ya tuna,Yace Ni ba ruwana da wata cutarki ai gwara ma ta kamamu tare,sai lokacin ya kwantar da ita a saman bed yabi lafiyarta ya kwanta Kara ta danyi kadan sabo da yanda ya

sakar Mata nauyinsa kadan,Aamna dai tana so ayi Romancing din Nan sai ta juya Masa baya ta fake da kunya Wai take ji,a zahiri Kuma ta juyana Dan ya zuge zip din,Don gulma har da rufe Ido,Zip din rigarta ya zuge a hankali,Harda makalewa Wai Bata so,yace why? Tace su Baba nake tsoro da kunya ka Bari sai na koma gidanka idan su Mummy sunzo.

Yace ba yau Zaki dawo ba? Tace Mummy ta min waya Tace na jirasu,Ahmad Yana son abinda Aamna ke so,Bai so ya Mata laifi sai yace kinfi so ayi komai idan kin koma? Aamna garin kunya tace ae harda wani Bata Rai ita bata so,yaji damuwa a ransa sai yaga Kamar Bata damu da shi ba,gashi Yana so shi ya rage zafi Amma Bata so idan yace zaiyi zai takurata ba a son ransa ba maida Mata rigarta Yana furta shike Nan,Aamna Kamar ta kurma Ihu ta cuci kanta,ta manta Ahmad Bai taba kula wata mace ba sai a kanta sannan shi baya Harkar Mata harkar gabansu sukeyi na shaye shaye Kawai.
Kasa magana tayi yace ko Zaki rakani? Ina zamuje? Yace Mummy ce ta aikeni gidan Yayarta Zan Kai Sako,ba damuwa muje na rakaka ta furta,tare da mikewa ta yafa mayafinta tare da daukan hand bag da takalmi me tudu Dark green.

Glass ta dakko ta saka wani light brown Nan ta sake canja dauri zuwa ture kaga tsiya,kyau Kuwa ba a magana,Fitowa sukayi ta Iske Mama a kitchen tana girki Baba Yana Zaune Yana gyara Mata wake,dama Watarana Yana Taya Mama Aiki ba sabon Abu bane Amma badan Allah yakeyi ba Wai Dan kar ayi Masa almubazzaranci sai ya zauna ya gyara da kansa,Mama ce ta juyo Tace Dan Allah Baban Zuhra ka bar wajen Nan Haka Haba me kwarin ma baza ka tsince ba sabo da tsumulmula,Baba yace naki na Bari a zubar min da dukiya a fake da kwari a dafa Mana da kwarin mu,kwarin wake ance Kara karfin gani sukeyi Ana so Dan Adam ya dinga Cinsu.
Mama Tace a Ina kaji? A radio bababban Likitan kwari shi yayi bayani,shi fannin kwari ya karanta cewar Baba.

Baba ganin Ahmad sai yace ki dafa waken Nan sosai sabo da bani da wadataccen jini a jikina,waccen shekarar 2020 har jini na bawa wata a asibiti Amma 2021 Ni kaina nasan bani da jini,idan aka aunani za a ga jini na Bai Kai na Bara ba sabo da yanzu ba'a cin nama da abubuwa masu inganci rayuwa ta canja kowa ya kwanta cuta sai kaji ance Karin jini,daga shinkafa da Mai da yaji sai tuwo da Dambu ba Dole a rasa jini ba Ana cin Dambu ai a ka'ida Dambu abincin agwagwi ne suyi ta tsatsatsaga.

Ahmad murmushi yayi ya Gane Baba,Baba Kuwa yace tunda abin Haka ne asibiti zanje na karbo gyadar Nan ta Yara wacce ake karbo musu idan sun rame sun lalace sunki girma Nima ita Zan karbo na Sha nayi bulbul,gaba Daya na wani Zuke sai Dan ciki na kwajaja a gaba da ganin kibata an San Bata lafiya bace sai Dan ciki a gaba,Dariya Aamna Suka Yi Baba yace ba abin Dariya bane Kuna gani sai tsumburewa nakeyi bani da jini sai kace Wanda nake cin kasa Haba ya kamata a dinga kula da ni..

Ahmad yace Nima Baba Ana aunani nasan bayan rashin jinin harda shawara tana damuna Ana auna Ni za a ga shawara ta Gama dani,Nima ba ci nake Ina koshi ba,sai nayi kwanta

kwanta ake bani kudin,Baba yace Kai kana Dan gidan Ajebo inji Yan Birni Dole fa ka siyo Mana Nama a gidan Nan duk wata shawararka karya kakeyi,Dariya Ahmad yayi yace to Kawai,Aamna Tace mun tafi Unguwa,Baba yace Halina da ke Aamna kin kasa wayewa wata kidahuma ce ke ace shekara kusan biyar a birni Amma har yanzu sai halin banzan ki na kunbiya kunbiya baza ki fito ki dinga fadan gaskiya ba yanzu idan gidansa zaku tafi Zan hanaki ne? Idan ma Hotel Zaki tafi me zamu ce tunda mijinki ne,Aamna ta bude Baki daga ji tasan Gulmar Baba ce Kawai so yake yaji inda zasu tafi Yana zarginsu,Mama Tace a dawo lafiya,Ahmad Yana gefe Yana jinsu saura shima ki ta Masa halinki na munafunci baza ki dinga Fitowa ki nuna kina son Abu ba,idan Kifi kike so kice ya dinga siyo miki,idan nama ne ko Madara ki fada Masa,Dariya ce ta kwacewa Ahmad su Wato Dole sai sunci kudinsa kenan shi yasa suke ta wannan abin,Baba da sigar lallami yace Yaron Nan idan mota kika ce kina so ya Siya Mana tsaf Zaki ga Allah ya azurta mu.

Tare da Yar China da Hafsat ya tafi da su,Bash suna waya da Tawaga yaji ance da Hafsat budurwarsa za a tafi ai sai shima ya tafi gidan Aamna,can ya Iske Humaira da Brown Palo,Yar China tun a mota take cewa Nima a layin zamu zauna ko? Idan munje kusa da gidan Nawa ka nuna min na fara ganinsa,Tawaga yace to,sai da taga an shigo unguwa ta kirki Yar China Tace kar dai ka fada min cewar Nan ne Unguwar da Za'a kawo Ni,Hafsat Dariya take Kamar cikin zai ciwo,Tawaga yace Nan ne Mana,Yar China tace na haye,Ni Kam na gama hayewa na baya sai labari,Hafsat tace nima Nan za'a kawo ni abokaine Bash abokinsa,Yar China ta juyo baya tana kallon Hafsat tace ban mu tafa,Suka tafa Tace ba dai wannan Dan santalin ba? Hafsat tace ae da sauri,me Suma fa tafi ta Tawagana tsayi,Hafsat tace shi fa,Hafsat Tace Dan Allah ya kika ganshi? Yar China tace fessss,to shine cewar Hafsat,Yar China tace mun Zama kawaye daga yau,ga gidana ga naki,Idan Muka haifi yara idan zanje Unguwa sai na turo su gidanki,kema Haka ko? Hafsat tace sosai ma,Tawaga ne yace gaskiya kun dameni Kuma,Shuru Suka yi har ya Shiga Estate din ya nuna musu ko Ina,Yar China tace an kure karyar kudi a Nan,ayi ta Neman kudi ba a samu ashe kudi Yana Nan, to a Nan duk tsiyar kudi an gama kure shi.
Yar China harda saita sabuwar Wayarta tana ta daukan Hoto Wai zata nunawa Iyalle.

Tunda Suka nufi part din Ahmad Suka lalace a kallo,Yar China tace ba sai an fada ba Nan na babban kwaron ne,Hafsat tace ai na masu abin ne,suna Shiga Ciki sukayi Sallama aka amsa Aamna tana zaune tare da Ahmad,Humaira da Brown ga Bash a gefe Daya, Hafsat ce ta radawa Yar China karki nuna bamu waye ba muyi yanga Kar aga Muna kalle kalle kamar Yan Kauye Yar China suna tsakiyar palon amma ita ba sirri da karfi yanda kowa zaiji tace ban gane Kar ace daga Kauye muke ba? Ni wallahi bazan wahalar da kaina ba kallo na zanyi Kawai sai a hanani Allah ya min Ido ace bazan gode Masa ba ta wajen kalle kalle ba,ka gani Yaya zata hanani kallo Wai bazan kalli gidan Nan ba Yar China ta Furta da shagwaba,Tawaga yace wane mutum ai bata Isa ba matar babban Yaya guda yi kallon ki kinji,Ahmad dukkansu kallo Suka tsaya yi suna dariya Yar China ba sirri ta tonawa Hafsat asiri,a fili Ahmad yace tsigarallahu kenan Tawaga za a Sha fama,Yar China ce ta karewa palon kallo sai lokacin ta kula da mutane a ciki Tace salamuaikum bayin Allah ,Aamna ta Aamsa suna dariya,Lokacin Yar China ta kalle su ta juya ta Kalli Tawaga tace Yaya Tawaga ai Nasara Ne tsoronsu nake ji,Turawa ne,Tawaga yace baki ji suna hausa ba hausawa ne, Yar China tace turawa sai kwai dan Allah ku yo min kwai ko guda goma ne na kaiwa Iyalleta gobe ta soya Mana muyi breakfast me Dadi,Ahmad duk danne Dariyarsa sai da ya dara.

Humaira tace Ni Kam nayi kawa sa'ata,Yar China tace kaji Yarinyar Nan jibeki fa Nawa kike zakice wani shekarunmu Daya kalle ki fa ni da na Gama Zana waec Zaki ce Ni sa'ari ce,Aamna Suka dinga dariya Wai tayi Candy ita Humaira da take University ma,Brown ne yace Yaya Tawaga ku zauna,Dariya Suka saki Wai Yaya Tawaga.
Yar China tace to ku duk abokan Yaya ne bazan durkusa na gaisar daku ba wlh nasan Kun

girmeni kuyi Hakuri Ina yininku ta Furta tare da Zama a saman kujera,Suka amsa Kuwa da fara'a,Ahmad tsokanarta yayi yace matar mu.

Yar China tace ba ruwana ban ce Ina sonka ba Kai dai da Allah ya maka kyau kaje da abinka Ni sai Aliyu Tawaga,Aamna tace Yar China kike ce mun balarabiya haskenki fa yafi nawa,yar China tace Alhmdllh saura kadan ai a Haifo Ni a zabiya Allah ya tsallakar dani, ku tace ku kunna Mana kallo mana,Ahmad ya kunna kuwa ya kamo India Yar China tace Kaini tashar hausa zalla inda aka san darajata da kimata kasar da Tawaga na yake Amma ka daukeni ka kaini India Ni ba Gunkiya  nake bauta ba Sannan ba saniya ba, Ahmad da Tawaga ne suka Mike zasu fita,aka bar Humaira da Brown suna Hira harda komawa Daya palon,Bash da Hafsat aka barsu a Nan palon,Aamna ta ja Yar China wani bedroom.

Shigarsu ke da wuya sai Daddy da Mummy sukayi Sallama,sai Kuma ga su Ahmad suna dawo Duk Suka hadu a palo,Jibson ya shigo tare da Mashkoor,Aamna tana Fitowa ita da Yar China sai ga wani Mutum baki siririn gaske sanye cikin suit bakake ya shigo da Sallama,Daddy yace kowa ya nutsu ya zauna,kowa ya zauna sai ga Baba da Mama sun shigo,Baba Yana shigowa ya rafka Salati da karfi tare da furta Rahilu Menk???????Allahu Akbar,Rahilu Kaine ka dada bushewa ka tsotse haka? Rahilu haka ka dawo Kamar Dan gudun Hijira,Rahilu kalli wandonka yanda ya maka yawa,Wannan Hannu naka Rahilu Kamar Sanda,Mama tace wuya sai kace na zalbe,Aamna Karki ga Baku Yi Kama ba shine mahaifinki maza ebo Masa abinci ya ci da Alama yunwa ta gama dashi a Sudan,ku bashi yaci ya koshi,yanzu dama zaman da kakeyi a can ba Dadi kake ji ba? Nayi zaton ma kudi kayi ka watsar da yarka ashe wahala kake Sha Baba ne yake ta magana,Aamna ta kalli Wanda akace Babanta wani mugun bushashe.

Yar China bata San Kan zancen ba tace amma wannan daga Tanzania yazo ko? Baba yace Allah Miki Albarka yar nan kema Kya fada ko Kenya ko Tanzania ko Kuma Senegal,to a Haka Wai Balarabe ne larabci yake yi,Yar China kirji ta dafe tare da toshe kunnuwanta tana cewa bazan ji ba...bazan ji larabcinsa ba,ta bawa mutane Dariya amma akayi Shuru,Baban Aamna Yana Jin hausa Amma ba sosai ba kadan kadan, Yaji abinda suke cewa Dariya shima Yar China ta bashi ya murmusa,Wai baza taji larabcinsa ba.

Masu Sharhi Ina godiya,duk inda yayi ma mutum Dadi ya fada haka ake so

AsmaBaffa
10/26/21, 2:20 PM - A Maryam: 🌵🌵DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

NA KUDI NE

DUNIYATA AAMNA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

101-105

Official

By
AsmaBaffa

Page naki ne

AUTA

Ahmad yana kusa da Aamnansa a zaune tare da rike hannunta,kasa kasa yace a Gaida Abbu mana My World ba'a Fushi da iyaye,Kallon Ahmad tayi idonta taf da Hawaye Kai ya girgiza mata Kar tayi kuka ya rada Mata a ajiye min kukan Nan sai anzo manta uwa,Murmushi tayi ba shiri,Ahmad ne ya juya harshe ya shiga suburbuda larabci Wanda ba kowa yasan yana ji ba,Baban Aamna yayiwa tare da Daddy dinsa Yana ,Abbun Aamna shima Yana yarensa cikin kwarewa,Baba yace shu'umi Rahilu akwai murya dama Indai kaji murya me dadi idan ka duba yawanci mummuna,Yar China tace kaji Larabawa Amma Banda Abbun Aamna bazan yarda Balarabe bane daga Tanzania yazo,Abbu ne ya kalli Aamna cikin Muryarsa wacce Bata fita sosai ya Furta Aamna ki yafe min,bani da bakin magana kawai ki yafe min,Yo a yafe maka ba'a San tsiyar daka shuka ba ka gudu,ko Kuwa can mun San me kakeyi? Cewar Baba.

Abbu ya kalli Baba yace Ni ban San dalilin da yasa na gudu na bar Aamna da Sumayya matata ba bani da dalili ban San me yazo kaina ba, ko me yasa hakan ta faru? Baba farat Daya yace Dan Iska ne Kawai Kai shine dalilin da yasa ka gudu algungumi Kai kamar na kwarangwal zaka ce baka San dalili ba sabo da Iskanci ya maka yawa,ai shi yasa aka ce a guji bawa bako

'ya aure,yanzu matanka Nawa da Yara? Baba ne yayi tambayar, Rahil yace Sanda na auri Sumayya matana uku itace ta hudun,bayan na samu labarin ta rasu Allah ya hadani da wata Yar libiya na aura,Baba yace Rahilu kaji tsoron Allah Wato Ashe ma munafuki kana Jin ta mutu ka Kara aure wato ka cike gurbi kenan zaka ce Allah ya hada ka da wata kaje dai ka kakai kanka Wai Kai wayo ko Dan muce kaddara ce to anki wayon,mu ka barmu a Nan kana can Kuna dancewa da Amaryarka,Dariya Baba ya bawa kowa Wai dancewa,Daddy yaji Dadi da Baba yake cin uban Rahil, Baba yace itama wacce ta aureka a Haka tayi asara mene abin so a jikinka Rahilu,Kuma har daga kasar libiya kaje ka auro ta karya kakeyi Yar wanke wanke da shara ce baza ta wuce Yar Niger ce taje Sudan aikatau ba ta rufe ka Tace Yar Libiya ce ita.

Inama tana Nan wajen na kure Yar banza yanzu nace idan ta Isa ta bani dutse dan Libiya na jefa a randar Aishatu maganin ciwon ciki,aka sheke da dariya,Baba shi baya Dariya da gaske yakeyin fadansa,Sannan yace to da ka Gama dancewar da matan naka Yara nawa Suka Tara maka? Rahil ya daga Kai Yana tunanowo,Cab Baba ya Furta suna da yawa kenan ya kasa irgasu,Rahil yace na Uwar gida Guda tara,ta biyu bakwai,Baba yace na hada Sha shida cif, Rahil yaci gaba ta uku Kuma guda shida,ta hudu Aamna kenan,sai wacce na aura bayan Sumayya ta rasu yanzu tana da uku,na hada talatin cif cewar wace Kuma me ciki yanzu take Shirin juyewa? Baba ya tambaya,Rahil yace Amarya ce,Dole wando yayi maka yawa Rahilu Nan gaba ma Sai dai idan ka koma saka jallabiya zalla Amma Riga da wando Ina tabbatar maka ka kusa rasa size din da zai maka dai dai,gashi turawa basa tazuge irin namu bare ka zamge kugunka.

Rahil ne yayiwa Daddy magana da larabci Wai ya gaji da masifar Baba zai yi tafiyarsa inda ya fito,Daddy ya tabbatar Rahil bashi da Imani yanzu wato Dole ma aka Masa yazo,Haushi yasa Daddy da hausa ya fadawa su Baba me yace ,Baba yace au haka kace ma? Yar China ce tace dan Allah Baba ku bashi abincin yaci ni Allah tausayinsa nake ji,Aamna ce tayi magana Tace na yafe maka koma mene kaje Kawai tunda dama Dole aka maka,kallon Aamna Rahil yayi rin mamanta sak,murmushi yayi tare da Furta na gode yarinya ta,Mama Tace rufe Mana baki wani yarka me ka kawo Mata tsaraba tun daga Sudan ko Dan lallensu baka kawo Mata ba domin ta dinga yiwa mijinta kwalliya ko Yar muhallabiya babu gata can tana tashi a can a banza,Baba yace sai ka dakko wani bushashen jikinka ka taho zikau zikau,Kiran Sallah aka kwala na Magrib,Daddy yace muje ayi Sallah mu dawo a karasa abinda ya kawo mu,Alwala sukayi gaba Daya su mazan suka fita masallaci Matan kuma Suka Yi a gida.

A hanyar dawowarsu Baba ya kalli Rahil Dariya taso kwace Masa yanda ya ganshi Yana tafiya kamar Yana tausayin kasa,Baba yace Rahilu kayi tafiyarka sosai kasa fa ba kyaleka zata Yi ba Matukar ka mutu aka binne ka matsar Nan sai ka shata,Sai kallon Rahil yakeyi Dariya tana kamashi,Baba yace Rahilu da gani kana ji a jikinka,a cikin yaranka ka kawo min da daya na rike maka shi,Rahil yace to Zan baka wallah,Baba ya sheke da dariya tare da dafa kafadar Abbu yace Rahilu anji wuya Dan gandal uba to bazan rike ba tunda baka da mutunci kai ai wallahi sai dai wuya ta kashe ka Ni Nace ka auri matan kana can kana Dancewa da su kana danno Yara duniya sannan kace na rike maka,Aamna ma da muka rike Allah ya karba,Daddy yace ai bazan Bari ma ka karbi wani Dansa ba wa yace ya tara Yaran,shi ga ayu to Kai ka jawa

kanka,Baba ya sake dafa kafadun Rahil yace kayi Hakuri Rahilu Ina ci maka Fuska Kaine ka jawo.

Kafin su koma gida su Aamna sun shirya kayan ciye ciye a palon sai abinda ka zaba,abincin Suka zagaye Yar China Tace Ni Zan yi Serving kowa,haka kowa ta zuba Masa abinda yake son ci,Baba yace Ni bazan zaba ba komai Ina ci a zuba min komai zanci akwai waje me fili a cikina,Yar China tace ashe Muna iri daya da Kai Baba,kema haka kike? Baba ya tambaya tace ae komai Zan cinye,kin birgeni cewar Baba,Yar China tana zuwa kan Rahil ta cika Masa plate kamar zai zubo abincin har wani tsiri yake Yi a plate tace ci ka koshi Abbu in Allah ya yarda kafin ka koma Sudan gidan jiya ka danyi bulbul,idan ka koma sai kowa yace America kaje,mu Nan ba yunwa akwai abinci Kuma Abbu ba ruwanka da Yaranka bare su cinye maka rabonka,Baba yayi Dariya Yar China da tsiya take yace da zai yarda yayi wata Guda a Nan Ina tabbatar muku kafin ya koma can sai ya saka Leda a kafarsa kafin ya cire wandonsa sabo da kiba,Rahil ya kalli abincin da aka zuba Masa yace bazan iya cinye wannan ba ai ko quarter bazan ci ba,Ni ba Jaki bane ya sa spoon ya Dan kwashi ganyayyakin Vegetables yana ci sai fruits.

Baba ya kalle shi yace Rahilu wa zaka ji kunya a nan kaci abinka karka zo kana dana sani,Wai mu zaka kife ai da ganinka an San baka Jin dadin rayuwa,Wai Kai nufinka Balarabe ne? Rahil yace sosai ma,Kana cutar kanka Kuwa mu idan sama da kasa zata hade baza mu yarda ba,asalinka Dan Kenya ne,Rahil ya Bata Rai har da buga plate da cokali cikin hausarsa wacce bata fita dai dai yace Allah kiyaye Ni...Ni... hadani da Kenya... baka ganewa Sudan can... ni Sudan Yana daga Hannu sama.

Baba Yana cin nama Yana dariyar gwarancin Rahil,Rahil harda cewa Dan an rike Masa yarinya za a dameshi,shi idan hakane a bashi yarsa ya tafi da ita,Baki su Baba suka bude yace gata Nan dauke ta ku tafi idan ka isa,a ka'ida ma Rahil Kara ya kamata mu kaika kotu Amma Muka Yi maka alfarma,Rahil ya Bata rai,Baba jinjina Kai yayi yace wannan da a Isra'ila yake harbe mu zaiyi,Yar China ce tace Kuma jirgi ya hau yazo Nan? Baba yace ae Mana,tab ai da akwalar mota ya dace a ganshi ciki,Mummy ce tace gidanku kaji yarinya a gabansa ga yarsa babban mutum,yar China da sauri Tace Yi Hakuri ai nufina yafi dacewa yazo a Private jet Yar China ta wayance,kowa Dariyarsa ya kunshe.

Sai Bayan Isha sannan duk Suka tafi gida,Yar China tace sai Nan gaba Zan dawo yau Baki sun Hana suyi hira,Aamna tace to Allah ya kaimu,Daddy da Rahil da Mummy,Humaira gaba Daya suka tafi masauki,su Jibson duk sun tafi saura Aamna da Ahmad a gidansu an barwa Aamna tarin wanke wanke da gyara Palo,na gaji Ahmad ya furta tare da mikewa saman sofa,Aamna ta kalle shi tare da cewa Ni kadai zanyi aikin My King ko dan tayani baza kayi ba,Fuska ya yatsina yace I'm sorry bazan iya ba idan kema kin gaji ki barshi da safe sai kiyi,Rabani da kwana da uban dirty haka,Aikinta tayi ta Gama ta Iske yayi bacci,Aamna girgiza shi tayi da karfi ya farka Idonsa cike da bacci,tace baza kayi min baccin wuri ba kazo cikin tsakiyar dare ka farka ka hanani bacci ba,Cikin shagwaba ya furta please Baby ki barni nayi bacci na,Aamna tace Ni Allah ka tashi kawai,ba Kya tausayina? to ai ba Aiki kake zuwa ba da

Zan tausaya maka ba,tashi muje wanka,Ido ya rufe zai koma baccinsa Aamna sai hakura tayi tasan bazai tashi ba Kansa ta dage a hankali tare da zama a kujerar ta maida Kansa saman cinyarta,da muryar bacci yasa hannayensa tare da rungumo hips dinta yana Furta so sweet yaci gaba da baccinsa,Gashinsa take Wasa da shi tana kallon Nigerian Film dinta,tunda ya fara bacci Bai tashi ba sai 9pm tana ta kallonta,taji Dadi da Bai dade ba Yana baccin,Kallonta yayi Yana murmushi yace thank you My world for your cinya,murmushi tayi tace sai wanka ko? Kai ya gyada Mata Yana cire Mata wani dan abu a gefen idonta kayan kallon Suka kashe tare da haurawa sama.

Ita kuwa Yar China tunda Tawaga ya dauketa direct shopping ya kaita ya siya Mata abinda take so sannan tace Yaya ka manta Icecream din,Komawa yayi ya dakko Mata guda Uku manya ta karba tana murna tace Thanks alot.
Tun a mota ta bude abinta tana Sha Tace Kar ya narke,a spoon ta ebo tace Yayana,Tawaga Uban tafiya,Yar China sai Tawaga haka Tawaga sai Yar China,Dariya Tawaga yayi yace haka yake Yar Chinata,to Sha ta bashi a Baki Yana driving tana bashi a baki Yana Sha itama tana Sha.

Yar China tace Yaya Wai kaji Yar Aamnan nan da iyayi Wai Ni zata koyawa wani darasi,Maganar Aamna ta gwada sabo da Aamna akwai Iyayin jaraba tunda me gyara ta koya Mata shike Nan,Yar China tace Wai a gaban saurayi nutsuwa akeyi ana Jan class,Allah na tuba Ni har a gayamin class Ni da kwana Nan na zana waec to ta Daya nake zuwa a aji,wanne ajin take so Naja idan ba na A.b.u Zaria take so na ja ba,Tawaga a ransa yace Zan Sha wahala kafin ta gane ya zanyi Ina son abata haka,a hankali zata canja,a gida ya sauke Yar china tare da rakata har Gaban Iyalle yace Iyalle ga Amanarki na dawo da ita,Iyalle tayi Dariya tace to an gode,sai da ya tafi Yar China ta fara bawa Iyalle labarin inda Suka je da Tawaga.

Kwana Uku Daddy da wasu dangin su Jibson aka Kai kudin auren Jibson,Humaira da Yar China,a Nan aka tsaida ranar aure gaba Daya Rana Daya dana su Jibson da Mashkoor,Ahmad yace baza ayi party ba tunda shima nasa ba ayi ba walima zasuyi iya abokai,Ranar da aka tsaida ranar aure Yar China Bata sani ba sai da ta dawo daga Islamiyya Iyalle tace to Yar Jikalle an kusa girma bikinki watan gobe an Kai kudin aurenki dubu dari da arba'in Yar china Tace me ya cinye goman? Dan jaraba su cika Mana ya koma dari da Hamsim,Iyalle tace uwaki Yar China Dan Iskanci to wasu ma dubu sittin ake Kai musu,sai kace ragon layya wallahi idan nice na fasa aurensa haba Iyalle dubu sittin fa? Ai gwara Kawai a bashi Ni Sadaka,Harararta Iyalle tayi Yar China tace yanzu fa Iyalle kwana Nan za a dinga ce min Amarya? Kwarai Kuwa cewar Iyalle,to gyaran Amarya fa ya za ayi ne Iyalle?

Iyalle ta rike Baki Tace oh yaran zamani mu a zamaninmu ai ko magana yarinya Bata Isa ba,idan aka Kai yarinya gidan miji sai miji ya kwana Uku Bai ga fuskar Amaryarsa ba tana lulle cikin gyalenta,Yana shigowa zata rufe kanta,Yar China ta  kyalkyale Dariya tace hmm ai wallahi da nice sai na sa reza na Dan yanka gyalen idan na lulluba sai na dinga leko idona ta Yar kafar Ina kallon Tawaga na,yanzu Kuwa Iyalle ai zamani ya canja idan kika zo gidana shayi Zan hada Miki me kauri na barki a Palo Ina can wurin Tawaga na Muna ta Jan zuga abin mu,Baki ji

sunansa ba Tawaga Uban tafiya ma'ana ya ja runduna,Yaja zugar mutane shine uban tafiya,Dariya Iyalle tayi tace to kije kuyi magana da kawayenki akan gyaran Amaryar,Wanne kawaye ai wlh ba ruwana sai dai na gayyace su biki amma ni Zan Kai kaina wajen gyara,ai nasan Mata da yawa,ga makwafciyar mu Nan Ummin Zainab can zanje ta gyarani fes,Zaki ce Wani kawaye so kike su aure min miji Dama anyi candy duk gamu Nan jiran kadan mukeyi.

A ranar Yar China tayi status a duk wani social media nata ALHMDLLH GOT ENGAGE tawaga Yana online ya gani Dariya yayi shima yayi irin status nata,Sunanta ta canja nan ma ta saka Mrs Aliyu Tawaga,frnds nata suna ta budewa Ana Mata Addua,Tawaga Kuwa Ya canja zuwa Tawagan Baby,Jibson suna gani Suka dinga Masa dariya,Ahmad yace Allah ya shiryeka yarinya ta maida ka sususu,Tawaga yace ai Kai baka da bakin magana gwara Ni ban siyar da citta ba Kuma ban saci kayan kallon surukai ba akan love,Ni banyi kuka ba,Mukus Ahmad yayi kawai yayi Dariya, Aamna tana kwance a jikinsa a saman bed Yana chat tana ta Masa shagwaba Wai sai ya koya Mata mota Nan gaba,Yana jingine da fuskar bed tana jikinsa kafafunsu rufe da bargo brown, ta maida kanta saman kirjinsa tana please King, please....sake hayewa takeyi jikinsa a hankali Tare da daura Hannunta ta Bayan wuyansa tana shafawa tare da kukan shagwaba kaji...kaji Baby...Damunsa tayi yace Alright Nan gaba Zan koya Miki shine Nan? Murna ta dingayi tare da kankame shi tana dariya.

Bayan sati Daya Rahil ya Gama shirinsa tsaf zai tafi da yamma,jirgin 5pm gidan Aamna yazo Suka gaisa har Ahmad sannan King ya Basu waje,Aamna da Rahil Abbunta Suka Yi har Hira sosai sannan ya musu Sallama da Niyyar tafiya,Aamna Tace zata Zo Nan gaba,Daddy kyautar ban girma yayiwa Rahil suka je gidan Baba Rahil ya sake Yiwa Baba godiya na rike Masa yarinya da yayi,Baba yace ba komai ai da na kowa ne duk da dai baka kawo Mana tsaraba ko Jallabiyya ba ai ba komai .

Amma Rahilu Kamar a kanka a saukar da Babu yanzu ko Yar tuffa ai ka taho Mana da ita ta jirgi Amma sai ka taho zikau daga bushashen jikinka sai wannan Yan iskan kayan Wai sut (suit)Kai a Dole ka cinye zaka Mana burga to ai jikinka ya bada Kai,Daddy yace Baba a barshi Haka ya tuba,rakasu Baba yayi yace Allah ya tsare Rahilu in Allah ya yarda tare da Aamna zamu zo Sudan zanga yaranka,Rahilu yaji masifar Baba da mita da lalatacciyar hausarsa yace bana so zuwanka....kar ta zo Kai da ita....Ni...Kai...Bama tare .. Bama...shiri...karka zo Sudan....Baba yace dan ma ance Za'a zo sai kace garin arziki,Sudan din fin Nigeria tayi? duk gaku Nan ragowar yunwa ku kanku Yan kasar Baku koshi ba,Rahilu ka dube ka fa har mu zaka ce Kar muzo muku gari,Sudan din Wanda duk irinku ne a cikinta me zamu kalla? Kuma wallahi Inshaallah sai nazo naga matsuguninka sai na sa maka Ido Naga yawan yayanka,sai Naga waye a ciki Allah ya Dora musu Suka yo Kama da kai,Rahil da gaske ya dinga cewa Ni bance kazo gidana ba bana so....Baba yace Allah baka Isa ba sai na zo,Daddy Yana ta dariya Yana kallon rikicin Baba da Rahil,Rahil motar Baba ya shige Yana Jan Tsaki Driver ya ja mota Suka wuce airport,Baba Kuwa gida ya koma Yana dariya yace airport zasu Sha kallo.

Bayan kwanani biki Yana ta matsowa ko wanne bangare shirye shirye sukeyi yayin da su Aamna suke Shan love abinsu yau saturday tunda Ahmad ya fita da safe sun fita da su Jibson

Basu dawo ba har Bayan Isha Aamna duk ta shiga damuwa,gidan ya Mata Fadi,ta rigida ta Saba da mijinta kullum suna tare,ta Kira wayarsa Bata shiga,ga wankanta ta sha tana ta zuba kamshi a Palo ta zauna tana ta jiransa hankalinta duk ya tashi ko ba kalau ba,Number Tawaga ta Kira lokacin suna tare da Ahmad suna cike wasu takardu masu yawa duk akan aikin da zasu fara Nan gaba a companies na Daddy Wanda Lokacin suna tare da Daddy a Hotel din da yake shi da Mummy da Humaira,Wayar Tawaga ya daga yace Aunty Balaraba ce fa King,maybe Kai take Nema ka manta tunda kasa wayarka a charge ka kashe baka kunna ba.

Ahmad Wanda hankalinsa gaba Daya Yana Kan Aamna yasan dama tana can tana jiransa ga Daddy a wajen ya hanasu sakewa da Aiki,Tawaga Sallama yayi Suka gaisa sannan tace Dan Allah Kuna tare ne? Yace ae Muna tare aikine ya Sha kanmu amma yanzu zamu taho gida,Ahmad ne yace bani Wayar,Yana karba Aamna da shagwaba tace Ina ta kiranka ka jawo na shiga damuwa ko ba lafiya ba,Idan na dawo Zan Miki bayani My world,Daddy ne ya samu Aiki Amma yanzu Zan taho,fatan kinci abinci? Ae tace yace good, me Zan siyo Miki? Tsire Aamna ta Furta alright.

Suna gama Wayar Basu Dade ba 8:30 Ahmad ya dawo gida,tana jiransa Jin motarsa da Alama shine,Yana shigowa palon tayi tsalle tare da rungumeshi tana murna sosai shima ji yake kamar yayi kwana Uku Bai ganta ba,Kallo ya Kare Mata tare da furta kinyi kyau My World,Ledar hannunsa ta karba tare da rike hannunsa daya tace let's go Suka haura sama tana cewa na Sha wahala Ina zaman jiranka,Eyya I'm Sorry Beb,never mind ta furta,kayan jikinsa wani shegen yadi ta taimaka Masa ya cire Yana Shiga wanka taje ta Hado Masa abinci ta kawo sama,kafin ya fito ta fito Masa da kayan baccinsa masi kyau,itama bedroom dinta taje ta canja Kaya kasancewar Bata Dade da yin wanka ba.

Bata dawo ba sai da ya Gama shirinsa sannan ya zauna inda ta Ajiye Masa abincin yunwa yake ji sosai sai Samunsa tayi Yana ta cin sakwara da miyar Egusi,ita Kuwa tsirenta ta bude taci yanda take so tace baka ci Kai? Yace ae Ni tsire Bai Dame Ni ba,sai da ya Gama sannan ta maida komai kitchen ta dawo Yana ta deshe jikinsa da turaruka da Alama brush yayi,na gaji ya furta kawai tare da kwanciya a saman bed,itama saman bed ta haura taho ya furta tare da Rungume ta Itama Haka da wuri bacci yayi gaba da su.

Sai wurin 4pm ya farka Yana farkawa ya Mike ya Shiga toilet,Bayan ya fito taji ya fara zare Mata Kaya a hankali.

Ayi Hakuri da wannan

AsmaBaffa
10/26/21, 2:20 PM - A Maryam: 🌵🌵 DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

NA KUDI NE

DUNIYATA AAMNA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY

106-110

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne

UMMI DEEJAT
MAMAN SAMHA
MAMAN MUNIBA
MUNEERA
HAFSATOU

Aamna farkawa tayi kadan,My world ki tashi,Cikin shagwaba ta juya tana cewa bacci King Dan Allah muyi bacci,Ni bazan iya bacci yanzu ban samu nutsuwa ba Ina wani bacci Ina tuna Mummy ta yanzu fa ki tashi ki bani Manta Uwa,Amma yanzu kin jawo Ina ta tuna Mummyta,Dariya ya bawa Aamna tana Jin bacci Haka ta Mike tana murmushi,jikinta yake karewa kallo rigar baccin tayi mugun Mata kyau gata sharara,to ka Jira nayi fitsari first,Alright ya furta ta Mike ta shige toilet,tsarki tayi da ruwa me zafi har da wanke Hq dinta da Genital wash me kamshi wanda ke maganin Infection Yana karawa mace Niima da dandano,Sai da tayi matsi da musk me Kama da Madara me dadin kamshin, sai da ta Gama kyalekyalenta ta fito ko Ina Yana kamshi Wai fitsari tayi,tun kafin ta karaso ya Mike tare da rungumeta babu Bata lokaci ya cire Mata Yar rigar,abinda yafi daukar hankalinsa ya shiga murzawa suna kissing juna a hankali Aamna ta fara ji a jikinta tana bankarewa,Saman bed ya jata Suka fada, tausayi ta bashi tunawa da yayi tana baccinta ya tashe ta,Kallonta yayi tare da Furta ban takuraki ba My world?

Murmushi tayi Kawai tunaninsa Kara take Masa Kawai Bata so ta nuna ya takurata ne,Wani kallon kauna ya Mata tare da dakko rigar baccinta da Niyyar maida Mata ita jikinta,Hannunsa ta rike a hankali tana Masa wani kallo Wanda ke nuna tana bukatarsa itama,ya rigada ya gane abarsa,a hankali da rada tace I need you My King,baka ji ba nace you know how to do it,ka Iya ka huta,Dariya ya saki,Ido Daya ta kashe Masa tace oya let's do it,Yatsunta ya rike Yana murzasu ya furta I love you My Wife,I'm gonna fuck you well Darling cewar Aamna yau itace zatayi yakin,Ahmad yana murna yace yau zamu Danse kenan,Dariya tayi tace Baba ya iya abin Dariya Wai Dansewa amma fa King seriously naji haushin Yar China yau,wlh badan Tawaga ba yau sai na ci uban Yarinyar nan Dan Kawai bata Sanni bane,yanzu ta Sanni Kawai nayi laushi ba Aamnan ce ta baya ba,Fuska Ahmad ya bata Nan take kallon Aamna yayi yace bana son wannan shirmen, Baki gani yarinya ce ba,Budurwar Abokin nawa ke kina Babba mene haka,? so kike a kawo su ku fara fada ku bata Mana abota,dama ko a dangi wallahi wani hargitsin da fadan Mata ke haddasa shi da gutsiri tsoma da gulma,abinda Bai Kai ya kawo ba ku Dora shi a ranku, goyon kakar Zaki biyewa kina ga yanda Tawaga ya dauke ki har fada Miki yayi zata dinga zuwa kina Dan ganar da ita wani Abu,tsakanin Hakuri da rashinsa kadan ne fa,to Zan fada Miki Estate din Nan kowa gidansa daban Kawai Estate ne Daya gida kin gani kowa da nasa daban,idan wata Bata je gidan wata ba babu wacce zata ga wata,wlh karki sake naji ance kin samu sabani da wata,Mijin kowa daban,Yar China duk cikinku itace karama,Muna zaune Ify zaku fara haddasa fada,shi Baba Baki ji haushinsa ba sai ita, Ahmad a ransa yasan Yar China bata kyauta ba amma yasan halin Mata gwara yayiwa tufkar hanci shi yasa ya dinga yiwa Aamna masifa tasan halinsa bai iya Fushi ba.

Amma ita baka ga abinda ta min ba? Shut up ya Furta da fada yace ance Miki Tawaga baida hankali shi Bai gani ba a gabansa akayi kina nufin bazai Mata fada ba? Tawaga ya fimu saurin fushi zai iya marinta ma akan wannan wlh karki sake na Kara Jin zancen nan,Aamna Idonta ya kawo ruwa yanda ya lullube ta da Fada kamar Bai Santa ba,Aamna tace ai dama nasan abokanka sun fini matsayi a wajenka,Sanda Suka Yi hatsari da nice nasan baza ka haukace Haka ba Ana gama zaman makoki zaka fara Neman auren wata sabuwar budurwar,Ahmad a

ransa Dariya yayi a fili Kuwa Tsaki Yaja tare da maida kayansa yace kin Bata min Mood sai ki Danse ke kadai,Aamna da zuciya tazo Mata wuya Tace ai Zan Iya Ni kadai,da me? Ya tambaya ta bashi amsa da hannuna,Yau Kuwa wallahi da an Bude Miki kofofin Jahanma da yawa.

Aamna ta saki kuka tare da cewa Yar Iska Yar China 'Yar Yarinya Kawai ,da gani kanwarta ce ta Raine ta,ba Kaka bace haukarta ta wuce ta goyon kaka goyon kanwarta ce,kanwarta ce ta yayeta Kuma bazan koya Mata komai ba,Dariya ta ba Ahmad Wai kanwarta ce ta raineta Wato karewar yarinta, Kwanciya yayi tare da juya Mata baya,Zama tayi abinta tare da kin kwanciya sai da Ahmad ya gaji ya jawota ta kwanta a jikinsa tare da makalkaleta a jikinsa Yana cewa bana son taurin Kan Nan naki My world,taurin Kaine da ke shi yasa Baba yake miki fada kullum kina Jin haushi,Aamna tace ai dai ba taurin Kai na maka ba gaskiya ka take min ga gaskiya Kiri Kiri amma zaka dinga min fada ko Hakuri baza ka bani ba sai fada ai dai mu Mata kashinmu a tankware yake Bama mikewa idan aka takura Mana Kara lankwashewa zamu yi ,to naji ya Isa daina zubar da Hawayen Haka ban sanki da kuka ba,Aamna tace wallahi bazan daina kukan Nan ba sai na zubar da gurbataccen Hawayena,Dariya yayi tare da rungumeta sosai yace to ya isa,Aamna ana kuka harda tari kuful-kuful kuka yayi kuka wai,sai da ta gama kukan shagwabarta sannan bacci yayi gaba dasu,washe gari Kuwa da Asuba suna idar da Sallah ranar baije masallaci ba a gida Suka Yi tare,Ko Adduar kirki Bai Bari sunyi ba ya shige cikin Hijab dinta Aamna tana ta Azhkar shi Kuma Yana Wasa da Boobs dinta Yana cewa kici gaba da adduarki Lada Kan Lada wannan ma Azkhar ne Babba, Dole ta hakura tare da Furta wannan ai tsokana ne King,Nan suka fara murza junansu suna wani nishi,Ahmad ya shiga buga harka cikin nutsuwa,a kasa sukeyi yau ko bed Bai Bari sun hau ba,Aamna tana Enjoying sosai cewa take Yeah....Baby Fuck me.....fuck...fuck....Ahmad Kuwa cewa yake do you like it? Aamna tana yeah fuck....

Washe gari da Yamma Tawaga gidan su Yar China yaje ya sameta,ta gyara gidansu fes Yana ta kamshi,tana zaune a kitchen tana girki a Murhun gawayi,sanye take cikin skert din atamfa da vest sai wata hula Kalar vest din da ta saka pink, Kamshi taji ta juyo da sauri sai taga Tawaganta,kunya ce ta kamata jikinta ba ko mayafi,Tawaga yaga jiki me kyau fari tas a ransa yace na gode Allah,kujera ya jawo tare da Zama Yana cewa Baki fa amsa min Sallamarta ba kina ta faman kallona,Firgit Yar China ta dawo daga hayyacinta yanda take Kallon Tawaga ya Mata kyau matuka,Yaya kayi kyau,ai kin fini kyau gimbiyata,Murmushi tayi Tace Bari na dakko maka Tabarma ko carpet,no..no ba Zama zanyi ba shigowa nayi na ganki ko naji sanyi a Raina tunaninki ya hanani sakewa Baby,Yar China ta rufe Ido tare da furta Kai Yaya Ni kunya nake ji Allah,Ina Iyelle ne? Ta tafi Unguwa gidan Kawu kaninta sai dare zata dawo,Zama ya gyara Yar China tana girkinta suna Hira,me kike dafa Mana? Yar China tace kasan Iyalle da son tuwo,Tuwon shinkafa nayi na gama miyar nake karasawa ta nuna Masa Danyar kubewar da ta goga,yace Ashe yau zanci abincin naji matar ta iya girki ko Bata iya ba,Dariya Yar China tayi tace na Iya girki fa Yaya,Haka nake so ai,Kin San me ya kawo Ni wajenki? Yar China tace a'a,yace Akan Aamna ne,kamar Ahmad ya sani yace yasan Tawaga sai yayiwa Yar China fada sai Kuwa gashi.

Tawaga yace kin bani haushi fa abinda kika Yi duk fadan da Iyalle ta Miki Baki ji ba,Baby Baki

iya magana ba taya kina yarinya a Gaban manya suna magana kina magana har Zaki dinga ciwa Baban Aamna fuska a Gaban yarsa,duk wajen ga mutane kina tunanin zasu ganki a me hankali,sannan Ni zasu ce banyi dacen Mata ba tunda na auro marar kunya,ko ba komai Mahaifi ne fa,kin San Kuwa me ake cewa Mahaifi? Kuma gashi Babban mutum dattijo,a Gaban manyan mutane Ina ta kyafta Miki Ido kiyi Shuru Amma ke Baki San ma Harara ba,sonki da nakeyi Allah ne ya sa min sonki Amma wlh da bazan so ki ba,ko Ni farko fa a makarantarku Haka kika zageni wannan zagin da kika min shine silar Haduwar mu,Kuma na gani naji Ina sonki a Haka,Amma shine matar abokina ta girmeki Zaki je har gidanta a gabanta kici fuskarta Kuma ke ba ruwanki ko a jikinki,haka Zaki yiwa dangina? Yar China ta kebe Baki zata Yi kuka Tawaga yace wlh kika min kuka sai na mareki a Nan wajen kin San Halina ya dan Iskanci Ana gyara Miki Abu ke kuka ma zakiyi,me na Miki? Yar China tace ai dai Sanda na zage ka dama sonka nakeyi,kullum Ina kallo kana kawo kannenka makarantar mu, Ni Kuwa in buya a bakin gate inyi ta kallonka Ina Jin dadi.

Ka tambayi Iyalle wallahi kullum na dawo daga makaranta sai na Bata labarinka,Ni Kuma Dana gaji zuciyata tana ta bugawa idan na ganka shine naji haushi na zageka ashe Allah yaga zuciyata shine ta Haka ya Zama silar komai,Kuma Ni Aamna ai ban San zata ji haushi ba Amma ka kirata a waya na Bata Hakuri,Indai zaka daina Jin haushi na Zan Bata Hakuri.

Tawaga saukin Kan Yar China yana birge shi Bata da taurin Kai Sam,tana Jin Tsoronsa ko ya idan ya nuna Mata fushinsa sai ta sakko,Wai dama ta Dade tana sonsa Bai Sani ba Amma Taki nuna Masa ko Alama sai da ya gaji ya fada da Kansa Lallai Yar China Ashe da hankalinta sai yaji ta dada samun guri a zuciyarsa.

Kallonta yayi yace Bari na Kira Aamna ki bata Hakuri,to Kawai tace,Ahmad ya Kira a waya bugu Daya ya daga lokacin suna garden suna hutawa shi Aamna,Ya akayi Tawaga? Tawaga yace King Ina Aamna? gata kusa dani,Okay please Bata Wayar zamuyi magana,Ahmad bai tambaya ba ya mikawa Aamna waya,Bayan sun gaisa yace Aunty Balaraba Hakuri zamu Baki akan abinda Yar China ta miki kiyi Hakuri dan Allah kuruciya ce gata zata baki hakuri,Yar China waya ta karba tace dan Allah Auntynmu kiyi hakuri nasan nayi kuskure bazan sake ba,Aamna sai kuma taji kunyar masifar da tayi jiya har suna fada da Ahmad akai,gashi baiyi karya ba Tawaga Yana sane zai dau mataki,Aamna tace ba komai kanwata karki damu ya wuce,Yar China Tace na gode Iyallace ta lalatani bata iya tarbiyantar Dani ba,komai nace sai ta kyaleni,ko me nayi sai tace nayi dai dai Bata min fada,Bata Nuna min hanya duk laifin Iyalle ne bata iya tarbiya ba,Iyallace da laifi Dariya Aamna tayi tace to ya wuce sis,Iyallace ta karasa shigowa gidan tana cewa da nayi Miki Ubanki?

Dan Ubanki to naji abinda kika ce Wato Ni na lalata ki ban iya tarbiyya ba,duk abinda kikeyi bana Miki fada ko? Tun yaushe kullum sai nace ki bari ki Bari kaza ba kyau Amma bakya Jin magana,na nuna Miki fari da Baki amma ba Kya ganewa kullum sai kinyi laifi an kureki kice nice na lalataki,Haka rannan a makaranta kinyi laifi aka tara Yan makaranta za a zaneki kika ce nice na lalataki a Gaban Yan makaranta da malamai ai naji labari wajen kawarki Habiba,Rannan Haka kika je har gidan sabuwar Amarya kika ce kayan dakinta da katakon dalbejiya aka Yi shi,Kuma kika ce mijinta Maye ne,Babarsa Mayyace Kuma kika ce a wajena kika ji,Tawaga ya

dinga dariya,Iyalle tace harda cewa wai ai Ni na tsufa na Dade a duniya Duk mutanen garin Nan a idona aka haife su sabo da haka nasan waye Maye nasan waye Wanda ba mayu ba,Yar China tana ta rokon Iyalle tayi Shuru amma Iyalle tace sai na fada Yar banzar yarinya.

Saura kadan ki kashe aure da kyar na samu case din ya mutu,yanzu kin tabka rashin kunyarki kince nice,tunda tonon asirin kike so ai Nima nasan sirrinki Bari na fada Masa,Iyalle tana kallon Tawaga tace bawan Allah kaje kayi zamanka ta dade tana sonka fa Kaine baka sani ba,tun tana Jss3 yau shekaru Uku kenan Kai baka sani ba,kullum ta dawo daga makaranta sai ta bani labarinka,lokacin ma Bata fara nono ba,Iyalle Tace ai kwanaki ma...Yar China ce ta fara ihu yeeeeeeyeyehhhhhh ta cika gidan Wai Dan kar Tawaga yaji Maganar Iyalle shine take ta Ihu.

Tawaga ne ya ja Hannunta suka koma Palo shi yau fess ashe Yar China ta Dade tana kaunarsa,sai yaji wani sanyi da nutsuwa a ransa yasan ba Wanda zai iya kwace Masa ita,fada ya dinga Mata da Nasiha tace Zan daina Yaya,Tawaga yace indai baki daina ba zamu bata,Kinga Amarya guda ango ya daina kulata sai ya? Yar China tace babu lafiya Amarya da ango suna fada ai sai lahaula,Yaya baza muyi party ba? Tawaga yace ae sai dai mu Danse idan an kawo min ke,Yar China ta tuno Baba ta dinga dariya,yace kuyi Dj a Kofar gidanku da kawayenki,Iyalle tace fa ranar da aka Daura aure ranar za a Kai amarya idon Yar China ya ciko da hawaye tana tausayawa kanta zata rabu da Iyallenta.

Tawaga yace kukan Kuma fa ya Furta Yana goge Mata hawayen da Handkerchief dinsa,tana shesheka tace Iyalleta....shike Nan Zan tafi na barta Ina tsoro Kar Yan iskan Unguwa su hauro suyiwa Iyalleta Fyade,Tawaga ya kwashe da dariya yace Iyallen da ta Shekara kusan Tamanin da wani Abu ita za'a hauro ayiwa fyade?.
Aamna tace to ake yiwa mahaukata Mata fyade Wanda suke ciwon hauka suna bin bola bare me hankali Kuma Iyalle ma ai da sauranta,jikinta Bai Gama saki ba,shi dai Tawaga dariya kawai yakeyi ita Bama kukan rabuwa takeyi ba,Tawaga yace ai gidan Kawu kaninta zata koma Kuma zamu ci gaba da kula da ita,tace to shike nan,na fadawa kawayena bikin saura lv idan ka buga shi a kawo min da wuri sabo da Ni gyaran Amarya za'a fara Yi min bana son fita Rana na lalace,Tawaga yace karki damu,duk kyan jikin Nan naki sai an Kara gyara shi? tace so nake fa na dinga kashe maka Ido da haske na Walwal.

Kudi ya Bata masu yawa yace gashi idan Basu Isa ba ki kirani a waya,Yar China taga kudi Tace Kai Yaya sunyi yawa ai gwara ka siya Mana abinci a gidan tunda kaga dai Ni ba wata garar arziki za a min ba tunda bani da gata,Murmushi yayi yace ai wannan an wuce Wajensa,Yar China tace Allah Yaya munfi marfin cikin mu? Sosai ma ya Bata amsa tace to Allah ya Kara budi,Tun a gabansa Yar China ta fara kasafin kudin, tana dubu biyar kudin maganin Infection duk na San bani da shi amma sabo da tsaro ko ya makale a lungun cikina ban sani ba,Iyalle tace za a siyo Dan mannau dubu hudu,duba daya da dari biyar kudin bagaruwa...Tawaga Jin irin bala'in da za a hada masa duk a Kansa yace Haba Baby duk Ni kadai so kike na kasa tashi,Yar China Bata Gane ba tace Haba Yaya sai kace wacce zan daureka da Igiya? Tawaga yayi kicin kicin yace bada Ni ba gaskiya Ni Kawai ki gigitani da kyawunki,kyan halinki,kwalliya,tsafta da Iya girki,iya soyayya shine Zaki birgeni,Yar China

murmushi tayi Kawai Tace ai girkin Ina sake koyen Kalar na zamani na gargajiya na iya,Tawaga yace yawwa ki dage a Nan,Iyalle tace cab Kaine fa zaka fi kowa cin moriyar,Yace no Ni dai karki fi karfi na,Yar China ta kyalkyale da dariya ta manta da wani Sex ma.

Tunda Tawaga ya bar wajen Yar China yake tunano irin yanda yaji Ana tsuma Amaryarsa,wajensu su Jibson ya wuce yace Wai ku bakwa gyaran Angon ne kamar yanda amare keyi? Jibson yace akan me Kuma? Amare suna ta tsumi mu mun zauna haka karfa Sufi karfinmu, Mashkoor yace Nima Haka nace muma mu nemi namu,Brown yace zamu danyi kadan gaf da biki Haka suka Gama tsarinsu Suma zasu tsumu.

Lokaci na tafiya ana zaune cikin farin ciki ana ta Shirin biki,biki ya rage Saura sati Daya su Yar China an zuba kyau da kanta take zuwa gyaran jiki,Kawayenta duk ta gayyace su,Haka su Sameera ma,Sameera ta kashewa jikinta kudi sosai sabo da tasan ta taba aure ai Kuwa kyan da ta zuba kowa ya kalle ta yasan ba karya duk Wanda ya ganta sai ta birge shi,Haka Nafeesat ma da Hafsat bare Yar masu da shi Humaira an kashe Naira.
Ba Wani shagali za ayi ba Ana daura aure da Yamma za a Kai Amare,,Iyalle duk kayanta an kwashe an maida gidan kaninta dakin daya bata,ana kai Yar China gidan miji zata koma.

Jibson suna tare da Mashkoor yace Yar bazawara ta akwai hankali Haka nake son mace ta Gama hada hankalinta,bani da hawan jini yanda take ji dani,Dariya Mashkoor yayi yace to dama Bazawara ai dole ka huta,Jibson Yana murmushi yace Ina fada maka Danfa ta hadu da gogagge ne,zata nuna min duniya na nuna Mata ai nima babban Kai ne,badan ni bane yanda suke sakin layi kasan Bazawara sun San komai ba ruwansu idan baka goge ba sai su kalle ka wani can,ai Kuwa Zan Sha dadi ba Wani kuka da jiran sai ta Saba,Tawaga dai zaici ubansa da wannan yarinyar, Mashkoor Yana dariya yace Yarinyar Tawaga girma ne Kawai da ita amma ni tana birge ni ko ba komai zaka Yi dariya, zai Sha fama amma ai jikinta Kuma ba karama bace gata doguwa Kuma akwai diri komai ya ciko cewar Jibson,Mashkoor yace ai Yarinyar akwai abin Moro a jikinta,Tawaga zai more akwai kayan aiki,Dariya Suka yi,Jibson yace ni da kuke cewa yarinya ce nayi zaton kwaila ce ashe ta nuna luguf,Dariya sukayi, Mashkoor Yana cewa Kaine aka cuta Jibson,Jibson yace karya kake Yi wallahi sameerata tafi Nafeesat dinka komai kana kallonta cif cif,ai duk ta fi Su Hafsat cika,to ba ta fisu girma ba maybe ma Boobs din nata sunyi doguwar sujjada wacce kafin su dago sai dai Hakuri,Jibson yace karya kake Yi wallahi Ni fa nasan abina tunda na taba tabawa, Mashkoor yace dan Iska Allah ya Kamaka dama wlh tunda Naga idan munje zance kana korata wai na Baku waje minti biyar zaka fito nasan baka kulla gaskiya ba,Baki Jibson ya tabe yace sharri zaka min ai dai Allah ya sani watarana ne tayi kwalliya me kyau na kasa Jurewa shima kissing Mukayi sannan hannuna ya Dan samu tabaraki yasa Mata Albarka amma daga shi ban sake ko wani kiss ba,ai na tuba ni bazan iya aikata wani Abu da Yar wani ba nayi hankali,Dariya suka Yi Mashkoor yace yayi daidai mutumina.

Yar China ankon su iri Daya dana Hafsat Kanwar Tawaga wacce Bash zai aura,Humaira Kuwa Bata ma Yi ankon ba sabo da babu wani time,Haka Nafeesat Yar Malam babu anko dama,su Ahmad ba Zama ita kanta Aamna sai hakuri tayi da mijinta Bai fiye Zama ba ana ta shirye shiryen biki,Yar China tayi gyaran jikinta tayi kyau Dangin mamanta Dana Babanta dake

an dauke musu komai na kayan daki Daddy yayi komai sai Suka tsaya a sauran abubuwan biki da abinda ya shafi Amarya,Yar China Tasha gyara na musamman,Haka sauran matan ma musamman Humaira da Sameera ba a magana,Humaira su suna da masu gidan Rana,Sameera kuma ta taba aure shi yasa tayi kamar me,bangaren Hafsat ma ta gama ba karya haka Nafeesat da take Nurse gata Yar me kudi in kazo Nan an wuce wajen.

Angwaye sunyi dinkuna na musamman Suma Kamar masu hadawa kansu lefe,gidan kowanne ya dau kamshi Daddy ya zuba komai har abinci store Guda,Lefen Amare Kuwa Tawaga Akwati takwas aka yiwa Yar China Haka su Mashkoor ma takwas takwas ko wanne Kalar design din akwatuna daban Haka kayan ciki ma ko wacce da nata Kalar daban,Mummy da Amarya tare da Dangi sabon gidansu na Kaduna suka dawo Wanda Daddy ne ya Gina shi daban idan sunzo Nan zasu dinga sauka a tunda ya Bawa Tawaga gidansa da Ahmad ya Bari sunzo sabo da saukakawa Dangin Ango ba sai anje har Lagos ba.

An Gama komai ana gobe daurin aure Yar China ta tura Yara makwaftan da suke mutunci su sanar musu,sai dai suji yaro ya shigo yace Wai Yar China tace ranar asabar ne daurin aurenta Kar kuyi girki ranar ku zo kuci abinci da ku da yaranku,ai ta dariya ace kace Allah ya kaimu,Bayan Kuma ta raba musu Iv sai da ta Kara sanarwa da baki.

Amare sun Sha lalle da gyaran gashi ko wacce mashaallah,Gaba Daya a babban masallacin Malam baban Nafeesat a Nan aka taru da dunbin tawagar angwaye da Amarya aka Daura Auren ko wacce,Jibril Jibson aka fara daurawa aure da Sameera Ana Gama nasa yace Alhmdllh na Haye ni Saura na Baya,yasha Uwar Shadda me shegen tsada fara tas harda babban Riga da hula me kyau,ga takalmi da agogo masu tsada,idan ka kalli Jibson sai ka sake Kallonsa ba karya da gani kasan wanka ya samu gindin Zama a jikinsa.

Bash da Hafsat sune na biyu Wanda aka Daura aurensu,Bash yace Nima nabi layinka Jibson na tsallake Alhmdllh,Bash kuwa Shaddarsa Arsh color ce,yanda ya tsira hular nan ga saje da Dan gemu ya zauna das kwance a fatarsa me haske haske abin kallo ne Bash,Na gaba Kuwa Mubaraq Brown aka daurawa nasa da Kanwar Ahmad Humaira,Daddy Yana ta farin ciki shi Kuma Brown kayansa wasu light brown ne,Yana da tsayi sosai da Dan jikinsa cif chocolate skin dinsa wata sumul sumul gashi dama shi akwai Isa da tamaka haka yake ya gama tsula kyau.

Mashkoor da Nafeesat aka daurawa aure Wanda yake sanye cikin wata Shadda ta Alfarma Grey color ba karya sai Wanda ya gani,Na karshe Aliyu Haidar Tawaga ne aka Daura da Sadiya Yar China, shi Kuwa Tawaga Sea blue ya saka tana sheki,ya kafa hula hancin Nan nasa dogo ya fito sosai,gashi jikin Tawaga na daukan wanka ne,ko me yasa kyau yake masa Allah ya bashi ba wata mace da bazai birge ba,Dukkansu ba Wanda zaka ce ya taba gwada ko shaye shaye,dama Sai Hali yazo Daya ake abota,Dukkansu akan Sadaki dubu Dari dari Wanda Malam Iiman Baban Nafeesat dukka shi ya biyawa kowa Sadaki a aljihunsa.

Masu kade kade suna Yi Ana ta kashe pics,taro yayi taro Uban gayyar King Ahmad duk Yana cikin wakilan ango Wanda Suka karbi aure dan shishigi Wai har da shi a ciki,Wani yard ya saka me Arnen tsada kana kallo kasan an gama kure karshen Naira a jikin Ahmad komai Silver

color ne,shima yau ya sa Yar hula duk sun tsirata irin na matasa,Ahmad uban gayya reception suka wuce da tawagar abokai da sauran manya duk aka tafi katon hotel a Nan aka Kama hole kowa yaci abinda yake so ga kida na tashi,Aamna Kuwa itama tana sabon gidan Daddy bangaren Amarya Humaira wacce taci Uban lace na gagara wani dark blue and Brown yanda zasu danyi matching da kayan Brown,Tace ai Nickname din Mijina Brown Dole mu sa Brown yau,Ana ta dariya ta Sha make up tare da Yan Kawayenta kadan.

Hafsat ma kayanta akwai Kalar kayan mijinta Bash a jiki,Haka Nafeesat din Mashkoor komai a tsari sukayi,Sameera wacce itama hakance ta diga kyau tana ji an daura Aure tace Zawarci ya Kare Allah bamu zaman lafiya Kawayenta suna Mata tsiya da dariya Suka ce Kai marya.

Bangaren Yar China cikin Yan uwansu ne da Suka cika gidan suka fara kawo labari,Kanwar Babar Yar China Salamatu tace ga Ogana ya bugo waya Yar China an daura aurenku an gama kece ta karshe an daura,Yar China Wanda yanzu ma ta shigo gidan ta dawo daga makeup,ta Sha wani dakakken material Sea blue yafi Shaddar Tawaga dark sosai da adon Golden a jiki,Yana wani walwali Yana kashewa mutane Ido,daurin dankwalin da aka nada mata da Golden headtie tayi kyau kwarai,dama gata fara sosai,dukka Dangin su Yar China farare ne yawanci gado Suka yo Yan Fulani ne usul Yar China ce tayi Kama da yan China Kalar Idonta da Dan shape din fuskar sai ta Zama Kamar ruwa biyu irin Babanta Dan China Babarta Yar Fulanin Nigeria Haka ta zama,kawayenta masu yawan jaraba gari Guda,wani gida me kyan gaske da girma ya sha tiles ko Ina a Nan ta sauki bakinta abinci iri iri na Yan gayu ta bayar aka yo Mata na saukar Baki,su Friedrice with chickens ta Sha hadin salat,ga Waina da Miya,sinasir,wani faten dankalin turawa da nama,Jullof rice,Dan Iyayin Yar China harda fura da Nono me yawan gaske an zuba a robobi kamar rufaida dink,gurasa ta Sha cabbage da Albasa da tumatur,harda Dambun shinkafa,alala,Tuwon shinkafa,ga lemukan roba da ruwan Roba da sauransu Yar China har makwaftan da suke mutunci sai da ta sanar musu Kar suyi girki ranar bikinta kowa yazo a Nan zaici ya sha.

Yar China sabo da surutu da tsokana kowa ya santa ta kwashi jama'a da yawan gaske,tana shiga wajen Iyalle taje tace Iyalle Kinga kwalliyata yanzu na dawo nayi sauri sabo da kar Ina can a daura auren ban sani ba,Iyalle tace an daura fa ga Salamatu Nan ta fada Miki,Yar China tace ai nayi tunanin Wasa take min au an daura Iyalle? Iyalle Tace kwarai,Yar China Fuska ta rufe tana kyalkyala dariya dangi suna ta dariya Ana kallon ikon Allah,Iyalle tace Umma salamatu na Miki Alkawarin dubu daya kafin ki tafi gida,Salamatu tace Yar banza fitsararriya abinci fa an Kai duk abinda kika ce wajen kawayenki,Habiba ta Ajiye na angwaye daban suna can gidan suna ta tsare tsarensu na Yan karya irinku can,Iyalle Tace gayu gayu ai mu akwai Harkar girma, Ana zafi Yar China ta dauki mufici tare da mikawa wata Yar Budurwa yar gidan Salamatu Yarinyar zata Yi 14yrs tace ungo Marsiyya duk inda nayi kina bi na a baya kina min fifita bana son kwalliyata ta baci tun kafin angwaye su zo.

Haka Yar China take yawo da yarinya tana Binta da fifita Wai ita Amarya,tuni Yar China ta Shiga gidan da Kawayenta suke Suka lullubeta da tsiya duk gasu Nan Yan matasa masu tarin kuruciya sai haukarsu sukeyi,Yar China ta dauki plate da cokali tayi kida rakacal...rakacal sai ta tsaya cik tace duk ku saurara kuji an daura Aure tuni babu wacce naji ta min Addua,ihu Suka

saki yeeeeee....sai Yar China wlh yeeew.....Duk sun Sha gayunsu sai kuruciya amma ba karya sunyi kyau,Habiba tace me Dj yazo dama munce ana daurawa zamu fara cashewa har lokacin Kai Amarya,Yar China tace iceko me Speakers Bakwai din Nan ne yazo? Suka ae mana,yawwa so nake a gigita kowa na unguwar nan so nake yau a San Yar China amaryace,Habiba kuje a fara sakin kida me fasa kunne,da fatan kunci Kun koshi? Suka ce ae har mun shirya na angwaye a palon da Muka ware za a sauke su,Yar China ta leka katon palon me kujeru na Alfarma ga girke girke daban daban an shirya na gayu gidan wata ce suna mutunci da Yar China shi yasa ta Basu gidan.

Washe gari da Yamma su Mummy duk sun Gama Shirin tafiya sabo da tasan Idan Suka yiwa Humaira Sallama tasan kuka zata musu sai basu sanar Mata ba gaba Daya da kawayen Suka tattara zuwa airport,Ahmad yaje rakasu Suma,sai da suka je airport Daddy ya riko Hannun Ahmad yace ya naji Shuru ne? da me fa Daddy ya furta da shagwaba,Daddy yace ba score har yanzu? Ahmad Yar kunya yaji yace Daddy verysoon,Nasiha ya sake masa sosai sannan suka Yi Sallama ya Rungume Mummy yace zamu Zo verysoon da My World,Marar kunya a Gaban Nawa cewar Mummy suna dariya gaba Daya ya musu Addua ya tafi Suma Suka Shiga jirgi abinsu.

Aamna yau ma Yar China Kawai ce Bata girki ita ta kaiwa lafiyayyen lunch da kanta taje ta Iske Tawaga ya duka a kasa Yana rarrafe Yar China tana bayansa Wai jaki jaki yake mata,Gashi ta daure Masa Ido da bakin kyalle,Yar China Bata sakko ba tace Aunty Balaraba kin ganni ajiye abincin an gode,Tawaga ya cire kyallen Yana Shirin cewa Yar China ta sauka tace ja muje sai ka kaini can bangon,Aamna tana ganin Haka ma Yar China ba kunya gareta ba ta juya ta tafi gida ma kawai,Karatun Qur'ani tayi sosai tayi Adduointa kasancewar me gidan baya gida Yana can shirye shiryen fara zuwa Office.

A saman Sallayar Bacci ya kwasheta har after 5pm ya dawo tana bacci Bai tashe ba ya wuce yayi wanka,Abinci yayi serving Kansa Yana ci Yana Santi har ya gama,sai da zai wuce masallaci ya tashe ta,tana tashi Tace Sannu da zuwa yanzu ka dawo? Murmushi yayi yace tun 5:20pm ,lallai nayi bacci Sannu da zuwa abinci fa? Naci tun dazu nayi wanka kije kiyi Sallah zanje masallaci,Okay ta furta sannan ta Mike ta wuce toilet.

Sai Bayan Kwana Uku Jibson ya fito Shar da shi har ya wani canja,su Bash suna ta Masa

dariya ana tsokanarsa,Ranar ne Kuma Ahmad ya fara zuwa Aiki Office,ranar Daddy ya Sha Kira a waya komai kafin yayi sai ya Kira a waya,sai 5pm ya nufo gida gaba Daya ya gaji Kamar an Masa duka abinka da ba'a Saba ba,Yana yin wanka Abinci yaci ko masallaci Sallar Isha bai iya zuwa ba a gida yayi Yana idarwa ya kwanta sai bacci,Ganin Haka Aamna ta gyara Masa blanket ta koma main Palo tana kallo sai ga Sameera taci gayu tare da Jibson Kamar Wanda zasu je wani party,Aamna tace Ango da Amarya Allah yayi fitowarku sai kace wasu kaji masu kwanci,Jibson suna wani zuba kamshi ya Sha shadda ita Kuma wani material ta zuba Malam peach,Jibson yace Ina mutumina? Aamna tace bacci yakeyi yanzu Bai Dade da dawowa daga Office ba Bai Saba ba sai bacci,Jibson yace ai Dole muma kafin mu Saba sai munji jiki,Hannun Sameera cikin nasa sai kunya take ji tana murmushi Kawai,Aamna tace ke Sameera Ni bana son kunyar Nan shi yasa Yar China ke birgeni da itace da yanzu Muna zuba Hira,Jibson yayi Dariya tare da furta ai wannan da kika ganta authentic ce, genuine and Lovable,Dariya Aamna ta dinga Yi tare da furta yayi kyau,suna ta Hira Yana ta wani koda Sameeransa.

Bayan sati biyu da bikin su Yar China duk sun Hada kansu suna zaman su lafiya sun Zama kawaye lokacin Kuma Saura kwana daya daurin auren Siyama,Hashim ya Kama gidan Hayarsa me kyau harda gate yasha tiles dai dai na rufin asiri,Iyayen Siyama ba laifi Kaya me kyau Suka Mata da Aamna akayi ake komai,ta bada gudunmuwa na kudi sosai da shi ma suka Yi kayan kitchen,Washe gari Saturday Amarya tayi kyau sai sheki takeyi ta Sha lalle da gyaran gashi 11am aka Daura Auren Siyama da Hashim,duk su Ahmad sunje group dinsu,Ango burinsa ya cika sai murna yakeyi ga albishir da Aamna ta Masa na karbar takardunsa an bashi Aiki zai daina aikin wahala,Da kwarinsa yake komai,Siyama Amarya dai ba yabo ba fallasa ta hakura Haka,Zuwa Yamma aka Kai Amarya abinta tana can yau ta hadu da Sarkin karfi cewar Baba Wanda shima ya Halacci daurin auren,Haka Mama taje bikin.

Aamna Kuwa da dare Ahmad ya tura driver ya dakko Masa matarsa,Suna Hanya Aamna tace Musa tsaya Amai nake ji, Musa da sauri yayi parking tare da mikawa Aamna bakar Leda har biyu yace Hajiya Yi anan sai ki jefa a kwalabati ai Aamna ko kula Ledar Bata Yi ba ta fita waje tare da tsugunawa ta Shiga sheka Amai Kamar zata fito da hanjinta,Musa ya Kira Ahmad yace Oga Muna dai dai sabon masallaci ka ganmu Hajiya ba lafiya gata tana ta Amai na tsorata fa Oga tun dazu take Amai yaki karewa,Ahmad gabansa ya Fadi yace me taci a gidan bikin? Karfa su kashe min Mata sauri ka kaita Hospital kafin na karaso,Sai da Musa ya jira Aamna ta gama tas ya Bata ruwan Roba ta wanke bakinta sannan ta shiga mota tana Nishi tace muje Musa naji sauki,Musa yace Oga Yana hospital yace na kaiki can,Aamna itama abinda takeji a jikinta kullum ya isheta Tace muje to.

Suna shiga Likita ta gani ta fada musu abinda take ji,Dake private ne Nan aka Mata wasu gwaje gwaje,tana jiran Result Ahmad ya shigo da sauri daga shi sai 3qtr da t-shirt fara,Zama yayi a inda take zaune ta jingina da bango tare da lumshe Ido,Ahmad yace Sannu My World,me kika ci a can? Aamna tace daga ganin Alala sai nayi sha'awa na ci Shikenan na fara Jin Amai,Ahmad yace Oh....me ya kaiki cin wani alalar biki kema,Ana zaune lafiya idan so kike Yi ai sai ki dafa da kanki.

Doctor ne ya karbi result din gwaji ya duba nan yace ranka ya dade na tayaka murna matarka

ciki ne da ita na wata biyu, Ahmad murna tasa yayi mutuwar zaune ya wani Bude baki Yana murmushi,Takardar ya karba a wani slow ya duba,Aamna ya kalla da fara'a ya rike kafadunta tare da girgiza ta sosai yace I make it my world,Haba Ni San Ina buga game din Nan dai dai ah ki tayani murna na samu first score,kallon Doctor yayi yace Likita mace ko namiji? tsaya karma kace min Namiji Baby girl ce ko? Zanyi Yar Budurwa kwana Nan,Ya kalli Aamna yace ki dinga Mata irin Calabar Nan tawa ta da kin tuna? Ai kullum da ita Zan dinga fita sai duniya tasan King yayi 'ya,Likita ya Bude Baki Yana kallon Murna Ahmad ya mike ya Hana Kansa sukuni gaba Daya, Doctor yace Dan Bamu waje Zan Mata wani gwaji,Ahmad yace ban Gane na baku waje ba? Ina mijinta wallahi baka Isa ba nasan latse latsen Nan da kukeyi zaka Mata ka Kira mace ta mata,sabo da ka Mai Dani gara ka kalli matata one in million na barta ka saki wannan shegen labilen naku ka latsa mata kafafu da ciki baka Isa ba bada Ni ba.

Likita yace Allah ya bada Hakuri ya Kira mace tazo ita tayi abinda ya dace ta basu shawarwari da Maganar zuwa awo etc.Aamna karar murna ta saki da sauri Kuma ta rufe bakinta tare da furta au na manta,Ahmad yace Adana ta sai munje gida,Hannunta ya rike Suka taho a hankali,Musa yace ya maida motar gida,tsohon me gadin Ahmad an Kara Masa matsayi ya tashi daga me Gadi ya koma Driver sabo da Amana irin ta Musa,tun kafin su koma gida Ahmad yace a shirya yau akwai party a gidan,Su Jibson duk Suka Zama ready Suka tafi da matayensu sashen Ahmad suna Jiran dawowarsu,Kafin ma Ahmad ya dawo Su Jibson an tanaji lemuka wannan karon babu Shan barasa,Tare da Aamna Suka shigo,tana rike a hannunsa,Ahmad ba jira yace a goal,Suma Kamar Yan siyasa Suka amsa da a goallllll......a goal....suka ce a goallllll......Yar China tace na Gane zancen,Ahmad yace na Zama Daddy matata tana da ciki na 2mnths tafi suka fara raf raf raf.....Jibson yace music .. Bash ne DJ ya danna,Su dai matan Dariya suke ta Yi,Yar China harda cewa a kashe kida sai na fara rera Mata wakar Dana tanaja,aka tsaya Nafeesat tace Muna jinki,Yar China ta fara Waka wai me ciki turtsi bulli.....me ciki turtsi bulli,Tawaga yace a amshe mata Yana Tafi suka ce Suma Me ciki turtsi bulliiii me ciki turtsi bulliiii....Tace ta kasa Zama,Tawaga yace turtsi bulli harda tafi sauran har Ahmad Dariya Kawai suke yi,Yar China taci gaba da cewa tsaiwa ta gagara....Turtsi bulli....Tawaga ya sake Amsawa,Aamna tace wannan ai wulakanci ne wallahi Zan rama, Ahmad ta kalla wannan tijarar daka min fa,Cikin murna Bash ya Danna kida Aamna sabo da kunya guduwa tayi ta kasa Zama sun Dade suna shagali suna ta tsare tsare.

Ahmad harda cewa a Ina za a Kama ayi suna? Humaira tace Kai Yaya ko kunya,Hararta yayi tayi Shuru tana dariya,Hafsat Tace ba Wani suna an daina yanzu,Inji uban wa? Cewar Tawaga zamu samu karuwa baza muyi murna ba sai mun kashe kudi,Nafeesat tace Ni dai nice me kula da me jego,Yar China Tace Muna wajen Bikin suna mu Allah ya sauketa lafiya,Ahmad yace Halina Dake hankali Yar China,ba Wanda yayi Addua sai ke,party fa kace za ayi cewar Mashkoor,to naji an Gama kuje Kun korar min ita sabo da kunyarku,Jibson ne ya fara mikewa ya rike Sameeransa zai tafi Ahmad yace gobe karku manta akwai zuwa Office,Allah ya kaimu suka tafi Yar China kin tashi tayi tace Allah bazan koma da kafata ba sai dai ka goyani,Abu me sauki cewar Tawaga ya goyata Kuwa Suka tafi Yar China akwai son wasa Kamar me.

Washe gari Ahmad waya ya Kira Mummy ya sanar Mata ta dinga Murna tana bawa Daddy

labari,su Saddeeq da Mufeedansa sai murna sukeyi,Basu Dade ba Kuma ya dauki Aamna Suka tafi Lagos,can ta Sha kallon kudi satinsu Daya Suka dawo,lokacin Kuma Ahmad yana Shirin tafiya da Aamna da Baba Sudan suje gano Rahilu,Baba ya rike wuta sai anje da shi,Kuma ya kamata aje da Baba sabo da shi ya rike Aamna,Baba ranar da Ahmad yaje ya sanar Masa ya Zama cikin shiri bayan an Masa passport,Baba yace Nima ka siyo min Sut (suit) irin ta Rahilu da ita zanje Masa Nima,Ahmad ba musu ya nemowa Baba size dinsa kala Uku,yace da jallabiya shima sai ya saje da Rahilu a Sudan.

Ranar da zasu tafi Aamna harda Shan abaya baka,Ahmad shi dai kana Nan Kaya yasa Yan ubansu,Baba kuwa harda sa jallabiya fara yayi Nadi da rawanin larabawa,Baba yace nasan mutanen Sudan ma tun a jirgi zasu fara Yi min larabci su Aamna suna ta dariya Mashkoor ya ajiyesu a airport Basu Dade ba jirginsu ya daga,Baba yace wayyo kunne na ya toshe wani dummm nake ji ice ko kamfanin mu na Najeria be? Basu iya jirgi me kyau ba,Ana ta yiwa Baba Dariya,duk ma'aikaciyar data wuce sai Baba yace baiwar Allah abincin jirgi ko baza a Bamu bane sai dai suyi ta kwantarwa da Baba hankali suce za a bayar idan lokaci ya cika,Wata Yar Budurwa ta fito cakwas cakwas itama ma'aikaciyar jirgi ce ta dafa kujerar Baba tare da cewa Baba a sa Belt,Baba yace yau Naga fitsara da gani ba'a kulla abin arziki ba ace ma'aikatan jirgi gaba Daya Yan Mata fella fella suke yawo suna kashe ma Ido sabo da a koya min fasikanci idan gaskiya ne a zuba maza Mana su dinga dakawa pasinja tsawa wallahi Baku da halin arziki kunyi asara an maida ku hotiho Ana talla daku a sararin samaniya,sai kunyi sama sosai sannan kuke tafka tsiya wallahi da Allah kuke bada mu ba,sai Dariya akeyi a jirgi Baba Yana ta masifa har aka kawo abincin jirgi.

Baba yace aikin banza shinkafa ce da nama Baba ya cinye nasa ya dauke na Aamna ya cinye,Ahmad ma ya bashi nasa ya cinye Baba yace abinci Kamar na Yaron Yaye Haka dama jiragan suke wannan rowar mutum ya biya kudi a bashi abinci naira Hamsim a dubu goma.
Baba Yana ta murna ya fita kasar waje zaiga Sudan yankin Larabawa,sai da suka sauka a jirgi Suka Shiga lafiyayyar Taxi Suka shigo har wata state,Baba yace me Zan gani? Sahara nake gani fa Ahmad,me Zan gani Haka? Yo wannan ai gwara naje Kano Kuma Sudan din ne? Aamna tana ta da dariya,Baba yace cab Dole Rahilu ya Shiga Uku a Haka amma Yaran wasu masu kudin suke Mana Iyayi Ana wallahi Yana can Sudan Yana karatu,tana Sudan tana karatu,ai wlh gwara Kayi Ado bayero iniversity (University) Ahmad Yana so ya dan rike ko Aamna amma yasan Baba.

Suna tafiya a mota Baba yaga wani Dan fari Yana tafiya a titi Baba yace wannan da gani bako ne shima baiyi Kama da su Rahilu ba duk yanda akayi daga Seria yazo gashi Nan a koshe bulbul,Driver dai suna ta larabci da Ahmad Yana Kiran Rahilu Yana Basu Address,Baba ya kalli wani Symbol kato Ana tallan omo Klin,yace Ashe Daya muke da su kaga jaraba Klin a Nan inama Aishatu tana Nan Sarkin ta'adi tazo ga mutuminta a Nan ma,Baba shi kadai yake surutunsa har Suka sauka a wani gida Kato me bene Hawa biyar, Aamna tace Baba anzo gidan Abbi na kaga gidan me kyau,Na Haya ne uban wa yace Miki gidansa ne,?Ahmad Yana jinsu dai suna Fitowa a taxi sai ga Rahilu ya fito sanye da jallabiya wata baka,Baba yace kaga bakin mutum ga bakin Kaya Rahilu manyan gari wuya kamar na zalbe,Rahil da fara'a ya tarbesu ya

dauki akwatin Ahmad Suka nufi ciki,wani Palo yasha adon Larabawa shi aka kaisu,Babba yana kallon gidan Yana Kallon Rahilu yace Yan karya an iya tsara gida,Matar Rahilu ce ta fito wata balarabiya fara tas,ta zauna sai da Ahmad Suka yi maga suka gaisa su Baba basa Jin yaren,Wata ce ta fito itama fara ce Amma ba Kal ba irin dai Bata fi farin mu na Yan Nigeria ba,bayan sun gaisa itama ta Mike tayi ciki,gabansu aka cika musu da Abinci iri iri na Larabawa,Baba yana kallo,wani kwano me kyau ya bude yaga kubewa Danya Guda Guda a cikin kwano da wani ruwa tsululu Yana yauki ya Sha tafsrnuwa da kayan Hadi,Wani kwanon ya bude yaga wani Abu shi kamar Tuwon Zuma da Dabino,Rufewa yayi ya Bude wani kwanon yaga miyar ganyen kabewa,Can Kuma wani tuwo ne Kamar na madara har da Cheese,Ga Fruits iri iri,Baba yace Rahilu Ina shinkafa inda Muka Fi wayo,Dan Iskanci kasan wannan ba abincin mu bane na awaki ne zaka sa a kawo mana,kalli kubewa Guda Guda, Rahilu Yana murmushi yace yanzu shinkafa zata Zo harda lemon Tsaki,Karka sake ku matsa min lemon tsami salon na barke da zawo.

Suna zaune sai ga wata shinkafa taji Hadi da hadin salat,Sai ga kaji an kawo,Baba yace yanzu naji zance Baba ya sauka kasa ya shiga cin Abincinsa Suma su Aamna suka gyara Zama tayi Serving Ahmad,Bayan sunci sun Sha suka Yi Sallah sannan aka kirawo Yaran Rahilu Suka dinga gaisar da su,Dake suna makaranta suna Jin turanci sai suka dinga magana da Aamna,Baba yace mu Kuwa sai kallo Allah wadaran rashin Boko,Sai dai Kawai Baba ya dinga cewa Hey...Hey....Ahmad Yana ta dariya a zuciyarsa yanda Baba yake ta aikin Furta Hey ga Yaran da yawa,Yaran Rahilu basa Bari suyi baccin kirki sabo da Hayaniya, Baba cikin dare kullum sai ya tsine musu Wai sun hanashi bacci,yace Rahilu Dan Iskan banza ya dinga dirkawa Mata ciki suna ta zazzago yara Haka kamar zomaye.

Masauki me kyau aka Basu Aamna cikin Yan uwanta Mata ta shiga,washe gari Kuwa Daya gidan Rahil Suka je Suma Mata biyu da Yara da yawa Ahmad yayi Larabci ko turanci Aamna ma Haka Baba Kuwa sai Hey kawai,Nan ma kwanansu Daya aka raka su wajen Dangin Aamna na uba sannan wani babban matashi Mahmood shi ya dinga fita da su Aamna yawo suna ganin gari suna pics,Baba duk inda akaje sai yace ayi Masa pics shima,Ana dauka zai ce da Aamna maza dorani a yanar gizo duniya ta ganni a Sudan,Rahilu ya Gama tsorata da cin mutuncin da Baba ke Masa amma wannan lokacin sai yaga Dan kadan ya masa,kwana hudu tsakani Ahmad ya kafe shi gida Za'a taho Rabonsa daya kwanta a jikin matarsa kwana hudu kullum tana wajen Yan uwanta shi bazai iya ba,Baba yace Kai Nima na gaji da garin Nan mutane kamar konannu kowa baki sai Larabcin tsiya akan me,Aamna ita tana Jin dadin haduwa da Yan uwanta sai Ahmad ya yini Bai ganta ba,ai Kuwa Yace gida,kwanansu biyar Suka dawo gida Nigeria Aamna tana ta faman Fushi da shi har Bash ya dakko su a Airport aka sauke Baba a gidansa da tarin tsarabarsa.

Baba Yana shiga ya Rungume Mama,Tace yau me Zan gani Baban Zuhra sai kace yaro? Baba yace na dakko darasi baza a barni a Baya ba,a gabana Rahilu yake Rungume matansa Yana musu kiss da shegen bakinsa kamar Kofar gari,Ni nafi Rahilu fasali shine bazan Yi ba sai ace na tsufa,shi yasa aka Yi Mana nisa a duniya,da Allah tsaya Rahilu ya mannawa Mama kiss a kumatunta biyu yace Haka akeyi yanzu duniya ta waye anci gaba kina Nan a dinkime Baki

zaga duniya kin Sha kallo ba,kije Sudan kiga yanda tsoho tukuf Wanda ya haifeni yake tarairayar matarsa itama tana Masa,ke Baki waye ba,Mama tace Indai wannan ne bada Ni ba,ai Kuwa wallahi Baki Isa ba kullum sai na dinga Miki da safe da Rana da dare ko ta karfi,Baba ya zuge akwatunsa ya dinga fito da tsaraba daga Kan sutura har su turare da lallen Sudan kala kala,Ya mikawa Mama yace Henna sunan wannan lallen Haka ake cewa gobe ki Kira me lalle ta lallaba Miki shi,karki sake da Yamma na dawo daga kasuwa Banga Henna na tashi a Hannunki ba,Mama tace Kai Baban Zuhra ka canja gaba Daya ka koma Wani Dan bariki,Baba yace shine ai wlh idan Baki Yi Henna din nan ba sai nayi sati banci abincinka ba Karki ce ban fada Miki ba yawwa ya Mike ya shige daki Yana cewa na koyo soyayya wajen Larabawa Zo kui cude Ni ki wanke min gadon bayana,Mama tace Ni wannan Sudan din Bata Yi ba wallahi Ka dawo Dan Iska gaba Daya,Baba daga daki yace Dan Guguwa na dawo karewarta.

Tun kafin Bash ya Kai su Aamna gida Ahmad ya like ya nane mata ya hanata sakat,kwana har hudu ko Rungume matarsa baiyi ba tana can wajen danginta ko ya kirata a gurguje take zuwa ta tafi Sam shi baiji dadin Sudan ba ga Baba ya hanashi ya Kama hotel bare ya dan samu ya shakata da Aamna a sudan shi yasa yaji Kamar akan Kaya yake,Aamna Kuma haushinsa take ji yace sati biyu zasu Yi Amma kwana hudu Kawai Ana biyar ya kafe su dawo gida ko Yan uwanta Bai Bari sun Dan Shaku ba,Bash Yana kallonsu ta Mirror Aamna tana Fushi Ahmad ya manne a jikinta Kamar zai shige cikinta gaba Daya ya haukace baya ganin kowa baya tunanin wani Bash ma Yana kallo,Aamna ta hade rai tace Kawai ko Gama ganin dangina banyi ba ka damu sai fada kake min Kai ka gaji gida zaka taho,yanzu ka min Adalci? Baki Ahmad ya bude yace kutmar...yace yanzu duk abinda nayi Miki banyi komai ba? My world???? Na kashe kudina na dauke ki har Baba Muka je har can sabo da na faranta Miki kiga danginki Ashe ban birge ki ba? Yanzu da Allah bai hore min ba da wanne kudin Zan kaiku? Kin min Adalci kenan? Fine and Good zamansa ya gyara ko yatsa Bai sake rike Mata ba.

Sai a ranta ta tuna Bata kyauta ba,tunda take arayuwarta Bata San ma inda Dangin Ubanta suke ba sai ta Silar Ahmad,Daddy dinsa kudi ya saka ya dakko Mata Babanta har Nigeria ita Kuwa me zatace da su,Jikinta ne yayi sanyi ta riko Hannun Ahmad ya fisge Hannunsa,Bash ta Glass yake kallo Yana ta dariya a ransa,Yana yin parking Ahmad shi ya fara fita yayiwa Musa Magana ya dakko Masa jakarsa,Aamna ta dauki tata da kyar ta bishi da sauri tana kwala Masa Kira My King kayan Nan sun min nauyi cikina zai zube,ko kulata baiyi ba,a compound ta bar kayan tayi ciki,Bash a waya ya Kira Ahmad yace please karka kulata kuyi fada,kayi Hakuri akan Dan abinda Bai Kai ya kawo ba haba King, Ahmad yace Yarinyar ta rainani da yawa in kashe kudi in kaita har can kaji Maganar data fada min,Matane sai hakuri King Haka suke sai anyi Hakuri shine zaman Auren karka biye mata Shedan ya dinga hadaku fada please, alright Ahmad ya furta tare da kashe wayar,Wanka zai shiga Aamna ta shigo da sauri tana cewa I'm sorry My King, me kika Yi? Aamna tace laifin da nayi maka,Baki ya tabe yace ba Wani abu ai ya shiga wanka,ya fara wanka kenan Aamna ta shiga tare da tube kayanta taje,ko kulata baiyi ba,Tace har yanzu Fushi kakeyi dani? Fushin me Kuma? Gashi Nan kana share ni kayi Hakuri nace kaji ta furta da shagwaba tana riko hannayensa,a kirjinsa ta kwanta ruwan Yana zubo musu ta Rungume shi tare da fashewa da kuka,Yaron cikinta ya tuna ya shafa bayanta yace it's Okay ya wuce,Ki kiyayeni Aamna wallahi Dan kece kin Sanni a baya bana son taurin Kai da

raini,Dan Ina sonki bazai hana na dauki mataki a kanki ba,Ni bazan dinga daukan wannan abin naku na Mata ba na shirme,ke ba yarinya bace,Ya isa Allah bazan sake ba cewar Aamna,cikinta ya shafa yace Babyna ya fara girma,Aamna tace muyi sauri naje na Mana abinci,nayi Order fa za a kawo kiyi zamanki sai gobe Inshaallah.

Wanka sukayi tace yunwa nake ji ka danyi Hakuri muci abinci sai na baka manta uwa,Ahmad Yana Jin Dadi harda cewa yau kwana zamuyi ko? Aamna tace as you wish,I'm all yours,I miss you ya furta,miss you much more My King,Abinci Musa ya shigo da shi wata sakwara da miyar kwai taji nama,yasan tana sonta shi yasa sai wani gasashen Naman rago Suka baje ya Bata a Baki da Kansa Suka koshi sannan ta daga Kai tana Shan Watermalon Juice ya fara zare Mata rigar wankan da take jikinta Dake ma Basu cire ba Suka zauna cin abinci.
Kirjinta Wanda Suka sake girma sunyi sake sake sai kyalli sukeyi ya shiga Matsawa Yana sarrafa su,Yace dama dai su dinga zubo da ruwan milk,Aamna tace sai an Haihu to,Allah ya kaimu a dinga Dan rage min Nima Ina zuka,sunyi missing juna kamar zasu cinye kansu Haka suke sarrafa juna suna wasanni iri iri daga Nan suka fada Manta Uwa.

Washe gari da Rana 2pm su Habiba su Hudu kawayen Yar China suka zo mata,ai Lokacin Tawaga Yana bacci ihunsu Sai da yasa ya farka a tsorace Yana daga Bedroom,Yar China yake jiyo muryarta tana Yan Iska sai yau?Fatima Bala Baki da mutunci Wallahi ai nasan inda na ajiyeki,Fatiman da aka Kira Tace Sorry kawata nayi laifi banzo biki ba wlh zazzabi ne ya rufe Ni,Habiba ta kalli Yar China Kinga yanda kika koma Kuwa Yar China? Kinyi kiba kinyi wani fresh Haka,Yar China tace sirrin Yana jikin Angon,Shewa sukayi da tafi su a Dole Shegu,Ya zafi Yar China? Yar China Tace wanne zafi? Duk karya Mata keyi dadi ne Kawai,Habiba tana Dariya tace kice mu daina jiin Tsoro? Ku daina Jin tsoro duk karya ne cewar Yar China Kawai ta barsu a haka,Ina Angon? Bacci yakeyi ku rage Voice dan Allah karku tasar min shi ya dawo dazu Allah sarki yaje Nemo Mana halaliya  a gajiye ya dawo daga Office a Haka ma Basu fara dadewa a aiki ba,Tafawa sukayi wata Maryam Tace kice kina bashi kulawa kawata Yar China tace ke dai bari jira nake ya tashi naje na wanke shi tas na shafe abina da mai,Sai dariya da shewa,Yar China ta kawo musu kayan ci da Sha harda Dambun nama, Tawaga ne ya sakko sanye cikin Shadda da Alama fita ma zaiyi,Yar China Tace Kun Gama Dani Kun cuceni Kun tashi My Man,Dariya sukayi suna Gaida shi ya amsa da sakin fuska,Rada yayiwa Yar China a kunne Wai ya tafi wajen Ahmad sai dare zai dawo,Su Habiba Yana fita Tace kina wuta Yar China Allah ya bamu I Taku,Yar China harda gyara zaman rigarta tana basarwa tare da cewa Ameen.

AsmaBaffa
10/29/21, 7:45 PM - Buhainat: 🌵🌵DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

NA KUDU NE

DUNIYATA AAMNA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

131-135

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne

Ummu Amaturrahman
Mrs mukhtar
Aisha
Maman Muniba

Sai Yamma likis bayan kawayen sun tafi Tawaga ya dawo ya Iske Yar China tana wanka,Direct Toilet din ya shiga sai da ta tsorata,Fuska ta kwabe tana cewa ka bani tsoro,Yunwa nake ji ki fito ki bani abinci, Yar China tana wanka tace Babu lafiya Tawaga na Jin

yunwa gani Nan,Dariya yayi ya fita Yana Fitowa da guntun towel dinta tayi kasa da sauri sai gata da tiren Abinci tana Subhannallahi gari yaci wuta Mijina na Jin yunwa yaga Friedrice ta Sha Hadi ga couslow da soyayyar kaza,Yace yaushe kika Yi wannan girkin? Ba naji kince Jullof din taliya zakiyi ba? Naga taliya Bata dameka bane shi yasa na canja shawara,tana serving dinsa ta tsuguna can Kuma towel yayi guntu da yawa Ana ganin Yar China tasan Yana gani amma Taki gyarawa tana satar kallon Tawaga yanda ya daina komai ya koma leken Yar China,ba tare da ta kalle shi ba Tace Allah ya yaye maka Wlh,muyi wanka tare kullum sai ka gani Amma baka koshi,Dariya yayi yace waye yake koshi da abin Dadi ya furta tare da jawota saman cinyarsa ta zauna Yana cin Abincinsa a haka.

Yar China tace Anya Kuwa ban samu ciki ba,sai da tasa Tawaga ya kasa hadiye Abincinsa yace me? Sati Nawa kwata kwata da Auren wata Daya kice kin samu ciki yaushe ma naci amarcin?Yar China tace kaga Allah maybe Ina da ciki sabo da lokacin period Dina yayi amma banyi ba,Tawaga yace au lokacin period yayi? Yar China tace tun last week Amma banyi ba,Tawaga yace Amma Baki fada min ba so kike Kawai ki fara period ban shirya ba,Shirin me zakayi Kamar Kaine me Yi tana Dariya ta tambaya,yace banci Amarci sosai ba ya kamata ace kafin ki fara nayi final,Yar China tana ta dariya ai Kuwa da sai dai kaji na fara yanzu ma maybe time ya canja min,Tawaga ya fara cin Abincinsa da sauri sauri ya gama,Wankan ma da sauri yayi ya fito ya Iske Yar China jikin Mirror ya jawota jikinsa tare da cewa bana bukatar kwalliyar ta fili,kwalliyar ciki nake muradi,Yar China Sarkin Dariya tace to saka min tozalin,Tawaga ya dauketa tare da furta farin gani kenan tozali,Saman bed ya direta tace Yaya Gazal me Dadi zaka saka min,Dariya Tawaga ya shiga Yi daga cewa Tozali shine harda Kara gishiri Wai Gazal,da waka ta Rungume shi tace a sa min Gazal me dadi...sa mini kaya...a sa mini Kaya,sa Mata....sa Mata....a sa mini Kaya.....Tawaga ya dinga dariya sabo da Yar China ta Gama lalacewa yanzu fitsararta take Masa ba ruwanta,komai girman magana fada takeyi.

Dama shi Haka yake so idan zaiyi Harkar nan Yana Jin dadin Yar China tana Kara Masa kaimi da Jin dadin Harkar.

Washe gari Sunday 5pm su Ahmad suna gidan Mashkoor a katafaren palonsa,Nafeesat ta kawo musu kayan motsa Baki ta Basu waje suna Hira, Mashkoor ya kalli gefensa dama da hagu harda leka jikin kofa ya tabbatar Nafeesat Bata kusa ya kalli Jibson yace na yarda da maganarka Virgin wahalar sha'ani gareta,har yanzu Taki sabawa da abin,Ina tunanin tana da Yan shekarunta Banda matsala amma har yanzu ta kasa sabawa gata Nurse Guda amma Ina Wai Dan wulakanci ma Dana tambayeta nace Wai har yanzu ke baki Dan Saba bane Wai sai cewa tayi Mashkoor ya gwada muryar Nafeesat Wai sai ce min tayi to ai Kaine Baby Dick din naka tarago Guda ne,Su Jibson Suka dinga dariya harda rike ciki, Mashkoor yace Wai Mene ma tarago? Ahmad Yana ta dariya yace ai kasan jirgin kasa ko? Mashkoor yace sosai,to wannan datsi datsi na jirgin kasa zaka gani gida Gida ai shine taragon jirgi, Mashkoor ya dafe Kai Haka taci mutunci na ashe? Da nasan Haka ne wlh sai taga bacin raina taragon jirgi fa? Jibson harda rike ciki Yace da Kuna ganina a banza Kuna cewa ai Ni ba mace ma Zan aura ba ai duk sai Kun Gane kurenku, Mashkoor ya shiga nanata kalmar taragon jirgi fa,suka dinga dariya,Brown yace ai Ni tawa ta washe ta Saba Kaya nake ja,Harara Ahmad ya balla Masa sabo da kanwarsa ce,Brown yace bani da jaraba a baka auren kanwa ba babu dama kayi magana,Dariya sukayi

Bash yace ai Ni Nawa surukin ba ruwansa tunda ya bani Hafsat ya kyaleni to shima yasan Yar wani  yake cinyewa,Tawaga Yana jinsu Yana dariya,Yar China ce ta shigo Basu ganta ba Amma sunji muryarta tana yiwa Nafeesat tsiya Nafeesat kiji tsoron Allah Mene duniyar kin wani makalewa Miji ba fita ba Shiga da Allah kizo muje mu hau lilo muyi wasanmu,Su Tawaga suka dinga kyalkyala dariya ita Yar China Wasa ne a ranta ma,Nafeesat tana Dariya tace rufa min asiri lilo Kuma sai kace Yar Secondary,Yar China Tace har abada a Haka zaku Kare ku zauna ku tsufa da wuri mazajenku suyi muku kishiya,ku Sam Kamar Baku waye ba Allah yasa ma Mijin naki kina bashi hadin kai,Da sauri Mashkoor yace Allah ya Miki Albarka duk da bakya jina Yar China Bata wani bani komai da kyar nake lallabawa kin gani na Zama Maraya.

su Jibson Suka dinga dariya,sai Kuwa suka sake ji Yar China tace karfa ki maida mijinki Kamar marayan karfi,Nafeesat tace kiyi a hankali suna palon can zasu iya jinki,Yar China ba sirri sai ta Kara daga Murya to Mene Dan sunji Ni Allah yasa nasiha nake Miki ba zugaki nakeyi ba,Ke kina Likita ma ku da aka koya muku a aji ko Baki karanta Biology bane? Anatomy to gashi Nan an Zana kayan aikin a jiki har can ciki bala'i bature sai da ya dauko hotonsa,mu da muke mata Muna da shi a jikinmu ba mu San cikin ba Amma bature sai da ya bude sirrin,Ai wlh da nice nayi Likitanci ai da ba Haka ba,ke kullum wani salab salab dake ba Energy ko ba Vitamins ne da yawa jikinki? Nafeesat kiji tsoron Allah ba abinda ba a Baki na kayan Dadi Amma kullum wani salab da ke,Nafeesat tana ta dariya yanda Yar yarinya ta tsaya Kamar uwarta,Yar China tace shine Your eyes,da nice nayi degree da anga bugaggiyar Yar duniya wlh amma ke kenan a kunshe a gida,Rannan Ina kallo mijinki Yana Miki magana kin wani hade rai kina latsa waya kin wani shareshi wayarki ta fishi muhimmanci.

Nafeesat tace na shiga Uku da sa ido ke Yar China ki raba kanki da sa Ido,Mashkoor Yana can Palo Yana amsa Hirar yace Haka kikeyi Yar China gaskiya ta fada,Baki Yar China ta tabe tace shike nan kici gaba da feeling Big girl ke me degree ko nurse kina daukan salary to ai shike Nan,Nafeesat a hankali tace ke Nifa har yanzu zafi nake ji idan Yana Yi ko wani abin kuke Sha ki sanmin? Yar China ta dinga dariya, Mashkoor yace banji me Nafeesat Tace ba kunji suna dariya,Allah dai yasa Yar China ta gyara min ita,Yar China tace muma ba sabawa Mukayi ba Hakuri mukeyi amma Ni dai yanzu bana Jin wani zafi Zan dai San Miki wata zumar tsumi da Yaya Salamatu ta kawo min,Tawaga yaji a kunnensa shima yace a can palon Wanda Kawai su Ahmad me zasu ji wai ban yarda ba a bayar Mana da tsumi ba bazai yuwu ba ya Kare na Shiga wani Hali,su Basu ji ma me Yar China Tace ba Amma shi Tawaga ya ji fes.

Gida Yar China ta koma ta Shiryawa Nafeesat mugunta ta kawo Mata na karfin sha'awa da Niima,Dan kadan ake Sha Amma Tace shanye du daga yau kin daina Jin zafi,Nafeesat ta karba tana murna tace Ina da magunguna Nima Amma bani da irin wannan,Yar China tana boye dariyarta tace wannan na daban ne shi na Hana Jin zafi ne,kafin dare yayi yayi aikinsa,Nafeesat ta daga Robar karama ta shanye Nan take,Yar China tace Bari in tafi gida Nima na Sha Nawa idan kinji zam zam gobe kizo na Kara Miki Ina da shi da yawa,Nafeesat harda rako Yar China tana godiya tace kina birgeni gaki yarinya amma kinfi manyan ma,Yar China tace Haka nake ai sai gobe ko a waya Kya bani labari Suka Yi Sallama Nafeesat tana ta godiya ta koma gidan.

Minti biyar Nafeesat ta fara Jin canji a jikinta,Ji tayi Niima duk ta sakko Mata Kamar me,Sha'awa ce me zafi ta riske ta,ji tayi ba Wanda take bukata sai Mashkoor,Abu kamar Wasa tun tana basarwa har ta kasa,girki ta daura Amma ta kasa ta kashe gas din tare da dawowa Palo ta zauna tare da zuba tagumi,Kwanciya tayi Nan ma ta kasa ta Mike agogo take kallo tana cewa sai yaushe zasu Gama Hirar Nan ne su dawo gida,6pm ta gani tace Kash yanzu ma nasan sai sunyi Sallah maybe ma har Isha sai sunyi,Kasa daurewa tayi ta Kira wayar Mashkoor Yana dagawa tace sai yaushe zaka shigo?sai Munyi Sallar Isha,lafiya? Tace lafiya shike nan ta kashe wayar.

Kasa hakura tayi ta tura Masa Text me Zan dafa maka? Ya Mata Reply da kin manta nace tea Kawai Zan Sha da dare,Okay tace,Zirga Zirga ta Shiga Yi tana safa da Marya ta ciji yatsa,ta koma saman bed ta kwanta,mikewa tayi zaune tare da Jan Tsaki,wanka ta Shiga ko zata sama salama Amma Ina Sam,Daure take da towel ta sake tura Masa da text yau da wuri zanyi bacci ka dawo da wuri, Inshaallah yace kawai,Nafeesat bata hakura ba tace Ina yin Sallar Isha zan da key a kofata ka dawo da wuri please,Shi Mashkoor Bai kawo komai ba yayi tunanin ma tsokanarsa takeyi dan yaje ta ja Masa Rai,sai da sukayi Sallar Isha sannan Yar China ta dinga Kiran Tawaga a waya Kamar mayya,Yana dagawa My Man Dan Allah ka dawo na gaji da Zama Ni daya,Ya lallaba abarsa ko mintu biyu ba ayi ba ta sake Kira Tace kasan fa nayi missing dinka ka taho gida Ni gaskiya,Kafin yayi motsi ta sake sambado kira tace kazo kaga kwalliyar Nan idan Bata Yi ba na canja maka wata,Mashkoor yayi tagumi yace kaga masu sharafi,Kuna Sharafi a kasar nan,Basu San Jibson ya tafi gida ba tuni sai gani sukayi baya Nan suna kallon gidansa Suka hango karshen rigarsa ya shige ciki,Brown yace kaga mayen Sameera ko Sallama,Brown yace karku manta gobe zamu je gaisar da Abbana Yana ta min masifa akan Jibson ya aure Masa Budurwa,Dariya sukayi Ahmad ya mike yace nasan tawa ba irin ta kowa bace tana can tana jira, Haka kowa ya nufi gidansa.

Mashkoor Yana shiga mamaki ya kamashi yanda Nafeesat tasa rigar bacci sharara komai nata a waje matar da a baya idan taga dare yayi sai ta saka wando jean pencil Wai dan Kar yayi Mata wani Abu ita zafi take ji, Mashkoor yace a ransa ko Yar China ce tayi gyara? ai Kuwa Zaki ga taragon jirgi iya ganinki.

Murmushi ta sake Masa me tsada a ransa yace uhm anga Taragon jirgina za a min wayo,basarwa yayi yace kinyi kyau,taga ya Saba like Mata sai taga yau Sam yaki ma ko taba Yatsanta,tana karairaya Tace Bari na kawo maka tea din sai mu kwanta ko? Mashkoor yace kawo Amma sai dai ki kwanta ke daya Ina da aikin office Zan karasa a gida kafin Monday,Wani dukul Nafeesat taji Kamar zata Yi kuka tace ko laifi na maka ne? Laifin me Kuma? Okay ta furta tare da kawo Masa tea,yau itace harda Zama a cinyarsa abinda take Jin Tsoronsa,Yana ta murna a ransa,Tea din ma yau a Baki ake bashi Yana sha,Har ya gama ya jawo system dinsa Yana dannawa ba Uwar da zaiyi amma  yace Aiki zaiyi,Zama tayi tare da kafeshi da Ido kamar zata lashe shi.

Rungumeshi tayi ta baya tare da kwantar da kanta a bayansa,a hankali yace wayyo Zafi yanda take ce Masa idan ya fara harka,Baby zafi ne dake,tunawa tayi Sanda Tace Zafi ne da shi,Wato ramawa yakeyi,Wata wutar Sha'awa ce ta sake ruruwa a jikinta,ta janye System din

tare da kashe wa ta koma gabansa ta Rungume shi suna facing juna, Mashkoor da kyar yake fuskewa ya Furta da Allura kike Yi zafin Hannu Zaki Yi,yanda ta fada Masa Wai da Allura yakeyi zafin Hannu zaiyi sabo da Yana saduwa da ita tana Jin zafi take fada Masa Haka,Kuka ta fashe Masa da shi tace Kai baka manta abu to kayi Hakuri ai kasan zafi Dole naji tunda Virgin ce,yace to yanzu me ya faru kike bukata? Hawaye ya sake zubo Mata tace Yar China ce tsinanniya ta bani wani tsumi tace maganin Jin zafin da nakeyi ne, Mashkoor ya dinga sawa Yar China Albarka a zuciyarsa a fili yace to yanzu me kike so?......kafin ya rufe Baki tace ci na,Ido Mashkoor ya zaro yanda take kunyarsa yace me? ta sake furtawa tana kallonsa da idanunta farare tas Amma sun canja sun koma ja,Idan kika ji zafi fa?bazan ji ba wallahi ta kamo hannayensa tare da dora su a Kirjinta ta Shiga kissing Dinsa a Baki kamar mayya,Yace muje bedroom,no muyi a Nan Dan Allah,Yau Mashkoor yaga love, gashi bata gajiya ko kadan duk bala'in gwarzontakarsa sai da ta so kure shi,Ya Dade Yana Mata tace Baby ko ka kawo anjima zaka Kara min, Mashkoor yace Alhmdllh Ni ai Haka nake so Muna hutawa muci abinci a sake ta Yi ba ruwana,Nafeesat Tace ae,yace to yanzu bakya Jin zafin? tace Babu zafi wallahi ko Daya sai dadi,ka daina fita yawo kaji kullum Zan na yarda, Mashkoor ya dinga dariyar Jin dadi,yace kutmar duma du yau na samu yanci.sai da ta gamsu sannan suka Yi wanka tare da sake cin abinci sai bacci me Dadi ya kwashe su, Mashkoor harda cewa idan kika ji kyaram cikin bacci ki tasheni na shige ciki tace to.

Sai da Asuba bayan sunyi Sallah Suka koma sabon harka,sai da safe Nafeesat ta samu maganin ya sake ta,Amma Bata ji zafi ba Kuma tayi Enjoying matuka,ranar yini tayi tana tunawa sai tayi ta dariya tana murmushi, Mashkoor Yana kallonta shi Dariya ma take bashi,Yau ga kalaman soyayya Mashkoor yini yayi Yana Jin sababbin kalmomi wajen Nafeesat har da yanke Masa farce,yau komai da kanta take masa ai Kuwa Yana ji Ahmad ya kirashi Wai yaje Office ya kwaso wasu takardu yace wallahi bazai je ba idan an isa a sallame shi daga aiki,Dariya Ahmad yayi shine fa ya kamata yaje Office din Amma sabo da Aamna tana jikinsa suna soyewa yace bazai je ba Bari ya tura Mashkoor,to Mashkoor ma yaki zuwa,Aamna Tace kace Jibson yaje Wannan Dan Iskan ne zai je gwara ma Tawaga ko Brown,Bash ma ba zuwa zaiyi ba,Tawaga ya Kira yaji muryar Yar China tana Yayana kazo ka taje min gashin ya bushe,Ahmad Yana ji ya fuske yace Tawaga Office fa zaka je ka ebo min takardun Nan Dana ajiye a saman Table,Tawaga yace kash...okay Bari na lallabata sai na je,Ahmad yace zanci Uwarku wallahi ya Kuna Aiki a karkashi na ban Isa na da kowa Aiki ba Haka ake ma'aikatan? Shi yasa gwara ka dauki bare Aiki Dan Kun San bazan iya korarku ba ko,Tawaga yace to bazanje ba sai kazo ka Jani Dan Iska Kawai ya kashe wayarsa,Aamna tana ta dariya tace ka hakura Kawai kaje da kanka,Yan iskan Yara ne sun rainani cewar Ahmad.

Sai wurin Magriba suka je gaida Baban Brown sabo da Yana Fushi da Brown,Abba da kyar ya amsa gaisuwarsu yace bana bukatar girmamawarku tunda Baku ji kunyar hada neman aure Dani ba,da girmana kuke gani da Bai kamata idan kuka ji naje gun wata ba kuje,sai da kuka Gama ci min mutunci lokacin da kuka kwance min zani a kasuwa yanzu kuce zaku dawo ku daura min,me zaku Gaya min,Abba ya kalli Jibbonsa yaga yanda jibbon yayi kyau ya Kara kiba yayi wani Fresh haushi ya Kama Abba yace a ransa da yanzu nine na canja haka Amma jiba fatata ko yaushe cikin shan ruwan gishiri Da suga nake sabo Yar fatata ta rage yaushi,a fili yace

ku tashi ku barmin gida bana Fushi da ku tunda Kun rigada kun Gama Dani kuje Allah bada zaman lafiya wani girmamani Kuma bana bukata ku rike abinku,Tawaga yace Abba sai da sa albarkarku zamu ci gaba a rayuwa,da Masifa yace da kun San da Haka kuka je inda nake zuwa bakin kinibabbe kaima ai naje wajen taka Neman aure tun a mota na hangoku a can Kun tare ko Ina Kun kankane na juya salin alin ba tare da Kun ganni ba kuje ku karata Yan iskan yara.

Suna ta boye dariyarsu Suka ajiye Masa kudi yace an gode kuje Allah bada zaman lafiya tattabaru sarakan Aure ko Shedan ya ganku Haka sai Kun firgita shi,Dariya sukayi Suka Shiga motocinsu har biyu Suka tafi.

Nafeesat Kuwa da Yamma taje har wajen Yar China a can ya Iske su Aamna da Hafsat suna hira,tana shiga ta antayawa Yar China ashar,Dariya Yar China tayi,Aamna tace lafiya? Nafeesat tace wallahi in fada muku Yarinyar Nan ta bani maganin Wai na daina Jin zafin XXX na Sha Ashe maganin sha'awa ta bani,Hafsat Tace Yaya kika Kare? Hmm ke dai bari,Yar China tana Dariya tace tsakani da Allah kinji dadinsa ko Baki ji ba?Nafeesat tace zuwa nayi ki Kara min ma Zan na Sha kadan kadan ba yanda kika bani Overdose ba.

Aamna tana ji tace ai Ni irinsa nake nema Yana Ina ku San min,Yar China ta dakko wani galon Guda na hadin zumar ta musamman,Aamna anji harka ta rude a Ina ake hadawa na bada kudi na? Yar China tace Yaya Salamatu ce ku kawo kudi a hado muku dubu goma goma,Aamna da sauri tace ki karbo Mana accnt number dinta har wasu Kalar ma Ayo Mana,My King ko Nawa ne nasan zai bani,Hafsat ta Mike tsam ta dakko cup a kitchen ku bani dama Bash ba Hakuri ne da shi ba Nima baya daga min kafa ku bani Nima,Suna Haka sai ga Sameera da Humaira sunzo,Ai Sameera mayya tace Kan bala'i ai na shanye tawa irin wannan dama Ina ta Nema ki bani na kurba,Humaira tace Mene ne bayin Allah? Aamna tace kayan harka ne Wanda ke sa me gida Hawaye,Yar China harda shewa tace har kuka ma Wiwi zai Miki,Humaira Tace ba ruwana Haka Kawai ma ya Muka Kare da shi bare na Kara da wannan Ina da wasu abubuwan ma so nake sai na Saba sai na fara,Yar China tace ke dalla kauyis Kamar bada Lagos kika fito ba yanda kike Yar balarabiyar Nan ai ya kamata Brown yasan can ciki dinma Balarabe ne idan Zaki daina zancen zafi da wani takura ki daina mu mun watsar Gazal ake sa Mana kullum,Suka dinga kyalkyala dariya,Yar China ta Zama fetsararriya bayan itace karama kuma.

Humaira tana Dariya Tace Gazal? Tozali ba yarinya zauna mu ba ruwanmu shi ake gwaguda Mana kullum kin zauna can wata katuwar tana wajen
tana siyen gishirin Mata tana yafawa ciki ke a barki a Nan,to mazan yanzu Zina ba komai bace a wajensu Allah kiyaye idan Zaki Sha ki sha,Aamna tace wallahi ai mu Bama daga kafa Bama Free,Nafeesat Tace ku bani Dan Allah tsarin Nan yayi Yar China Uwar Mata,Hafsat ta bulbulawa cikinta,Aamna Robar ruwa ta dakko aka zuba Mata sannan ta Sha wani,Haka su Nafeesat ma aka barwa Yar China ragowar nata itama ta Sha kadan tace kadan Zan Sha sabo da tun safe na Sha wani,ta mayar da abinta,suna hirarsu Aamna dake dama Yaya bare anyi Kari tace Kai na tafi Good Night yanzu zai dawo,Yar China Tace za dai kije kwada Masa Kira a waya ya dawo,Nafeesat tace Nima nayi Nan,Daya Bayan daya suka tafi kowacce.

Baba kuwa ya Canjawa Mama sabon suna daga Aishatu ta koma Ya Hajja,Mama tayi ta Jin kunya Amma Baba yace Ina ya dakko darasi wajen Rahilu,Mama Tace kaji kunya wallahi,Yana

daga kwance yace kalle Ni Nan nafi Rahilu komai Amma Rahilu yanda naji Yana Kiran Hubby abin ya firgitani Dole Nima na dauki mataki Ina laifi ma dana Yi Kara nace Ya Hajja karki jawo wallahi ma koma sweetner ma,Mama tayi Mukus.

Siyama tunda aka kaita Hashim Bai wani Bari sai ta so shi ba ko wani abu ba jira yake karbar Hakkinsa kullum,Siyama ba yanda ta iya gashi Yana kyautata Mata sai abinda take so Bata da bakin Yi Masa musu akan komai,Jin Dadi ba Wanda baya Bata sabo da duk Samunsa gida yake kawowa mutum ne me zuciya, da ka samu me kudi da mota marar zuciyar kyautatawa Iyali gwara Dan dako me zuciya.
Ga Aiki tuni Ahmad ya dauke shi bashi da matsala shi kam,Ita kanta Siyama sai ya fara birgeta,Waya ta Kira Aamna suna waya,Aamna Tace ya me gidan fatan ba a bashi wahala? Dan Allah karki amfani da kiyayya ki cutar da shi,Dariya Siyama tayi tace wa? Ai in fada Miki Ni wallahi ya fara birgeni,Ni yanzu masifar birgeni yakeyi in fada Miki ga tsafta ga iya daukan wanka,ke in fada Miki ga iya love har mamaki nake yanda ya iya Romancing ko bature Albarka mutuniya ta,Aamna tana dariya tace kice yafi Faisal? Siyama tace Faisal din banza Ni sai yanzu Naga ma Ashe yafi Faisal kyau da komai wlh kawai kudi Faisal ya fishi Kuma Inshaallah shima kwanan Nan zamu Faso gari tunda ya fara Aiki da Ahmad,Baki gani ba sai abinda nake so abinci yanda me kudi yake cin me kyau Haka Nima komai available,sunansa ma me Dadi Hashim Dan Allah yaushe Zaki hada shi da sunan Faisal,Wai Faisal Abu ba Dadi Haka Kalar karya feso karya shine Faisal,Aamna tace iyye Dan Adam kenan kayan Allah,Kawai Hashim ya tafi Dake? Siyama tace Ni yanzu ma na gano ba birgeni yake Yi ba sonsa nakeyi,Lokacin da suke Wayar Hashim ya shigo da danyun kajinsa a Leda za a zuba farfesu,farin ciki ya kamashi yaji da kunnensa tana sonsa shi Kam ya Gama dacewa,tun Siyama tana jaririya yake kaunarta,ba irin wulakancin da Bai Sha ba a wajenta sabo da baida kudi Amma gashi yanzu cikin sauki,Godiya yayiwa Allah Dan murna ji yake kamar ya tashi sama,Sabo da murna fita ya sakeyi ya sake siyo kifi da wasu tarin abin makulashe.
Siyama yau taga tattali da soyayya wajen Hashim,sai ta Kuma Jin sabon sonsa.

Lokaci na ja cike da kwanciyar hankali da kaunar juna cikin Aamna ya shiga wata Biyar har ya fito Ana gani,Bata wani laulayi me wahala,a satin Kuma Humaira ta fara zazzabi da Amai yaki karewa,Ana zuwa Asibiti akace ciki ne da ita har na wata biyu,Brown harda rawa a Palo a Gaban su Tawaga ya fara Break dance suna ta dariya,lokacin Kuma Nafeesat canjin da taji a jikinta tana zuwa hospital wurin aikinta Tace a Mata test sai gashi tana da ciki na wata daya sai Result ta kawowa Mashkoor,Yar China tana ji tace Allah ya tsare watakil muma Muna hanya badan Allah yasa last month nayi period ba da Nima asibiti Zan tafi a gwada Ni Naga abin Kamar gasa ne ai muma ana Mana aikin ba finmu rakashewa aka Yi ba sai dai a nuna Mana shekaru,Hafsat tafi kowa son ta samu ciki tana son Yara a rayuwarta Amma itama Shuru Tace to Muna jiran tsammani,Sameera Kuwa da Jibson dama su ko a jikinsu idan sun samu suna maraba.

Kwanci tashi sai da cikin Aamna ya shiga wata Shida sannan Sameera ta samu cikinta,Jibson harda yanga zaiyi da shima,Hafsat ma ta samu ciki,Yar China ta damu kanta Bata San tana da cikin ba ma garin jarabar wasanninta ta tafi part din Aamna ta hau lilo tana ta shillo

a kai daga lokacin Mararta ta daure ta Shiga kwala Ihu ba ji ba gani,Aamna ta fito,Allah yasa sun Iya mota mazajensu sun koya musu Yar China ce Kawai Tawaga yaki koya Mata sabo wasan tsiyarta Kar ta kashe kanta da mota shi yasa duk inda zata shi ke kaita ko Driver, Aamna ce ta fito ta hango Yar China a kasa ta zube Jini malalala Fitowa ta kasanta,a gigice ta Kira Nafeesat Suka saka ta a mota sai asibiti suna kaita aka Kira Tawaga Suka sanar musu suna Office ma,Tawaga ya gigice yace me ya sameta? Aamna Tace ka kwantar da hankalinka Bari tayi,yace Ni ba barin ba ya lafiyarta? Tana Nan ma an canja Mana dakin Hutu har mun gyarata bacci ma takeyi, Kasa tuka motar yayi sai Jibson ne ya dakko shi Suka wuce Asibitin Basu Dade da shiga ba Yar China ta farka da kuka,sai ihun kuka takeyi an zaci ma wani ciwo takeji aka yo kanta,Ana tambaya lafiya? Yar China ta sake rushewa da kuka tana shafa cikinta ta kalli Tawaga Wanda ya rike Daya Hannunta Tace ance Wai Bari nayi? to menene tunda lafiya kike ai Yaron yaje zamu samu wani,yar China ta sake rushewa da kuka wallahi bazan yarda ba sai an bi min hakki na sakakin likitocin Asibitin Nan ne,sune Suka jawo cikina ya zube,Wa yace ki hau lilo da shegen wasanki cewar Iyalle da ta shigo yanzu hankali a tashe,Yar China tace sai an biyani cikina bazan yafe ba,duk wahalar da Muka Sha ai ban San Ina da ciki ba da ace na sani yaushe Zan hau lilo,Wata Likita Tace dalla malama rufe Mana Baki kin cika Mana asibiti da kuka mijinki gashi Nan Zaki sake samun wani.

Bed din Yar China ta doka da karfi tana burbuwa ta nuna Likita da yatsa Uwarki ce zata min Cikin shegiya tsinanniya duk ba kune kuka jawo ba da kunyi aikinku da kyau cikin zai zube ne Shegu Yan Practical duk irinku ake zubawa kuna kashe Yaran mutane,Tawaga ta kalla tace sai an biyani Diyyar dana da aka kashe min a Asibitin nan, Iyalle da karfi Tace Diyyaaa? Yar China Tace ae,Likita tayi Dariya tace to madam ki Gama zamuzo muyi Miki wankin ciki,Yar China ta saki sabon kuka tana za a zura karafa a cikina so suke su karasa min mahaifata,yahudawa ne America ce ta dauki nauyinsu sabo da a rage yawanmu a duniya,yahudawa ne suke biyansu ta karkashin kasa,Duk Wanda yaji haukar Yar China sai yayi Dariya,Yar China tace ko America ce ta Basu kwangila ko kasar Denmark matsiyata sune basa kaunar musulunci kasar Denmark sune ma.

Barin tayin Dan aka bawa Tawaga a kwali Yar China tace ku Bude min Naga gudan jiinina tana kuka sosai Iyalle ta karba ta Bude Mata Yar China ta bangale Baki tana murmushi Yaron da ko halitta ba a fara Masa ba Amma take zuba Uban murmushi tace Allah sarki zamu hadu da Kai a makarantar Annabi Ibrahim,aka kyalkyale da dariya,Yar China ko kulasu batayi ba tayin dan da kusan ma jini ne shi take kallo Tace ga jini na can na Gane shi ga bangaren Tawagana can Suka hadu a broader, da tuni sunanka Ahmad sunan Babana za a mayar idan mace ce Kuma Salma sunan Babata Amma Ina,Iyalle ce zata rufe kwalin Yar China ta dage sai ta sake ganin Danta aka Bude Mata Karo na biyu tace Babanka ya Sha wahala kaji Amma mun yafe maka sai munzo ka jiramu a madakata kaji Allah yayi maka Albarka sai Watarana Amma kayi Hakuri zaka Dade baka ga munzo darul salamu ba sabo da Inshaallah baza mutu da wuri ba sai mun Haifo kannenka Suma sun Haihu yayan kannenka sun Haihu sannan ka ganmu,kayi gaggawa Dana, da ace ka zauna ai da kaga kaun....Yar China ta karasa da kuka Tace First Night dinmu nake tunawa Iyalle ke Baki San turanci ba First Night Iyalle shike nan,Allah sai na Suma Yar China tayi luuuu akan bed Wai ta Suma,Dariya aka dinga Yi har Tawagan nata Haka

ya tafi da tayin,Yar China tana cewa karku cike Masa Ido da kasar kabari Kai Jibson wallahi karka sake ka taba min da baka Yi Addua ba nasan halinka.

Baki Iyalle ta make Mata,ai Kuwa Yar China ta Sha wahala da aka Mata wankin ciki duk bakinta sai data daina magana,Tawaga hankalinsa ya tashi yasan duk abinda ya Hana Yar Chinansa magana ba karami bane,Sai kuka Kawai takeyi da kyar tace Dan Allah ka barni Iyalle ta tafi dani wajenta nayi ko sati biyu ne Dan Allah? Tawaga harda wani kwalla yace na yarda My love zanci gaba da Zama a Gwauro kafin ki dawo,Yar China da slow tace ai a dakin Iyallen ma Sai ka kwana Watarana,Iyalle Tace inji Ubanwa wallahi Baku Isa ba sai na fasa tafiya dake,Tawaga yace Wasa fa take Miki,Aamna tace da an barta ma Sai mu kula da ita,Yar China tana Jin jiki tace me kuka sani na Haihuwa Kuna Yara me zaku iya gwara tsohon Hannu,Iyalle Tace Ni Zan gyara abata,washe gari Yar China taji sauki aka sallamesu,Tawaga ya Hado mata Kaya ya sauke su a gidan Iyalle gidan kanin Iyalle kenan a dakin Iyalle.

AsmaBaffa.
10/29/21, 7:46 PM - Buhainat: 🌵🌵 DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

NA KUDI NE

Duniya ta Aamna is dedicated to Garba Butalawa family.

Official

By
AsmaBaffa

Page naku ne

DUNIYATA FANS

Tayi tunanin zata iya Zama ba tare da ta damu ba amma ganin Tawaga ya tafi duk sai taji ba Dadi Dan ma Allah yasa gidan Kanin Iyalle da Dan kyau ko Ina yasha Siminti bandakin Iya harda tiles a toilet din Kalar na zamani,shima Toilet din matarsa Haka yake,Ruwan Zafi Iyalle ta tafasa Cikin Yar China ya duri ruwa ganin ruwa me yawan masifa gashi na zafi ya tafasa,Iyalle ta tasa Yar China a gaba sai da ta Mata wanka da towel ta gasata sosai ta Sha azaba sosai harda kuka,Allah yasa Tawaga ya kawo Nama iri iri da kayan Karin jini ga magunguna,Fruits ba Nema ba,maltina da su Madara available, Sha Kawai takeyi tana ci ba ruwanta,Ko kwana Uku Bata Yi ba ta wani murmure har kiba tayi da kyau,Iyalle tuwon shinkafa Miyar Alayyahu ta Sha man shanu da kifi ta girkawa Yar China da kanta,Lokacin Yar China tana wanka Tawaga ya shigo da ledoji,Iyalle tana Masa tsiya baya gajiya,Ya zauna a Kan gadon Iyalle,Iyalle tace ga abincinta Nan a flask Bari ni na leka gidan gaisuwa,a dawo lafiya yace ta tafi,Mintuna kadan Yar China ta fito daure da guntun towel ga karami Kuma tana goge jikinta,Tawaga ya bita da kallo,ta Masa kyau sosai tayi wani kiba da haske,a gefensa ta zauna tare da kwantar da kanta a kafadarsa tace Sannu da Zuwa My Heart,Murmushi ya saki yace Dole kice Haka ai tunda kin gudo kin barni,Dariya tayi Tace ai Zan dawo Kamar yau ne,Abincinta ya nuna Mata Iyalle Tace ki cinye,Murmushi tayi tare da mikewa ta shafa lotion dinta me shegen kamshi ta dakko wata Yar bakar Vest me kyau ta sa Skert din atamfa ta sa bra tare da vest din tayi kyau,gashinta ta gyara fes sannan ta bi jikinta da turaruka masu kamshi ta shafa powder da lipgloss tayi kyau matuka.

Tawaga sai kallon Kirjinta yakeyi yanda Suka cicciko,spoon ta dakko Guda biyu ta bude Tuwon na Danyar shinkafa Tace Busmillah,tare sukaci suka koshi,ya Bata ledojin Nan ma kayan ciye ciyene ga Naman kaza gasashiyar,Yar China tace Ina Jin dadina wlh,kwanciya tayi a jikinsa sai Kuma ta fara kuka,Mene ne haka? Zaki fara ko? Bata Rai yayi yace daga min jiki na tafi gida abina naga Alama daina zuwar Miki zanyi,tunda kika Yi Bari Dan ma ba'a sanshi ba babu Wanda ya Shaku da shi kullum nazo sai kin min kuka ki tashi to mu koma gida sai nayi miki wani cikin,Yar China tana goge hawayenta tace Allah jaririn ne akwai shiga Rai,wannan tayin jinin shine abin Shiga Rai? Yar China tace ae Ni Ina son abina jinin kalarsa me kyau Kamar ruwan zuma,Dariya ta kwacewa Tawaga,Tace Kuma ma ai Nonuwa ne suke ciwo duk sun cicciko wallahi sun min nauyi,wannan ai me sauki ne Indai ruwan zai fita sai na shanye,Yar China ta makale kafada,yace mu gani to tayi masa Shuru,Hannu yasa tare da janye rigar sama.

Wayo ya Mata tare da Furta Wai Wai wannan ai Massage suke bukata,Yana tattabawa yace Massage suke bukata,da sauri tace Allah? Yace ae mana, ai ban sani ba da tuni idan munje wanka zance Iyalle ta dinga danne su da Towel cewar Yar China,da sauri Tawaga yace no Miji ne ya kamata yayi ai Hannu na tafi na Iyalle girma da laushi idan na Miki yau ma gobe Zaki ga sunyi sauki,sai na dawo gobe na sake Miki Haka dai kamar sati Daya yanda kafin ki dawo gidana kin warke,jinin ya dauke ne? Ya tambayi Yar China Yana son Yi Mata wayo,Tace a'a

Saura kadan Nan da kwana Uku ma Iyalle tace zai dauke,hakan yayi kyau cewar Tawaga Dadi ya Gama kamashi,cike da nishadi ya shiga massaging Dukiyar fulaninta tana Jin Dadi tana lumshe ido,Yace da Dadi ne? Kulle Kofa kasa key Kar wani ya shigo abin Nan na Yi ne cewar Yar China,Ba musu ya dannawa Kofar Iyalle key ya dawo,Yar China da Yatsanta ta daura a saman lips dinta tace nan,ya Gane ya shiga tsotsar lips dinta,Yar China ta sarkalo da hannayenta wuyansa suka kwanta a saman gadon Iyalle Yana luguiguita ta yanda yaga dama,Yar China ta shiga sarrafa shi itama da kanta yanda zai samu ya rage zafi ba tare da sai anyi babbar harka ba,Zaucewa sukayi ya furta matse min cinya Honey,Duk ba Kaya a jikinsu Yar China ce Kawai me pant,ai Kuwa dai da Cinyoyi a samu gamsuwa a nutse ba tare da sun batawa Iyalle komai ba,Yar China harda dabara ta sa tissue a jiki ya fitar ta wani saka a bakar Leda ta daure,sai da suka daidata kansu tsaf kamar ba abinda ya faru ta Bude kofar ta tarkata na zubawa a shara ta Kai Dust bin ta dawo.

Suna Shan Fruits Iyalle ta dawo Bata Gane komai ba sai da Tawaga ya Mike zai tafi taga jikin farar shaddarsa duk jambaki da powder,ga lips dinsa yayi red shima sabo da jambakin Yar China Daya Sha,Fuskewa Iyalle tayi sai da Yar China ta raka shi har mota ta dawo,Iyalle tace Nan da sati Daya Zaki tafi baza kiyi min sati har biyu ko Uku ba,Sabo da me ? Sabo da na gaji da sintirin mijinki,Yar China Tace to shike Nan Ni gwara ma na tafi dama na gaji gida duk zafi ba AC ba komai,can abinda Naga dama nake Yi Amma Nan duk kinbi kin takurani,Mijina Yana can Yana ta kamshi ke Kuwa jikinki duk kauri,dama Ni manage nakeyi da ke Ina kwanciya a bayanki wani fayauuuu....ba hug ba komai da Mijina ne fa sai nayi shagwaba ta,Mufici Iyalle ta kwadawa Yar China a baya tana Yar banza fitsararriya.

Kamar yanda Iyalle ta furta Yar China tana yin sati Tawaga yazo Suka tattara tare da komawa gidansu tana ta murna.

Rayuwa na tafiya Sannu Sannu sai lokacin cikin Aamna ya cika cif dai dai edd dinta Amma Bata Haihu ba,tayi nauyi da yawa Dole sai masu Aiki Dattijai masu kwari Guda biyu aka kawowa Aamna suna tayata aikin gida,Yayin da Suma cikin su Sameera duk ya tsufa Banda Yar China babu ciki.

Bayan Sati daya da cikar edd din Aamna cikin dare suna kwance ta kasa kwanciya,nakuda ta fara,kasan bed ta koma ta zauna tana daurewa,tun tana dannewa har ta kasa ta bigi kafar Ahmad dake banci Bai San me ake ciki ba,a hankali ya Bude Idonsa tace ka tashi Dan Allah mu tafi asibiti wallahi Ina Jin Haihuwa zanyi washhhh Allah marata wayyo gadon bayana,Ahmad Yana ta nuku nukun tashi ta fashe da kuka tana buga jikin bed,ba shiri ya dire a kasa da kayan baccinsa ya dakko Mata wani zani ta daura a saman kayan baccin ya kifa Mata Hijab tare da dakko kayan data nuna Masa ta shirya a cikin wata jaka duk na Haihuwa ne ta tanaji komai abinta,Dauka yayi tace dakko har Bowl din jaririn,Ahmad ya dakko ya sauka da gudu gudu sauri sauri ya saka kayan a mota ya dawo ya dauke ta ya kwantar da ita a bayan Mota,Nafeesat ya Kira da Mashkoor,Yar China ta saman window dinsu ta leko Jin maganganu ta tashi Tawaganta Tace ga Aamna can tana fama Allah ya tsare mugun ji  yau zata San uwarta ta kawo ta duniya tashi mu tafi na koyi darasi kafin nawa,Tawaga yace ke da kika Yi Bari,ance wani barin ma ai yafi Haihuwa azaba Kuma idan kunje Kun tarar Mata a Kai me zakuyi mata muyi Mata Addua Kawai,Sameera ce ta fito Dake itama ta taba Yi aka tafi da ita,kafin ma su karasa Hospital an

sanarwa Mama tuni Mashkoor a daren 1am yaje ya dakko Mama Suka taho Asibitin.

Aamna Kuwa tana ta daurewa bata kuka Shuru kawai Bata magana da Alama tana Shan wahala,private ne Single room ita Daya aka basu,Bayan an duba Suka ce Haihuwa ce tazo gaf,Ahmad suna waje hankalinsa a tashe Kawai tagumi ya buga,Mama da Su Sameera suna ciki tare da Likitoci,taimakawa Aamna sukeyi har aka samu Aamna ta santalo katon danta namiji Kamar yanda suka gani a scanning,tana Haihuwa ta suma sai da kyar Aamna ta farfado ta Sha wahala Amma tayi Hakuri tayi juriya matuka,Jaririn Nafeesat ta goge da man Zaitoon dana Habb fes a towel aka nadeshi,Yaron girmansa ya Isa Kamar ba daga jikinta ya fito ba,Sameera ce ta kaiwa Ahmad jaririn,Bai ma San ta Haihu ba suna Zaune da Mashkoor hankali a tashe sai jariri Suka gani, Ahmad ko jaririn Bai karba ba yace ya My world take? Ras take Ahmdllh Bata da wata matsala yanzu ma gyarata akeyi,Sai lokacin Ahmad ya saki ransa tare da godiya ga Allah Yana me karbar Jaririn,shagala yayi da Kallonsa Baki Nan a Bude, Mashkoor yace to Malam Addua fa zaka Masa,Sai lokacin ya shiga Masa Addua a kunne sannan Mashkoor ma ya karba tare da Yi Masa,sai ga su Tawaga Suma a daren sunzo sun Iske an Haihu ma,Jibson ya karbe Jariri Yana cewa mun zama Iyaye yau,Bash da Brown ma Suka karba suna ta Masa Addua,sai Tawaga shima har da cewa bari na Masa shillo ya daga karmar zai shillashi sama,Ahmad da bala'i ya dakawa Tawaga Tsawa zai kwace dansa Yana masifa aikin banza so kake ka hallaka min yaro,Dariya Suka dinga Masa gaba daya,sanadin Haka ya karbe dansa ya Hana Tawaga fafur.

Humaira sai Waya take bugawa taji ko ta Haihu aka ce Haihu lafiya,Haka Hafsat da Yar China Suka ji a waya,sai bayan Aamna ma tayi wanka ta canja Kaya aka canja Mata dakin hutu,komai an gyara Neat ba matsala sannan aka bada dama su Ahmad Suka shiga,Tana kwance ta lumshe Ido tana hutawa,Ahmad kamar zai shige cikinta duk yabi ya kankane ta,Sannu su Tawaga suka Mata da Barka sannan kowa yayi waje ya barta da Ahmad dinta da jaririnsu.

Aamna ta kalle shi Suka hada Ido tare da sakarwa juna murmushin kauna,Yace me Kama Dani aka Haifo,Aamna tace Haka naji su Sameera suna fada,Ahmad ya nuna Mata Yaron ta karba ta Masa Addua itama sannan tace ka duba jakar can akwai Ribbom Dina ka Kama min gashin Nan ya dameni,Ahmad ya ajiye jaririn a gefenta tare da dakko Ribbon din ya daure Mata gashin sosai yanda bazai dameta ba,yunwa nake ji ta furta,Yanzu Jibson zai kawo abinda Zaki ci ki Dan Kara Hakuri ya Furta Yana shafa fuskar jaririn,Aamna tana satar Kallonsa tace ai fuskata zaka shafa ba ta Jariri ba idan da a baya ne kafin na Haihu ai fuskata kake shafawa,Dariya ta bawa Ahmad ma shi,ba a Dade ba Jibson ya dawo da ledoji Naman kaza da fruits sai gida da yaje ya taho Mata da tea a flask da komai na amfani,yace Mama tace na taho Miki da me Dan nauyi gashi Nan Humaira ce Kawai Allah yasa tayi faten doya ya rage kiyi manage kafin safiya,Aamna tace hakan ma yayi,Nafeesat ce ta hada Mata tea me kauri da kaza taci ta koshi har faten doyar.

Bacci ne ya kwashe Aamna,su Ahmad sai murna da bige bigen waya duk sun cika Asibitin da surutunsu,Su Yar China Kuwa suna tare da Humaira a gidan Hafsa Suma sun hadu suna

zuba Hira,Yar China tace Yau Aamna karshen Sirri ya Kare yau likitoci sunga Hq,Basu da mutunci matan Nan Haka suke zura Masa Ido,Dole su makance da wuri cewar Hafsat,Humaira Tace to yanzu ma ba mu zo Haihuwa ba Ana ta duba mu Ina ga Haihuwa,Yar China tace ai ku shirya ba Wani sirri idan da duhu ma wata shegiyar touch suke sawa me haske,Dan ma matane Amma ai da kunya,lokacin Dana Yi Bari Ina dawowa nace to Tawaga sai dai kayi hakuri dakinka dai yanzu ba sirri ,Humaira suka Kama dariyar Yar China,Yar China Tace shegiya ai Kuwa likitar ta kiyaya wlh taga tsafta iya tsafta da kamshi sai da ta min jinjina Tace da wasu matan ne Haka dagajaja ake gani,Humaira tana Dariya Tace a gidan Ubanwa ta ganshi fes lokacin kina Bleeding,Ke banza ce yanzu fa Dana warke ai mun koma Hospital ta dubani taga ko Mai normal,Humaira tace sai kace wacce ta haihu,Yar China tace su Ina ruwansu Abu ba abu ba sai suce sai sun duba ya na iya,Hafsat tace ni wlh Nima abin ya isheni ayi ta sa ma yatsu.

A daren Mazan Suka dawo gida har Ahmad,Yar China Suka koma part dinsu,Ahmad sabo da Murna da kyar yayi bacci,Nafeesat aka Bari sabo da ita Nurse ce sai Mama,Itama Sameera mayenta ya taho da abarsa gida,a daren Ahmad ya sanarwa su Mummy suna ta murna,Washe gari jikin Aamna yayi kwari ka rantse ba ita ta Haihu ba,da wuri Yar China,Hafsat da Humaira Suka zo da kayan Kari,Yar China ta kinkimi Jariri tana wayyo Allah ji Dan Allah yaro zukeke me Kama da ubansa,Ina ma Nawa ne mashaallah,Kai Aamna kinyi Aiki yanzu daga jikinki ya fito? Gaskiya kin Sha wahala,Aamna tana dariya tace wlh abin ba a cewa komai,ai naso jiya nazo ko darasi na dauka Amma Yaya Tawaga ya hanani,Aamna tace akwai azaba wallahi da ikon Allah bazan sake ba Allah ya tsayar min iya Nan,Karya ma kike fada wlh sai kin Karo Ina laifin ma biyar ko hudu,Humaira Tace ai fa Amma Daya jal idan aka Miki kishiya ta wuce ki fa? Aamna Tace ga fili Nan Indai wannan abar ce taje ayi ta sa Mata Ana Mata ciki Ni na hakura,Na rantse da Allah nayi zaton a kabari Zan farka na ganni,tunda nake ban taba Jin azaba ko rabi rabin wannan ba,kukan ma kasa Yi nayi na koma kurma Kawai.

Yar China harda cewa Ahayye taji uwar Bari,Ni kaina Kinga dai Bari ne Dan Blood ne Amma naji a jikina,Kai Ina tausaya Mana Mata,Mama da shigowar ta kenan tana ta kallon Yar China Kamar Tv Tace wannan yarinya da jarabar iya zance take sai kace Babbar mace ko dai tsohuwa ce ta rike ki? Yar China tace a Hannun Kakata na girma,Yanzu naji zance cewar Mama.

Siyama ma da duk wasu abokan arzuka Haka Suka dinga sintiri,Baba yazo shima ya dauki Jariri Yana Masa Addua karshe yace Allah yasa karka gado taurin Kan Mamanka,sannan karka dakko rashin kunyar Babanka kaji,yaro Babanka har satar min kayan kallo yayi Akan son Mamanka,maza ka girma idan Ina da Rai ka biyani startime Dita da radio,kakanka Rahilu Haka Muka je Sudan Muka dawo ko kyallen Handkerchief Bai Bamu ba sai da kudinmu Muka Yi tsaraba,Yana can Yara da jikoki zasu hallaka shi Yana ta karmashewa,kaf kamfanonuwan duniya babu wando Size dinsa,idan ka girma ka kalli Rahilu sai kayi Takaicin Fitowa a tsatsonsa,ga tsayi Kamar bishiyar turare wani zamarke da shi,Mama ce ta kwace jaririn tana cewa Kai dama ai baka son mutum idan ba kudi zai baka ba,yanzu da Rahilu zai maka kyauta me tsoka cewa zaka Yi yafi kowa kyau,Baba yace to ayi min kyautar a gani Mana dama yace zaizo idan Aamna ta Haihu yau Zan fada Masa a waya sabo da dama ya min Alkawarin wani

takalmin fata da yace zai kawo min Yana da kwari sai nayi shekara goma Ina sawa ba tare da ya tsinke ba Rahilu duk Harkar tsumulmula ya kware a cikinta.

Aamna Tace gaskiya Baba ka daina,In daina Ubanki? Sanda na Sha wahalar rike ki ya taimaka min da kwandala ai wlh Rahilu Matukar Bai min kyauta ba ya shiga uku,har yanzu Bai iya Yi min godiya ba a matsayina Wanda na rike Masa yarsa ta girma na Bata Ilimi na Aurar da ita,shi ba ruwansa ko a jikinsa ai kin gani da idonki ko yayi min godiya? Aamna tace a'a amma ai Dan Allah kayi,to bazan daina ba idan kinyi zuciya kisa ya gode min Sannan ya girmamani ta hanyar Yi min kyauta,ai Ni babbar girmamawa ayi min kyauta,Mama Tace a Haka zaka Kare,Suna Haka Ahmad suka shigo ya Sha wani shegen wanka cikin kana Nan Kaya Yana kamshi,Baba yace Iyye kaga Wanda basa tsufa Kamar ba shi ya Haihu ba,kaga Danka fa Kato Amma bakwa saduda da daukan wanka wannan kamshi Haka kamar turaren dakin Ka'aba,su Ahmad suka dinga dariya,Baba yace ga Aski na banza Kun iya to dai Kun fara Haihuwa,Ahmad Yana dariya yace Baba ai wanka yanzu ne ma zamu fara,Kin shiga Uku Aamna Mata yanzu zasu fara sintiri a gidanki kuwa cewar Baba,Aka dinga dariya Aamna tace wlh Bai Isa ba gida Zan dawo,Baba Baki Bude yace gidan wa? Gidanka Mana,karya kikeyi Kai yaro idan tace zata hanaka aure kayi Mata shegen suka ka kirani a waya ka Kara min kukanta kana jibgarta Ina jiyo kukanta ta waya,Ahmad suna ta dariya da su Jibson,Yar China tace Baba kana ba damu wlh wa yake Yayin Kara aure yanzu ai tsohon yayi ne,Tawaga harda cewa wlh Ina zamu Kai Yara wannan ta Haihu wannan ma Haka,Baba Baki Bude yace sun shanye ku,ku daina Kiran kanku mazaje sam,Mata sun Gama da ku,a Haka kamar wasu mazajen kirki,Hafsat tace Baba kaima fa Daya ce jal,Gata can itace ta kankaneni ya nuna Mama da baki,Baba da abin Dariya Yana ta Basu Dariya ana Wasa da dariya ba ruwansa,Sai Yamma aka sallami Aamna,Mama Tace zasu tafi da ita Ahmad yace bazai yuwa ba,da kyar ya Amince zata Yi sati daya tal.

Kullum suna gidan Baba mazansu da matansu suna sintiri,Baba yace Jaraba akan Jariri daya tal samarin Nan da matansu sun hanani sakewa a gida,wannan suzo da Yamma wannan da Rana wannan da safe,kullum ba ranar banza,Tawaga harda zuwa Wai sai an bashi Jariri ya tafi da shi yawo a mota,Aamna ta hana,Kuma da sanin Ahmad Wai su a Dole sunyi da,akan sunan Jariri har wuri me tsada aka Kama,anan Suka shirya party Wanda yafi na aure tsaruwa da komai,Katon sa da raguna biyu aka yanka yaro yaci sunan Baba Hussain sabo da rike Aamna da yayi Ahmad yace Baba zai mayar,Baba ya dinga murna,jaririn Nan Yana ganin gata wajen Baba komai ya siyo yace na takwaransa ne, Aamna suna kiransa da Fu'ad,Zuhra an sa Babanta sai murna,Su Yar China ranar suna sun chashe da Kawayenta Wanda itama ta gayyata.

Bayan suna da kwana Uku Aamna dai tana gidan Baba Allah ya kawo Rahilu tare da matarsa Uwar gida da yaransa biyu mace Daya Namiji Daya,Tsaraba Rahilu yayiwa Jariri kaya masu tsada,Baba Kuwa Jallabiyya aka kawo Masa har kala biyar da takalma harda turaruka,matarsa Kuma ta Bawa Mama da Aamna dogayen riguna masu Kyawun gaske,Baba ai sai ya canja ka rantse Rahilu wani Dan Uwansa ne,Satin su Rahilu Daya Suma koma kasar su,Baba suna zaune da Aamna da Mama sai Siyama da Zuhra da Suka zo,Baba yace Rahilu kenan Ana can Allah sarki ai idan Rahilu yaso mutumin kirki ne Watarana,wannan karon ma Sai Naga yayi fes

da shi ya canja yayi kiba,ko dai Rahilu wasu kulli ya taka ne? Aamna da Mama suna ji su dai sun San babu abinda Rahilu ya canja Yana Nan yanda yake Amma sabo da yayiwa Baba kyauta harda yabonsa.

Baba harda cewa Indai mutum ba a Nigeria yake ba to Dole sai kaga canji Dole sai kaga mutum nutsatse da hankali,idan Dan Nigeria ne Marar hankali ya kalli gidana ai bazai bani kyauta har ta kudi ba,amma Rahilu Dake a kasar masu hankali yake bayan tsarabar Kaya ma da zai tafi har dollar Amurca ya bani,su dama wajejen yankin su Rahilu hankali ne da su,a nutse suke komai,ko wata kasar suka je zaka gansu daban,shi yasa Watarana nakan so mu hadu da shi Ina samun Karin Ilmi na zaman rayuwa da kula da Iyali,Mama ya kalla yace Ya Hajja ko ke Baki ga canji ba? Mama Baki ta tabe tace daga baka kyauta duk ka haukace,sai nasa Aamna taje dake kasar su Rahilu sannan Zaki waye,Naga Alama kina cikin duhu har yanzu,Baba Yana ta yabon Rahilu suna jinsa.

Satin Aamna Biyu Oga yazo ya tattara Suka koma gida,yabi ya hanata sakewa da bin kwakwafi Wai Kar ta fara Sallah Bai Sani ba,Aamna Tace yanzu Arba'in dinma baza ka Bari nayi ba? Kina fara Sallah Kuma ai kinyi Arba'in me Zan jira,Aamna tace to yaushe zamuje Hospital game da planning din? Ido Ahmad ya zaro yace Fu'ad Daya tal ai yayi kadan Ni yanzu nasan dadin Yara ki Karo min daya sai ki huta,Aamna ta fashe da kuka ta tuna wahalar data sha,Ahmad ya dage shi Kuma kome zata Yi sai ta Karo Masa wani Yaron suka dinga fada ba Wanda yake yiwa wani magana a junansu,Aamna da ta gaji wajen su Jibson ta Kai kararsa to bakin su daya abinka da abota ta Amana,Su Tawaga suka ce ya Bari Yaron yayi kwari idan ta yaye sai ta samu cikin wani,Ahmad yace ni Sam wlh ban yarda ba,a shekaruna ace yaro Daya Ni bana son Kara aure Allah ya gani Amma Ni yanzu Ina son Yara idan ta Haifa min ko biyu ko Uku sai tayi ta planning dinta Nima Ina son haka,Tawaga yace Nima Haka na tsara na gani Yara suna da Dadi Niima ne Amma ba irin yanda muke Haihuwa a kasar hausa ba barkatai ba a iya daukan nauyin Yara,ba Ilimi,ba ci ba Sha Ana ta zubar da Yara suna dawowa su addabi duniya,gwara dai kadan sabo da halin rayuwa ma,Aamna dai gani tayi yaki yarda tayi duk abinda zata iya Amma Bata samu Nasara ba.

Shi kanshi fushin da takeyi da shi ya dame shi duk ya rasa Jin dadin gidan,Wajen Bash yaje yace yanzu ya zanyi da ita? Bash yace kaje Kawai ku shirya ka fahimtar da ita nufinka ba Wai fada da Fushi ba,kasan Mata fa in taga dama zata ma Yi a boye baka sani ba sai dai kaga Taki samun wani cikin,Ahmad yace wlh da Kuwa ta Gane kurenta Aamna ta fiye rigima da taurin kai amma ba komai kyaleta,Bash yace masalaha itace kasan ta Sha wahala ita tasan me ta ji.

Yau da dare Ahmad dakinta ya shiga ya Iske tayi kwanciyarta ita da Fu'ad dama tunda suka fara fadan wurin 4days kenan ta daina zuwa bedroom dinsa.

Tunda ya shugo tana kallonsa tayi kamar bacci takeyi amma Kuma zuciyarta tayi fari kwal da shigowarsa sabo da ta Gama gajiya da fadan Nan nasu ta hakura ma zata Haihu hakan tunda Yana so.

Jaririn ya dauka tare da maida shi bed dinsa da ke jikin nasu,Addua ya Masa tare da kashe light ya koma Bayanta ya kwanta Yana me Zura hannayensa ta kasan Hannayenta ya rungumota jikinsa.

Masu Sharhi Ina godiya wlh Kuna birgeni.

AsmaBaffa
10/29/21, 7:46 PM - Buhainat: 🌵🌵 DUNIYA TA AAMNA🌵🌵

KARSHE

NA KUDI NE

DUNIYA TA AAMNA IS DEDICATED TO GARBA BUTALAWA FAMILY.

141-150

Official

By
AsmaBaffa

Page naki

Ummi Deejat

Aamna an samu dama harda yanga,nasan ba bacci kike Yi ba kina ji na,duk akan Haihuwa ne kike ta wannan fushin? Aamna a hankali tace ai Ni ba Fushi nakeyi ba,tunda kana so ai shike Nan ko mutuwa zanyi na hakura ai Sanda kake so sai ayi planning din tunda dama mu Mata Bamu da yanci,Dariya yayi kadan yace za muyi Mana Amma ki daure ki Karo min biyu Kinga Uku kenan sai muyi Kinga bamuyi aure da wuri ba ya kamata ace tun tuni Ina da Yara sun Kai hudu ko ma biyar,Aamna Tace ba matsala Allah ya bamu na gari,Ameen ya furta sannan ya fara rabata da kayan jikinta,Aamna ta Sha gyara itama a matse take sabo da haka Suka fara kashe juna da kauna,an Dade ba a hadu ba ai Kamar zakuna Haka suka koma yau.

Sai gaf da Su Humaira zasu Haihu Yar China da Siyama suka samu ciki,Yar China harda rawa,wannan lokaci lallabawa takeyi bata Wasa sabo da kar cikin ya sake zubewa,sai da ta sa Tawaga ya kawo Mata Yar aiki duk sabo da kar ciki ya zube,komai a hankali take lallabawa har Humaira ta Haifi Yarta mace santaleliya,taci Suna Farhat an Sha shagali,bayan tayi kwana talatin Hafsat ta haihu itama mace,ranar suna taci Amrah,Sati biyu tsakani Nafeesat ta Haihu itama ta Haifo Namiji Kato Mashkoor ya maida sunan King Ahmad,Sai da Nafeesat tayi Arba'in sannan Sameera ta Haifi mace itama taci sunan Ummatinsa data rasu Safiyya suna Kiranta da Little Aamna.

Abubuwa suna tafiya normal sai sake bunkasa sukeyi arziki Yana yalwata yanzu ma Basu fiye Zama a kasar ba sai tafiye tafiye suke Yi zuwa kasashe Daddy ya sakar musu komai,Siyama tuni mijinta Hashim ya Siya musu katon Gita me gate ga motar Hawa lafiyayya sai abinda tace.

Su Ahmad duk inda zasu da matansu suke Tafiya Matukar zasu Yi Kamar sati Daya basa tafiya mutum Daya,Baba tuni Ahmad ya Siya Masa mota sannan Suka je aikin hajji shi da Mama,Haka su Tawaga ma Iyayensu duk sunje da Wanda ya kamata duk Ana ta biya musu.

Aamna sai da suka shirya tare da Ahmad,Mummy,Daddy,Humaira, Sadeeq da Mufeeda tare da yaransu Suka je can kasar su Daddy taga Dangin mahaifiyarta da kowa satinsu biyu suka dawo,Gaba Daya su Aamna sun sake gogewa da wayewa,sun Zama matan manya kana kallonsu kasan suna hutawa,yaransu bulbul kyawawa gwanin sha'awa.

Siyama ce ta Haifi Yarta itama kyakyawa taci suna Fadeela,Bata Dade ba Yar China yau Sunday da Asuba ta fara nakuda,Bata wani daure ba tana Jin ehem ta saki kuka,Weekend ne Tawaga ya koma baccin hutunsa yaji Yar China tana kwada Masa Kira da karaji tunda yaji yau

ko Dan My Man din Bata ce yasan ba lafiya yanda yaji tana Tawagaaaaaa...kazo kafata ta rike....Yana Fitowa room dinta ya ganta ta fito daure da towel da Alama wanka tayi,tace wani ruwa ne yake zubo min da yawa kafata ta rike,wayyoo....mutuwa zanyi.....ruwan jikina zai kare,Tawaga ya rude tare da zura jallabiyya ya sa Mata kaya,itama ta hada kayan haihuwarta tsaf a jaka yanda sauran sukayi ai kinkimarta yayi,Yana Fitowa da ita Nafeesat ta fito zata tafi wajen Aiki ai sai ta fasa Driving motarta Suka tafi tare da Yar China,Humaira ma ta bisu a tata motar dake Dukkansu suna da mota ta kansu mazan sun siya musu,Aamna motocinta har biyu masu tsadar gaske ko tayi Driving ko driver ya tukata,Yar China ce Kawai Tawaga yace sai tayi hankali Bata Jin magana.

Yar China duk ta cikawa mutane kunne da kuka duk ta tashi hankalin Tawaga ya rasa yanda zaiyi,Iyalle tuni tazo Asibitin ita da matar kaninta,Yar China tana Iyalleta rike ni Iyalle mutuwa zanyi wayyo marata Iyalleta....ai Sanda Kan jaririn ya fara Fitowa Yar China Tace gashi Nan Iyalle.....gashiiiii.....wani nishin tayi gumi Yana keto Mata ta ko Ina ta wani shide gaba Daya sannan da taimakon likitoci Yar China ta Haifi katon danta Namiji, tunda ta Haihu akaji Shuru Yar China wahala ta kare,komai da ya kamata anyi sai Yamma aka sallame su,Wannan lokacin Iyalle gidan Yar china ta koma gaba Daya da Zama sai Yar China tayi Arba'in zata tafi.

Yar China Kamar zata cinye danta,ranar suna ba ayi wani biki ba kasancewar Yar China jininta ya Dan hau dalilin Haihuwa sai akace Kar ayi suna sabo da Hayaniya,ranar suna yaro yaci sunan Baban Tawaga da ya rasu Wato Abdallah Yar China tace wow suna me Dadi badan suruki bane Bai kamata a boye sunan ba Amma Dole nayiwa Tawagana kara,Su Aamna suna ta shawara wanne sunan za ana kiransa da shi,Aamna tana sani Tace a sa masa sunan Babana Raheel,Yar China tace wlh Sam Haka Kawai ai Baba za muna tunawa yanda yake ce Masa Rahilu hhhh Suka dinga dariya,kowa ya fara kawo suna a junansu matan,Sameera tace ga Aalim ga Affan,Humaira Tace Farhan,Siyama tana gidan itama Tace ga Faisal,Yar China ta doki Siyama a cinya tana Allah ya kiyaye Ubangiji ya yaye min ai akan na sa Faisal gwara Zubairu Kawai,Suna Dariya Yar China Tace na Dauki Aalim din kawai,Allah yasa Aamna ta Haifo mace next Aalim Dina ya samu budurwa nasan zata Yi kyau tun tana Budurwa Kinga idan ta yoki zata Yi katon Nonuwa ko ba komai Dan Aalim Dina ya samu na tabawa,Suka kece da dariya,Humaira tace wallahi Allah ya shiryeki,Yar China tana Dariya tace Ni dai kuyi sauri ku haifo wasu matan sabo da Aalim Dina ya zaba ya darje ciki,ko wasan bayan murfin kofa sukeyi ai kunga ya dinga rage zafi,Suna ta dariya Yar China tace Aamna sai ki dinga yiwa Yar budurwar Taki fada idan kin haifowa Aalim Dina da Allah idan shine a dinga San Masa Yana dumbula,Suna ta dariya Aamna tace Allah ya shiryeki bazan yarda da Kwarton danki ba,Nafeesat tace Ni dai ga Nawa shima Yana jira,Sameera me mace tace tace ku karata tawa ta samo bare,Hafsat ma tace wlh bare Aamna kije da yaranki,Humaira tace Ni dai bance komai ba,Yar China tace dan Allah Humaira ko ke ko Aamna Ina yiwa Aalim riko sabo da jinin larabawa zai dace da fara shima kunga gashi fari ko Yaya? Aamna tace ke da Zaki koya Masa kwartanci uban wa zai Baki yarsa,Yar China ta gyara rigarta zata bashi nono tace yaro fara Dana Mamanka Ana maka gorin Nono,Yar China harda Dora Hannun Dan Jariri a dayan Nonon Dayan Kuma Yana Sha tace ja Kaya kafin Ubanka yazo shima duk zanji daku,Su Aamna suna ta uban dariya,Humaira tace Yau fa akayi suna Yar China Amma kike Neman Miji? Yar China

harda turo Dan karamin bakinta tace to Mene Ni ba kazama ba wallahi Indai da sama sama ne yazo,karku ce wani waye wannan madarar jaririn akwai ta ubansa a ciki Yara ku zauna can,ai mu ba a barin mu a baya,tsafta iya tsafta yarinya Bai San Sanda zai Sha ba ma ta furta tana dukan Cinyar Aamna,gaba Daya Yar China ta Raina su babu wani Babba a ciki.

Sai da ya Gama Sha ta mikawa Siyama Dan Tace rike shi na dawo Anya Yaron Nan ba idona kanana ya gado ba kuwa? Aamna tace a'a wallahi idon Tawaga ne haskenki yayi Kawai duk shima Tawaga ba Baki bane Amma kinfi shi haske kalleki Kal fa Yar China Nima kin fini haske sosai sai dai kiyi haske Daya da Ahmad dina,Yar China taji Dadi an yabeta tace to Idonsa ne yaki budewa sosai har yanzu sai dai ya kyallo shi ya rufe haba yaro Kamar munafuki,Humaira harda rike ciki sabo da dariya,Yar China tayi kitchen Ana wani rausaya harda Murguda Kunkumi ita ta ciko tayi dam,Aamna Tace Tawaga Yana hutawa mutuniyata,Yar China Tace wlh sai a aza room( Other Room) ma inji Shugaban kasa,Hafsat Tace ai yayi gaskiya Women belong to the kitchen and ze Aza (other room).

Sai dare su Aamna Suka kyale Yar China da Iyalle,Iyalle ta tasa Yar China gaba tana Mata fada Kar ta sake ko ta daina jini ta Bawa Tawaga kanta zai Mata wani cikin da wuri,Yar China tana shirya Aalim dinta tace to Iyalle bazan yarda ba,karki damu shi bashi da wannan zalamar ma,Iyalle ta harari Yar China Tace makaryaciyar banza Naga kwananki biyu da Haihuwa da idona na ganku a kitchen Kuna wannan jarabar tsotsar bakin naku Dan Ubanki Wai Uwar me kuke ji ne wannan wacce masifa ce  bakin ma baza a barshi ba,Ni na taba ganin wannan jaraba Yar China ki raba kanki da wannan halin maitar,Yar China tace to Wai ke Iyalle Ina ruwanki? Ai sa Ido ne ya kaiki kallar mu a kitchen,aikin Reno fa da kula Dani kika Zo Taya Zaki hanani kula da Mijina,Ni wallahi baza ki Rabani da Mijina ba Yar China ta fashe da kuka,Iyalle ta saki Baki tana kallon ikon Allah,Yar China tace ai dama tunda akazo bikina Naga kinki Yi min Nasiha nasan da wata a kasa a ranki,gashi Nan Zaki ce Kar na kulashi,mu ai ba tsofaffi bane irinku yanzu Kai ya waye,da Ilimi ake Aiki,bazai samu abinda yake so ba Ina jinin biki shine Zaki ce Dan kiss dinma na Hana bawan Allah, bariki kike so yaje ya dinga cakumar Yaran mutane ya dakko min cuta Ina zaune gandandan akan na Haihu Allah bazai yuwu ba.

Iyalle ce ta dauki Robar ruwa tare da bin Yar China da gudu zata kwada mata tana Dan Ubanki daga Miki fada Zaki ce Zan rabaki da mijinki ki bashi abinda yafi jikinki ma Dan Ubanki ki bashi har duwawunki ma,bayan gaba ki bashi har baya ma Dan ubanki,marar kunya fitsararriya,Yar China tana Dariya tace Iyalleta Sorry Kinga dai jego nakeyi karki jawo wajen da aka min Dinki ya sake kecewa Mana Haba,Iyalle jaririn ta dauka ta karasa shirya shi tana cewa Zaki ci Ubanki da son Miji wallahi idan kika Yi wani cikin kafin Arba'in kiyi kuka da kanki,Yar China ta dafa kafadun Iyalle tana Dariya tace Iyalleta Tawaga hankali ne da shi fa,Wani Namiji ne yake da hankali akan wannan abin? Ina yaga hankali Zaki ga hankali marar kunya Jeki,Allah yaji Kan mahaifinki ai laifinsa ne tunda aka haife ki nace a samu wanzami ya cire Miki Beli Amma yace Sam yanzu an daina Yayin hakan cutarwa ne ai gashi Nan Baki da kunya kin koma Harija.

Yar China ta dinga dariya,Iyalle Tace ai Dole kiyi Dariya tunda kika Haihu kika sake sabon

salon daukan wanka na Jan Hankalin me gida,kullum ki dinga Shiga ta rashin mutunci kina kwarkwasa da karairaya a gabansa Ina kallon abinda kike Masa,kici kwalliya ki Sha turare wallahi Zaki Yi Dana sani,Dan masifa kina jegon ma baza ki huta ba,kin makalewa Miji Haka kika ga anayi,Idan ya shigo kika bishi sama sai ki shafe kusan awa biyar Baki sakko ba uban me kukeyi a saman da jego? Yaron Nan kullum Ina jiyo kukansa idan kika tafi dashi tsakar dare zai ta kuka ba'a lallashinsa,Yar China tace to mutum bazaiyi bacci ba sai mu zauna lallashinsa idan ya gaji ya daina Ni bazan dauki wannan iskancin na jariri ba ace sai dare zai tsiri kuka uban me aka Masa ai wlh sai dai in ki dinga kwana da shi amma mu dai cikin dare Indai na bashi nono baiyi Shuru ba baccinmu zamuyi.

Iyalle ta saki Baki tare da furta Haka kika ga anayi Dan Ubanki? Ke Haka aka Miki? Baki da Hankali Sadiya amma a Haka kike cewa kina son danki Wai?Yar China dai shuru tayi ta shiga kitchen ta hadowa Tawaga Abincinsa ta haura sama ta Ajiye sannan ta koma bedroom dinta ta gasa jikinta sosai yanda Iyalle ta koya Mata sannan tayi wanka da Sabulun me kamshi ta fito ta ci gayu cikin wata sabuwar atamfa super wacce Tawaga ya dinka Mata cikin kayan suna Blue and White,sun Mata mugun kyau Riga da skert,gashi ta Sha uban lalle me kyau,gashin Nan yaji Gyara a dakin Iyalle ta sameta tana shafa turaruka Baki Iyalle ta tabe tana cewa aikin banza Yaran zamani Baku San ciwon kanku ba ga danki Nan yayi bacci, Karbar Yaron Yar China tayi yasha kayan baccinsa masi kyau farare dama wanka aka Masa Yana ta zuba kamshi,Iyalle Tace sai da safe,Yar China Tace Allah tashe mu lafiya Naman suna fa da aka fara soyawa Yana kitchen idan Zaki ci,Iyalle tace na eba ma a plate kizo ki hada min shayi me kauri da breadi na naci na koshi,Yar China tasan Iyalle da son shayi, Yaron ta Saba a kafada ba tare data wani tallafe shi ba Jin ya zauna daram a Haka ta bi steps sai ga Tawaga ya dawo suna magana da Iyalle tana tsokanarsa dake itama ta Zama kakarsa.

Da sauri ya karasa ya cafke jaririnsa Yana cewa Baby Ganganci ne fa wannan Yana binta da mayen Kallonsa yace kinyi kyau Yar China ta Mika Masa Hannu Suka rike Hannun juna tace gani Nan zuwa yanzu Bari na sallami Iyalle,okay ya furta ya haura sama da jaririn nasu,Sai da Yar China ta Gama sallamar Iyalle sannan ta kashe kayan wuta tare da haurawa sama,tana shiga lokacin ya fito a wanka Yana goge jikinsa da towel,Yar China ta karba tare da karasa goge Masa jikin,Lotion ta shafa Masa sama sama sannan Tace kayi Sallar Isha ai? Yace ae da su Ahmad Mukayi ma,Yanzu sai abinci? Yana murmushi yace kadan Zan iya ci Aamna ta Riga da ta shirya Mana abinci,Yar China hade Rai tayi tace Amma ai sai ka fada min tun wuri Kar na sa Hafsat tayi girki,itafa tayi ta kawo sabo da Kai,to tunda Hafsat ce ta Yi ai ba laifi idan banci ba,Amma idan naki ne  kin San ban Isa naki ci ba,Murmushi tayi Tace kazo da magana,yanzu kayi magana ta kirki My Man Bari na kaiwa masu Aiki yanzu zasu cinye,Abincin ta sauka da shi ta Basu tana dawowa ya jawota jikinsa Yana sinsinar Kamshinta yace Anya Zan iya Kiran Arba'in Kuwa? Yau sati Daya banyi komai ba gaskiya Ina Shan wahala,Amma ai Ina gamsar da Kai ko ba ta wannan hanyar ba,Yeah ya furta Yana zuge Mata zip din riga.

Jibson Kuwa Sameera tana bawa Jaririya Nono kasa hakura yayi jaririya tayi wayo sosai tana Shan Daya ta rike Daya Jibson ya cire Hannun jaririyar ya sa nasa a Kai Yana cewa duk ke kadai sabo da sangarta da Rashin tausayin Mahaifi kina Sha ma baza ki hakura da Daya ba

sabo da son kai Anya wannan ba hadamar Baban Brown ta kwaso ba kuwa,Dariya Suka dinga Yi har Sameera tace Dan anace kenan,Yarinyar ya kwace yace Kar cikinta yayi Kato ya isheta haka,da Kansa ya shiryata sabo da an Mata wanka,har Pampers shi ya sa Mata tare da kwantar da ita a bed dinta sannan Sameera tayi Shirin bacci itama Suka kwanta,Jibson Yana Wasa da gashinta yace Ina tausayawa Tawaga kafin matarsa tayi Arba'in ba karamin wuya ake Sha ba,Sameera Tace to Kai ai baka jira Arba'in ba 2weeks fa Kawai ka dawo Aiki,To ai 2weeks a wajena yafi shekara ma,rashinki ai masifa ne a gareni cewar Jibson Yana lalubeta.

Bash da Hafsat dinsa Kuwa kallon wani film sukeyi a Palo daga Nan suka fada lobayya,a Nan palon Suka rakashe abinsu,yayinda Mashkoor me kwasar bacci a jikin Nafeesat dinsa yau wacce Rana Ana bacci da wuri sai Asuba zai gwangwaje,Brown Kuwa yau fada sukayi da gimbiyar tasa shi yasa Suka kwanta kwanciyar Kai da kafa,shi ya juya Kansa can ita ta sa kanta saitin kafarsa ba mutunci,Cikin dare Bai ma San sun koma sun manne da juna ba,Yana farkawa Yaja Tsaki tare gyara kwanciyarta ya koma yanda suke a farko Kai da kafa,Itama Humaira Haka ta sake Matsawa can gefe Amma kafin Asuba sun dawo sun makale juna,Brown Yana farkawa Karo na biyu yace mayya kin dawo kin manne min ai shike Nan sai kiyi ta kwanciya,Humaira tace gaka Nan bakin Maye Ni da Kai waye yazo wajen wani kowa ya matsa Wajensa mana,to daga min kirji na tashi,sai lokacin taga Ashe ma a saman kirjinsa ta kwanta,da sauri ta matsa ya tashi ya wuce Toilet da Niyyar Alwala ya wuce masallaci.

Oga kwata kwata King ba Bata lokacin yau da wuri aka Yi harkar sun  gwangwaje abinsu,sai Asuba Suka Yi wanka sosai tare da Sallah,Fu'ad Yana ta baccinsa Aamna ta haura saman bed ta kwanta a jikin mijinta tana shafa Sajensa da gemunsa tana son yin bacci tace yaushe zamu tafi Lagos din ne kaga fa Mufeeda ta Haihu jibi suna ya kamata mu je,Ahmad yace hmm ni wanne suna Kuma? Ki Bari zamuje wani meeting sai na tafi dake,Ni da Tawaga zamuje sai mu tafi daku ku biyu ma Amma sai Nan da 2weeks,Aamna zata Yi magana yace bana son jayayya fa,ai Allah ya kaimu zance Kawai, Alright ya furta Yana shafa gadon Bayanta suka koma baccinsu.

Bayan Yar China tayi wata biyu da Haihuwa Tawaga ya sama musu Admission shi da ita Amma shi dama NCE ne da shi Degree ya tafi Yi,ita Kuwa Yar China fresh level one ta samu Health education, Part-time sukeyi a private University,Shima Jibson da Bash sun koma schl,sai Hafsat da Humaira,Nafeesat,Aamna,da Sameera duk suna da Degree Basu da matsala Kuma ba Aiki zasu Yi ba,Yar China Suna karatunsu sosai ba ruwanta.
Aamna Bata samu ciki ba sai da ta yaye danta da watanni sannan ta samu wani,Ahmad sai murna yake yi,Sai da cikinta ya tsufa sannan sauran ma Suka samu ciki Banda Yar China again,Wannan lokacin Aamna mace ta Haifo zukekiya,Yar China Tace Alhmdllh Aalim Dina ya samu tasa, Siyama Kuwa kafin ma ta yaye ta samu ciki sai gashi ta Haifi Namiji itama,Sai daga baya duk tazarar ba Nisa su Nafeesat Suka Haihu suma,Sameera Namiji itama,Humaira ma Haka,Nafeesat mace ce tayiwa Danta kanwa,Hafsat Mace itama ta sake Haifa.

Sai bayan ma yaransu sun shekara sannan Yar China ta samu ciki ita Sai da Danta yayi Shekara Uku sannan ta samu wani cikin sabo da Allura tayi ta planning,Suma sauran matan

wannan karon duk family planning sukayi,Ahmad da kyar ya Amince sai da Aamna ta dinga kuka kullum sannan ya hakura.
Gaf da zasu Gama school Yar China ta sake Haifo Namiji kyakyawa,Wannan lokacin Yar China an sake Zama Babba an Kara nutsuwa sai dai surutu da abin Dariya sai Wanda ya karu ma,ga shegen Iyayi da wani tashe da take ji,Sunan Yar Aamna Suhailat sai Yar China ta sawa nata Suhail Wai ko za a samu akasi Suhailat taki son Aalim sai ta so Suhail shi ya kwashi dadin cewar Yar China,Ahmad da Aamna ta bashi labarin target din Yar China ya dinga dariya yace wlh bashi Kuwa zanyi Ina bayan Yar China nima.

Sai da Yar China tayi Arba'in sannan Tawaga ya Mata kyautar motarta sabuwa kantamemiya kasancewar karambanin Yar China yasa ta koyi mota wajen su Aamna,Sai Bayan sun nutsu suka sauke farali daga Nan Kuma sai yawan zuwa Umrah,suna zamansu lafiya da yaransu abin sai Wanda ya gani,Iyalle ma an kaita Aikin hajji da kaninta,Yayin da Aamna take waya da Yan uwanta na wajen Uwa da uba sannan sukan ziyarci juna jefi jefi,Abin gwanin birgewa sai Wanda ya gani,Daddy sai Hutu Kawai yakeyi bashi da matsala,Mummy ma haka.

Yau Ranar auren Aamna da Ahmad ne ya sake zagayowa,Kamar yanda suka Saba shirya Dan kwarya kwaryan party a hadadden gidansu Wanda gidan duk kusan shekara sai an canja Masa fasali da furniture.
Iya su ya su ba Wanda aka gayyata daga mazan sai matansu da Yan Yara su dagwai dagwai Yara Yan gayu da su,Dukkansu kowa ka gani ya dauki uban wanka na kece raini,shigar Ahmad da Aamna ta musamman ce wata maroon and white suit ya Sha gwanin sha'awa,Aamna ma kayanta wata gown white an nada Mata gogoro da maroon takalmi da pose dinta maroon gaba Daya,Tasha makeup ta kece raini,Ka rantse yau aka Daura Auren,anyi wani decoration a garden kusa da pool dinsu,gwanin birgewa,Ga kida Yana tashi sosai,Su cake dankareren gaske,Su Tawaga da matayensu an kashe wanka cikin shaddoji na kece raini,matan wasu da lace wasu da material,Siyama da mijinta itama sun zo,Yar China tana ta pics Haka ga me daukan pics daban na musamman,girki ba irin Wanda ba a shirya ba,kowa ka gani cikin nishadi yake.

Bash ne ya fara magana tare da Bude taro da Addua,Ahmad King ya karba speaker din ya fara magana kamar Haka
Yau ce ranar data fi kowacce Rana muhimmanci a wajena,ranar da Mummy ta gano min matar aurena,ranar da aka min auren dole,lokacin da muke tsaka da cin duniya,Muna tunanin cutata akayi wanda Ashe gata aka min ban sani ba,Munyi fada,munyi dambe da matata Ina ganin tana takura min,har ta gaji ta sare ta bar min gidana,Ina murna ta tafi amma Kuma na sake haduwa da ita a hanya naji Ina sonta duk zaman da mukayi ban so ta ba sai Dana ganta a kwararo Allah me iko Kuma lokacin na fada kogin sonta,Ina tsoronta ga sonta zai kashe Ni,Lokacin Ina King Dina,Sabo da ita na canja shiga,na koma shiga ta Kamala,na haura katanga sabo da ita,na siyar da citta sabo da ita,nayi wanki sabo da ita,Ni king nayi kuka dalilinta sannan Kuma karshe ta Zama silar shiryuwata na koma mutumin kwarai Wanda sanadin hakan ya jawo duk abokaina Suma Allah yasa Suka shiryu duk da cewa Su Hatsari silarsa tafi karfi,Dariya sukayi gaba daya.

Yace Yan Uwana, abokaina, abokai na Amana,Ina ji da ku Ina kaunarku, sannan Ina addua Allah ya sake hada kanmu ya Bamu lafiya da tsawon rai,Ina tabbatarwa wata abotar tafi Yan uwantaka,Suna tafi Suka ce Ana tare Our King,Aamna ta kwace speaker Tace My King dai,Suka ce no our king Aamna ta dage ita Tace My King dai,Nan Suka zauna aka dinga ciye ciye da shaye shayen lemuka Wanda suna ta tuna rayuwarsu ta baya suna labarin wani ayi Dariya wani a tausaya,sosai abin nasu ya kayatar,su Mummy ma ta waya Suka musu murna.
Lemo Suka tsiyaya a glass cup kowa ya daga tare da furta cheers.

ALHMDLLH

NAN NA KAWO KARSHEN DUNIYATA AAMNA.

INA MATUKAR GODIYA GAREKU FANS MUSAMMAN MASU SHARHI BASA GAJIYA MUSAMMAN
UMMI DEEJAT

NA GODE DA ADDUARKU FANS ALLAH YA BAR ZUMUNCI .

Saura idan Allah ya kaimu Kuma novel kyauta Next.

AsmaBaffa